06/05/2022 à 15:31 - Les messages et les appels sont chiffrés de bout en bout. Aucun tiers, pas même WhatsApp, ne peut les lire ou les écouter. Appuyez pour en savoir plus.
06/05/2022 à 15:23 - Sœur Amih: <Médias omis>
06/05/2022 à 15:33 - Mom Lateef: <Médias omis>
06/05/2022 à 15:36 - Sœur Amih: <Médias omis>
06/05/2022 à 15:39 - Mom Lateef: <Médias omis>
06/05/2022 à 15:52 - Sœur Amih: <Médias omis>
06/05/2022 à 21:22 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_1_

Cike da murna ya shiga ba wa yaran hannu suna tafawa yana fad'in "Yaran kirki kenan, amma

fa kunyi k'ok'ari."

Cike da zumud'i *Hameeda* da ba za ta wuce shekara bakwai ba tace "Abba, to za ka siya mana kyautar da ka yi alk'awarin siya mana idan mu ka yi k'ok'ari?"

Da fara'a a fuska dattijon yace "Dole na ma, ai ina fita daga nan zan kawo muku kyautarku."

*Hadeeya* dake zaune kusa da shi ne tace "Amma dai Abba ai na fi su k'ok'ari ko? Dan haka kyautata za ta fi ta su kyau."

Hararanta Hameeda tayi tace "Ka ji yarinya, ke da ma ko jarabawar ba'a muku ba, ku fa yara ne."

Kyakyawar matashiyar matar dake zaune gefe da su tana kallonsu da murmushi a fuskarta ce ta bud'a baki cike da gayu a harshen faransanci tace "Calmez-vous les enfants, votre Papa offrira a chacun le bon cadeau (ku kwantar da hankalinku yara, Mahaifinku zai ba ko wa kyautar da ta dace)."

Wani kallo ya jefa mata cike da so da k'auna yace "E toi, me za ki basu?"

Wani mahaukacin fari ta masa da ido kafin tace "Ce une secret entre eux et moi (sirri ne tsakanina da su)."

'Yar k'aramar cikinsu wato *Hamdeeya* ce ta k'arasa kusa da mahaifiyarta cike da shagwab'a da kuma yarinta tace "Momma, ni ma za ki siya min kyauta?"

D'agata tayi ta d'ora a cinyarta tace "Sosai ma yariyata, ai ke ce ma gaba kafin kowa."

Duk farin ciki da murnar nan da ake *Haleematu* na tsaye gefe tana kallo, ganin dai ita ba'a ambaceta ba yasa ta matsowa kad'an kusan mahaifin tace "Abba nima za ka siya min?"

Wani mugun kallo ya watso mata daga sama zuwa k'asa kafin ya d'auke kai yace "Da wannan sakaran sakamakon da kika kawo ne zan kashe miki kud'ina?"

Sunkuyar da kai tayi a marairaice tace "Dan Allah Abba, ko k'arami ne ka siya min."

A tsawace ya kalleta yace "Matsa ki bani wuri, ba zan siya d'in ba *Saleema*."

Dake sunan mahaifiyarshi gareta sai suke kiranta da sunan Saleema, d'ago kanta tayi ta zuba masa idonta da suka cika taf da hawaye tace "Abba, to idan na yi k'ok'ari a zango na k'arshe za ka siya min?"

Saida ya sake hararanta sannan ya yatsina baki yace "Watak'ila."

Murmusawa tayi tace "Tozan yi Abba."

A sukwane ta nufi inda mahaifiyarta ke zaune wacce ka rantse bata falon, sai dai tana zaune tana kallon komai dake faruwa, duk da ranta na suya amma ba ta da yanda za ta yi da ya wuce hak'uri, Saleema na k'arasawa ta zauna kusan Mamanta tana mik'a mata takardar (bulletin) sakamakon, karb'a tayi a raunane tana duba sakamakon, nauyayyar ajiyar zuciya ta sauke ganin sam ba wani k'ok'ari da Saleema ta yi, dan ko a yawan yan ajinsu mutum uku kad'ai ta bari a bayanta.

Uwarsu Hadeeya kam dake cike take da farin cikin dake d'awainiya da ita mik'ewa tayi ta nufo inda *Alhaji Yusuf Jiji* ke zaune, *Safeeya* na ganin haka ta yi saurin d'auke kanta dan ta san me amaryar za ta yi. Ai kam *Ardayi* na zuwa d'an rank'wafawa tayi ta d'ora hannunta a kafad'arshi sannan ta sumbaci labb'ansa, daga ita har shi ba wanda ya ji kunyar yaran, dan hakan ba sabon abu bane a wajensu.

Saida suka aikawa junansu wani kallo da su kad'ai suka san ma'anarshi kafin ta tattara hannayen yaran ta rik'e a hannunta, d'an juyawa tayi ta harari inda Safeeya da 'yarta suke tare da fad'in "Alajina zan shiga ciki, kasan yau ina cikin farin ciki saboda nasarar da yarana suka samu, ka san fa abun da ka jini ne, gado sukayi."

Da wani murmushi a fuskarshi ya bi bayanta da kallo cike da so da k'aunarta, kamar yanda soyayya ta sa ya aureta haka yake da matuk'ar son farar mace, dalilin da ya sa ma kenan ya kutsa ya shiga lungu da sak'o ya zab'o buzuwa da ta amsa sunanta, gashi kuma kwalliya ta biya kud'in sabulu tunda har ta zama fitilar gidansa mai haska masa duk wani duhu.

Saida suka ga shigewarta kafin ya d'an gyara zamanshi yana matse fuska ya d'an kalli inda Safeeya take ya ga ko tana kallonshi ne, idansu na had'uwa ya szke had'e fuska kamar zai fashe, shi a dole kar ta kawo masa wargi duk da kuwa ya fi kowa saninta akan hak'uri da kau da kai. Murmushi kawai tayi ta d'anyi gyaran murya tace "Abban Hajia, ina ganin me zai hana ka je makarantarsu yaran nan ka ji me ye matsalar Saleema, ta yiwu akwai wani abun da bata ganewa?"

Cike da basarwa ya d'an kawar da kai yace "A idonki dai ba k'ok'arin da bana yi akan karatunsu, har malami na musamman na d'aukar musu da ke zuwa gida yana sake musu bitar abinda aka koya musu, a k'alla kowane dare yana d'aukar awa biyu a gidan nan, to idan ba ta fahimta yanzu ba sai yaushe?"

Jinjina kai tayi alamar gamsuwa tare da sassauta muryarta sosai tace" A kawo maka abinci ne?"

" Sai na yi wanka." Ya fad'a ba yabo ba fallasa.

*Bayan wani lokaci*

Rashin damar zuwa da yau malamin na su bai samu ba yasa Alhaji Yusuf zaman dirshen yana koya musu karatun saboda jarabawar da zasu fara gobe ta zangon k'arshe, allon (ardoise) Saleema ya karb'a ya fara mata da lissafi, sosai ya rik'e allin kafin ya rubuta mata 4 a tara da 4 nawa zai bayar?

Cikin ikon Allah sai Saleema ta k'urawa rubutun ido tana kallo sam ta ji ta manta da komai ta yanda ta kasa fad'a da sauri, da yatsunta take ta k'idayawa yayin da yatsanta d'aya ke cikin bakinta tana ta motsa bakin. Kafin ta ankara Alhaji Yusuf ya d'auke fuskarta da wani mahaukacin mari yana fad'in "Dan ubanki wannan d'in ne ba zaki iya fad'a ba? Bari ki gani..."

Jawo k'afarta yayi bai kulada kukan data fashe da shi ba saboda girman da marin ya ma shekarunta guda goma ya matsata daf da shi, sake nuna mata rubutun yayi yace "Nawa ne nan dan uwarki?"

A kid'ime cike da son k'watar kanta tace "Biyar."

Wani marin ya gaura mata yace "Wannan d'in ne biyar? Ubanki ke da biyar d'in."

Kallon Hamdeeya yayi dake k'arama a cikinsu kuma yar shekara hud'u yace "Idan na tambayi Hamdeeya ta fad'a min wallahi ci miki uwa zan yi."

Nunawa Hamdeeya yayi yace "Autata nawa ne nan? 4+4?"

D'an jim tayi sai kuma ta furta "8."

Bai jira komai ba kam ya shiga jibgawa Saleema allonta tare da kikkifa mata mari yana fad'in "Me yake shiga kanki ne? Ke baki ji kunya ba yanzu? Wannan fa k'anwarki ce ta uku ma, ke ce babba a cikinsu amma ke ce dak'ik'iya mai k'walwar kifi."

Da sauri Safeeya ta fito daga d'akinta gabanta na fad'uwa, ganin yanda yake dukanta ta ji ba dad'i sosai, a sanyaye tace" Haba Alhaji, a haka ta ya za ta fahimci abinda ka ke koya mata? Dukan ya yi yaw..."

A tsawace ya nunota da yatsa yace" Ke rufe min bakinki, dama na jima da fahimta ke kike d'aure mata gindi kina sakata lalaci, duba fa ki gani abinda ta kasa fad'a sai k'aramar k'anwarta ce ta fad'a, wannan ba abun kunya ba ne ?"

Ardayi da fitowarta kenan daga d'akinta ita ma tana jinme ke faruwa ta fito tana fad'in" Ta fad'i

haka mana saboda bata so a koya mata ilimi, burinta 'yarta ta zama kamar ita, wannan ma ai abun kunya gareka a ce kana fama da iyalinka akan karatu."

Girgiza kai tayi cike da kissa tace" Karfa ka manta siyasa kake, ta ya za ka nuna iyalinka a haka bayan ba sa gane komai."

Ta k'arashe tana hararen Safeeya, kallonta Safeeya tayi tace" Saboda ba 'yarki ba ce ake duka ko? Ta hakane za' a koya mata ana mata dukan mutuwar? Ko kuma a ganin ta hakane za ta fahimta?"

A hassale Yusuf yace" Koma dai menene ai gaskiya ta fad'a, saboda hakane fa yasa ko nunaki bana so na yi a matsayin iyalina, ba yanda zanyi ne tunda iyayena ne suka had'ani da ke, amma 'yata dole na d'orata akan irin tsarina."

Tsamm! Safeeya tayi tana kallonshi da mamakin kalamanshi, bai tab' a kwatanta fad'a mata haka ba sai yau, me ya yi zafi daga magana har yake cizgata haka? Hawayen da suka malalo mata ne yasa ta saurin juyawa da sauri ta koma d'akinta, da harara ya bita tare da d'auke kanshi ya mayar kan Saleema wacce ke kuka kamar ranta zai fita, sake gyara zama ya yi alamar dai za sucigaba daga inda suka tsaya.

*Bayan sati d'aya*

A shirye dukansu suka fito cikin kyakyawar shiga, sai dai duka yaran na Ardayi riga da wndo ne na siket a jikinsu yayin da kawunansu ke bud'e sai dogon gashinsu da aka mishi fasalin kitso mai kyau. Daga cikin mota yake hangen yaran na tunkaroshi, tabbas ya fi son 'ya'yan Ardayi, sai dai bai san me yasa ya fi son su ba, saboda kyawonsu da farar fatarsu ne? Ko kuma dai saboda ilinmunsu ne? Maida kallonshi yayi kan Saleema dake bayansu cikin shigarta ta doguwar rigar shadda da kyakyawan hijab d'inta, ba za ka kirata bak'a ba saboda tana da d'an haske, sai dai idan ta jera da su Hadeeya bak'a take komawa saboda haskensu, kyawu kuma ba'a magana dan ba wani kyan fuska gareta ba, shi mamaki ma yake wasu lokutan yanda Saleema ta zama jininshi, duba da shi dai yayi tashen kyawu a zamanin k'uruciyarsa, kuma har yanzu da yake da shekara arba'in da yan kai, sannan mahaifiyarta ma kyakyawa ce dan ta wata fuskar ta fi Ardayi kyau, duhu ne kawai gareta na fata wanda kuma yake k'ara fito da kyawunta. Amma Saleema ba kyan fuska ba hasken na fata, wanda daga shi har uwarta da ta yo d'aya daga cikinsu to fa da ita ma kyakyawa ce, ga kuma wani munin na daban wato rashin ilimi.

Drebanshi ne ya bud'e musu inda mahaifin na su ke zaune duk suka shiga, da fara'a ya amsa musu da "Kun gama shiryawa?"

"E Abba." Suka fad'a kusan a tare, a hankali dreba ya fara jan motar suka fita a harabar gidan, cikin sanyayyar murya Saleema ta kalli mhaifin na ta tace "...

_Yan uwa barkanmu da sallah, da fatan Allah ya karb'i inadunmu yasa muna cikin 'yantattun bayi, Allah ya gafarta mana zunubanmu._

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_2_

Cikin sanyayyar murya Saleema ta kalli mahaifin na ta tace "Abba ka min alk'awarin siya min kyauta nima idan na yi k'ok'ari?"

Ba tare da sakin fuska ba yace "Idan kin yi k'ok'arin zan siya."

Washe baki tayi da farin ciki tace "Na yi ma Abba."

Wata harara Hadeeya ta jefa mata ta ja tsaki, a tausashe Saleema ta kalleta tayi k'asa da kanta, ba wanda ya sake magana a motar har suka isa makarantar, tsabar farin ciki da sakawa ransa 'ya'yansa za su ciri tuta ko tun yaran basu gama shagali ba ya dawo d'aukarsu, hakan yasa saida ya d'an jirasu na wasu mintoci.

Hadeeya da Hameeda na gaba sun taho da gudu da fara' a a fuskarsu, bud'e motar sukayi suka shiga suna rige-rigen mik'a mishi sakamakon kowace na fad'in "Abba ka ga ni nayi ta farko."

Karb'a yayi tare da kyautukan da aka basu a makarantar yana dubawa, yanda bakinshi ya kasa rufuwa tsabar farin ciki yasa shi kasa furta komai, sai da Hamdeeya ta shigo fuskarta da alamar damuwa, jawota yayi yace "Ya ne autata ?"

Dariya Hadeeya ta k'yalk'yale da ita tace "Abba wai dan ba'a bata kyauta ba ita ma, na fad'a mata ta yi hak'uri idan ta kai ajin CI (pramary 1) ita ma za'a bata."

K'ara jawota yayi jikinshi zai yi magana sai kuma ya tuna da babbar 'yarsa wacce ta fara kiransa da sunan Abba kafin duk wad'annan, da sauri ya d'aga Hamdeeya daga jikinshi ya kalli Hadeeya yace "Hadee, ina mai sunan Hajia?"

Saida ta yatsina fuska kamar ta ga abun k'yama kafin tace "A aji na barota ba'a kira sunanta ba."

Maida dubanshi yayi ga k'ofa yana fad'in "Me ya hana ku jir..."

Bai k'arasa fad'a ba suka hangi Saleema na tahowa ta rufe fuskarta da hijabi da alamar kuka take, wata mummunar fad'uwa gabanshi ya yi da tunanin ko lafiya? Abun da ya fara zuwa masa shine, kar dai sakarcin Saleema ya kai k'adamin da ta fara bayan gida a jikinta da har yaran nan ke biyarta suna mata ihu da tafi? D'an sauke madubin dake b'angaren shi yayi tare da bud'e motar da niyyar fita.

Sai dai wak'en da kunnuwansa suka tsinkayo ana ma babbar 'yarsa yasa shi dakatawa tare da rintse ido, a rayuwar duniya bai tab'a tsammanin haka za ta faru ga ahalinshi ba, a matsayinshi na wanda k' ok'arinshi ta sa gwamnati d'aukar nauyin karatunshi har ya keta hazo saboda

iliminshi, yake alfahari da kasancewarsa d'an Alhaji *Saddi Jiji* wanda har turawa suka shaida iliminsa ya kuma karb'i lambobin girma ta fannin ilimin kimiya, a matsayinsa na wanda ya tashi a ahalin da babu wanda gwamnati ba ta wa rana ba, hakan yasa ko a gari aka fad'i ahalin Jiji ake musu inkiya da ahalin *bariki* ba dan komai ba sai dan sanin mutane a kan su cewa su d'in mutane ne da suka san darajar boko kuma suke bata hakk'inta yanda ya dace, daga shekara ashirinda ta wuce zuwa yanzu da wuya ka samu wanda ba ya aikin gwamnati, ba wai dan sun dogara da ita ba, sai dai a ganinsu ta hanyarta ne kad'ai iliminsu da alfaharinsu zai bayyana jama'a su sani. Amma yau gashi kunnuwanshi na jiyo mishi ana ma babbar 'yarsa da saboda k'auna ya saka mata sunan mahaifiyarshi wacce ita kanta ta kasance likitar da a lokacin tana d'aya daga cikin mata biyu da suka fara tiyata a k'asar Niger, yau gashi ana ma takwararta d'an kira da wacce ta zo ta kusa da k'arshe a ajinsu.

Dakatawa ya yi daga shirin fitar ya d'aga madubin ya rik'e hab'a cike da jimami, dreban da ya ga yara na bin Saleema ne ya tsawatar musu ya bud'e mata gidan gaba ta shiga ta zauna tana ci gaba da shashek'ar kuka.

Suna isa gida a fusace ya fita a motar ya nufi d'akin Safiya ba tare da ya bi ta kan kowa ba, Saleema dake kuka da sauri ta zagaya bayan gidan ta lab'e kusa da tagar d'akin mahaifiyarta dan tunaninta dukanta zai yi, sai dai daga nan inda take ta juyo muryar mahaifin na ta sanda ya fad'a d'akin Safiya yana fad'in "Na sha fad'a miki ki dinga kula da karatun yarinyar nan amma ba kya ji, yanzu dubi abinda ta jawo mana, na je d'aukarsu amma yara na binta suna mata ihun jaka."

A razane Safiya ta mik'e tana kallonshi a mamakance tace "Jaka kuma?"

A hassale yace "Jaka mana, idan ba jakar ba mecece? Wacce ke zuwa k'arshe a komai, yarinya ban da majina ba komai a kan ta."

A raunane ta girgiza kanta ta sanyaya murya tace "To yanzu da kake fad'a min ya kake so na yi? Na bud'a k'wak'walwarta na tusa mata ilimi? Ko kuma na kasheta saboda bata ganewa?"

Dafe k'ugu yayi yace "Au ! Haka ma za ki ce?"

Jinjina kai yayi yace "Ya yi kyau."

Juyawa yayi ya fice a d'akin, wata nauyayyar ajiyar zuciya Safiya ta sauke ta koma ta zauna tana dafe k'irjinta dake doka mata da mugun k'arfi.

*Washe gari*

Da gudu yaran suka tarbeshi inda ya dinga rumgumesu a jikinshi yana sumbatarsu, cike da kissa da karairaya Ardayi a ta k'arasa gareshi, ba tare da jin nauyin komai ba suka rumgume junansu tare da sumbatar kumatunsu.

Safiya dake jera abinci akan tebur bata kallesu ba dan dama abinda ta san zai faru ne, inda Saleema dake zaune k'asan carpet ta bisu da kallo a ranta take ayyana "Ko me yasa Abba bai da kunya?"

Manyan ledojin hannunshi ya ciro kwalayan dake ciki na wasu mahaukatan dogayen riguna da k'ananan wayoyi masu kyau ya ba wa Hameeda da Haddeya, inda Hamdeeya ya bata riga da wani k'aton abun wasa da sunan kyautarsu, da sauri Saleema ta mik'e abun ka ga yaro jikinta har b'ari yake ta ajiye k'aramin almakashin hannunta ta tunkareshi tace "Abba ni ina nawa? Baka ban ba fa."

Wani kallon raini ya mata yace "Ni d'in zan kashe miki kud'i? Wace tsiyar kika tsinana? Wannan shirmen da kike?"

Ya fad'a yana nuna tsummokaran data tara gabanta kala kala na atamfa, leshi, shadda da saurensu ita a dole d'inki take, juyawa tayi ta kalli kayan sannan ta kalleshi tace "Abba d'inki ne fa nake yi."

Kallon Safiya yayi da ke ci gaba da aikinta duk da tana jin me ke faruwa amma ta dake kamar ba ta ji ba. Yace "Kina ganin irin shirmen da take tara min a gida ? Madadin wannan me zai hana ta d'auko littafinta tayi karatu?"

Shiru ta masa dan tun jiya yake nemanta da rigima ido bud'e, dan haka ba ta kulashi ba, Ardayi dake d'an gyara matsatsan rigarta mai k'ananan hannaye ce ta d'an tab'e baki tace" To ita kanta karatun ya sha mata kai ne bare kuma ta koya ma 'yarta?"

Sai lokacin kad'ai Safiya ta kalleta tace" Kinga, idan muna magana tsakaninmu ki daina saka min bakinki, bana so."

Kallonshi tayi fuskarta a d'aure tace" Me ya sa ka hanata kyautar ita ma?"

K' ank'ance ido yayi da mamakin tambayarta yana d'an gyara rigarshi ta shadda da aka ma k'aramin d'inki kasancewarshi d'an zamani bai cika son manyan kaya ba yace" Ban gane ba? Ke baki ji abinda na ce ba ce?"

D'auke kanta tayi daga gareshi sannan tace" Gaskiya ba ka adalci ko kad'an, ita ma fa haihuwarta kayi kamar sauran, me yasa za ka dinga fifitasu a kan ta?"

" Saboda sun fita. " Ya fad'a cikin d'aga murya, ido cikin ido ta kalleshi kafin ta kalli Saleema tace" Zo nan."

Da sauri Saleema ta k'arasa gareta tana matso k'walar da suka taru a idonta, kama hannunta tayi suka juya a wurin suka barsu nan, tab'e baki yayi irin ko a jikinshi kafin ya shiga wata sabgar.

*Kwana uku* kenan da faruwar wannan abu ya ga sauyi sosai daga Safiyar, dan ta daina walwala haka ma Saleema ba ya ganinta a falon tana wasarta, wanda dama ko can ita kad'ai takr wasar suma su Hadeeya suna ta su, k'arara duk mai ido ya ke gane da bambaci a tsakanin matan, wanda ba komai ya jawo haka ba sai fifikon da amarya ta samu fiye da uwar gida, ita ma kumata same shi ne dalilin dogon karatun da tayi wanda a yanzun take cin gajiyarshi ta hanyar aiki a banki.

Tsakanin mata da miji dama aka ce sai Allah, damuwa da hakanyasa shi dawowa gidan bayan ya tabbatar yaran na makaranta kuma Ardayi na wajen aikinta, a d'aki ya sameta kwance da alamar bata jin dad'in jikinta, k'arasawa yayi ya zauna kusa da ita yana kallon kyakyawar fuskarta wacce tana d'aya daga cikin abinda yasa har yau yake tare da ita da kyautatawa.

Hannu ya kai ya tab'a wuyanta yace "Me yake damunki ne?"

A hankali ta yunk'ura ta gyara zamanta kafin tace "Ba komai."

Da sauri ya fuskanceta sosai ya rik'o hannunta yace "Safiya hushi kike da ni akan abinda ya faru? Kiyi hak'uri kinji, b'acin rai ne ya sa da kula son da nake ma Saleema, ina so na ga ita ma ta zama kamar 'yan uwanta, shiyasa kika ga ina haka."

A tausashe ya d'an fara lumshe ido ya kwanto da ita jikinshi cikin muryar da ta fahimci kan zancen yace" Kiyi hak'uri kinji *Sofee*."

D'an murmushi tayi ta d'ago daga jikinshi za ta yi magana, sai kuma ta yi saurin rufe bakinta saboda aman da ya tuk'ota, da sauri ta sake toshe bakin tana had'eshi gudun kwafsawa, cike da kulawa ya kalleta yace" Oh! Baki da lafiya ne? Me yake damunki ne?"

Sunkuyar da kai tayi cike da kunya ta girgiza kai, d'an kawar da kai yayi a ranshi yana mamakin kunya irin ta Safiya, shekara goma sha d'aya da aure amma har yau kunyarshi take, shi ba zai iya tuna ranar da ta nuna mishi buk'atarta ba sai dai ya karanta a tsakiyar idonta ko daga jin sautin muryarta, hakan na birgeshi matuk'a a game da ita, sai dai kuma a matsayinsu na ma'aurata yana so ya ga tana komai b'aro b'aro, duk da dai hakan ba wata matsala ba ce dan kunyar tana taimakonshi sosai. Sake kallonta ya sake yi yace "Safiyyyyya."

Yanda ya ja sunan na ta ya sa ta d'agowa ta kalleshi, da murmushi a fuskarshi yace "Ko dai ciki gareki?"

Da sauri ta rufe fuskarta ta sake duk'ar da kanta tana ji kamar ta nutse k'asa, cike da farin ciki ya jawota jikinshi yana fad'in "Masha Allah Sofee na, dama kullum addu'ata Allah yasa ke ce za ki haifa min auta a gidan nan, kin san na fad'a muku yara shida na ke da buk'ata a rayuwata, idan ma zan samu k'ari to kar su wuce bakwai."

Ita dai rufe fuskarta tayi da da rigarshi tana mamakin tsari irin na shi, in banda abun shi ko wa ya fad'a masaana wa Ubangiji iyaka? Wato shi ne ma zai k'ayyade yaran da yake so ya haifa a duniya.

D'agota yayi yana lek'a fuskarta yace" Amma dai ki shirya mu je asibiti dan a duba lafiyarku, bana so na rasa wannan Safiya kamar yanda na rasa sauran."

Narai narai tayi da manyan idonta tace" Bana tunanin wannan ma zai tsaya, kamar sauran shima na san zai tafi ne."

Girgiza kai yayi yace" A'a ki daina fad'in haka, in sha Allah za ki haifeshi. "

Kamar za ta fashe da kuka ta kalleshi tace" Abban Hajia shida fa, shida na samu duka suna zubewa, har hutu aka bani ko hakan zai sa a dace amma har yanzu shiru."

Cike da jimami da tausaya mata ya k'ara rumgumeta a jikinshi yana rarrashinta, kasancewar d'akin a bud'e take yasa Saleema da ta taso daga islamiyya shigowa kan ta tsaye ba tare da tunanin za ta samu mahaifinta a d'akin ba duba da kwana uku kenan ma ko magana ba ta ga sunayi da mahaifin na ta ba, sai dai tana ganinshi ta zabura ta juya za ta koma waje, inda Safiya ma ta firgita da sauri ta mik'e daga jikinshi tana son matsawa nesa da shi, da mamaki ya kalli uwar ya kuma kalli 'yar, sai ya rasa duk me ye haka d'in? Kamar wani wanda aka kamada wata matar? Da fa Ardayi ce ba ruwanta, hasalima ita har kayan baccin take sakawa kuma a gaban yaran, idan ta kama ma har rumgumeshi za ta fara yi a hakan kuma a gabansu, a ganinsu dai ai iyalinsu ne ba komai.

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💏💏💏💏💏💏💏💏💏💏
*BAIWATA*
💏💏💏💏💏💏💏💏💏💏

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_3_

Cikin ladabi Safiya ta kalleshi tace "Abban Hajia."

"Na'am." Ya amsa yana kallonta, ci gaba ta yi da cewa "Dama Saleema ce take fad'a min wai tana son shiga koyon d'inki, ka san nan kusa da mu akwai wata dake koyawa mata d'inki."

Murmushi ta saki a fuskarta ta ci gaba da fad'in "Na fad'a mata ta yi yarinta dayawa, amma kuma na ga tana da k'ok'ari wajen yin d'inki, dan kullum da abubuwan take fama a gidan nan."

Aje cokalin da yake cin abinci ya yi ya kalleta sosai yace "Safiya, gaba d'aya alamu nuna min suke ke kike hana yarinyar nan maida hankali kan karatunta, 'yata ta cikina ta yi d'inki? D'inki fa ?"

Girgiza kai yayi dake nuna abun ya ma bashi dariya yace "A tarihin gidanmu ko mai siyar da sutura babu, ta ya zan bar yata ta fara koyon d'inki?"

Kallonta yayi da kyau yace "Kina ji na? Saleema idan har ba ta fito min a matsayin babbar likitar mata ba to ta zo min a matsayin wata engineer ko babbar 'yar jarida, idan fa hakan ya gagara ne zan so ta zama hazik'ar mace a cikin siyasa."

Kallon Hadeeya yayi dake cin abinci yace "Me kike so ki zama a rayuwa?"

Cike da iyayi ta waina idonta kafin tace "Abba, ni dai gaskiya irin aikin Momy nake so, irin yanda take shigarta idan za ta tafi, da jajircewarta a kan aiki yana birgeni sosai."

Jinjina kai yayi cike da gamsuwa ya kalli Hameeda yace "Ke kuma fa yar Abba?"

Cike da yarinta tace "Abba, ni dai so nake na yi dogon karatu akan harkar tattalin arziki."

Cike da jin dad'i ya jinjina kai har da murmusawa yace "Da kyau 'yata, wannan shi ne abinda ya kamata."

Hamdeeya ya kalla da fara' a yace "Autata dai na san bata da matsala ko?"

Cike da k'uruciya Hamdeeya tace "Abba ni dai malama zan zama."

Dariya yayi yace "Hakan ma burine mai kyau."

Kallon Ardayi yayi wacce duk abun nan da ake hankalinta na kan wayarta yace "Masoyiyata kin ji fa, dan haka sai ki k'ara zage damtse."

D'an murmushin yak'e tayi dan hankalinta ba nan yake ba tace "Dole mana, kar ka damu masoyi."

Sai lokacin ya sake kallon Safiya dake ta kallonshi da mamaki yace "Kin dai ji, dan haka ke ma idan za ki d'ora ta a turbar da ta dace ki fara tun yanzu, amma bana son maganar shirmen banza da wofi."

*Bayan kwana biyu*

Hannunta ya kamo suna shigowa d'akin ya kalli Safiya dake gyara gadonta yace "Yanzu wannan shirin da shi za mu tafi da ita? Baki ga yanda yan uwanta suka shirya ba?"

Juyowa tayi tana kallonshi sai kuma ta kalli shirin jikin Saleema, doguwar riga ce ta shadda jikinta mai kwalliya sai hijab da ya dace da kayan tare da takalminta masu kyau da tsada, sake kallonshi tayi tace" Me ye aibun shirinta?"

D'an gajeran tsaki yayi yace" Kin wani saka mata manyan kaya, baki ga na yan uwanta bane?"

D'an kawar da kai tayi tace" Ka yi hak'uri, amma gaskiya bana sha'awar koyawa yarinyata fitar

da tsiraici tun tana k'arama, gwara ta san hijab shine rufin sirrinta."

Cikin jin haushi yace" Ke da anyi magana sai ki nuna kin fi kowa tsoron Allah, to wannan 'yar abar wani ne zai yi sha'awarta ? Ina ma abun yake a nan?"

Wani tsaki ya sake yi yace" Kinga dan Allah d'auko min wasu kayan na canza mata idan ke ba zaki iya ba."

Jinjina kai tayi ba yanda za ta yi ta d'auko mishi riga ta kanti ta kawo, da kanshi ya fara k'ok'arin taimakawa Saleema, hakan yasa ta fara kakkare jikinta cike da kunya saboda rashin sabo, yana gama taimaka mata ta saka kayan ya kama hannunta za su fita, da sauri ta kalleshi tace "Abba hijabina?"

Harara ya wurga mata yace "Dallah muje malama."

Haka ya ja hannunta suka fice a gidan tana ta jin ta wata iri ba yanda ta saba fita ba. Wajen taron ma da suka isa kasa sakewa ta yi har matar abokin na shi wacce take murnar shagalin k'arin shekarar d'aya daga cikin yaranta ta masa magana ko me yake damunta, cike da takaicin halin k'auyenci da dabbanci a ganinshi na Saleema yace "Ba komai, iskanci ne kawai."

Dan a ganinshi k'auyenci ne duba da yan uwanta da sauran yaran yanda suka sake cikin yara yan uwansu suna ta tik'ar rawa dalilin k'aton redion da aka saka musu, sai ita da ba ta waye ba za ta wani had'e wuri d'aya kamar mai jin mugun sanyi.

Dawowarsu ke da wuya ya samu kiran waya daga malamin Saleema, dan ba ya kirashi da malaminsu duka ba saboda su Hadeeya sai sun ga dama suke zuwa makarantar islamiyya, Saleema ce dai babu abinda ke hanata zuwa dan ba ciwo ba, bayan sun gaisa a tsanake da mutumtawa malamin ke fad'a masa "Alhaji dama akan Saleema ne, shiyasa na ce bari na kira muyi magana."

Gabanshi ne ya fad'i dan abu d'aya tunaninshi ya bashi, wato a islamiyar ma bata gane komai? A nutse malamin ya d'ora da "Dama Saleema na d'aya daga cikin hazik'an yara a islamiyar nan, kuma abun birgewa yanda take da matuk'ar fahimta akan ilimin hadith, to dama akwai lokacin da aka ware ga maye da suke d'aukar karatun hadith, shine nake neman alfarma ko za'a lamunce mata sai ta dinga zuwa lokacin da za'a yi darasin? Zai zama idan an tashi k'arfe sha biyu na rana ita ba za ta koma gida ba za su wuce ajin d'aukar hadith, k'arfe d'aya da rabi sai a sallamesu."

Shiru Alhaji Yusuf ya yi yana tunanin abinda malamin ya fad'a, sai shed'an ke raya masa to dama tana gane karatun islamiya na boko ne ba ta ganewa? Sai kawai zuciyarshi ta raya mishi ai da gangan ne ta ke k'in aje hankalin a boko, tunda gashi tana gane hadith. Jinjina kai kawai ya yi yace "Shikenan."

Ya kashe wayar da tunanin matakin da zai d'auka, har ya yanke hukunci bai sanar da kowa abinda zuciyarsa ta yanke masa ba, yana jiran lokaci yayi ya zartar kawai kowa ya gani ya kuma sani.

*Washe gari*

Ganin ta dawo da kuka yasa ta tarbeta cike da kulawa tana tambayarta "Saleema, me ya faru ? Wa ya dakeki?"

D'aga kanta tayi tace "Abba ne a waje yace wai na dawo, kuma wai daga yau ba zan sake zuwa makarantar ba."

Da mamaki sosai a fuskarta tace "Ban gane ba za ki sake zuwa ba? Me kika masa?"

Cikin kuka tace "Nima ban sani ba, kawai koroni yayi."

Numfashi ta sauke tana ji akwai dai wani abun, amma haka kawai ba zai hanata zuwa makaranta ba, nuna mata gado tayi tace "Zauna nan, bari na je na ji me ki ka yi."

Za ta fice a d'akin Saleema tace "Mama idan ya ce wani abu na masa ki bashi hak'uri dan Allah."

Murmushi ta sakar mata sannan ta fice a d'akin, a farfajiyar ta sameshi zaune da na'urarsa yana dannawa, kujerar gefenshi ta ja ta zauna a nutse tace "Abban Hajia, ta sameni yanzu take fad'a min wai ka hanata zuwa islamiya, shine na ce na san dai wani laifin ta yi ko?"

Ba tare da ya kalleta ba fuska a d'aure yace "Ba ta yi laifi ba, kawai dai na soke zuwa makarantar ne, ba kuma ita kad'ai ba har da yan uwanta."

Hankali tashe zuciyarta a kid'ime ta furta "Inna lillahi wa'inna ilaihi raju'un!"

Da sauri ya juyo yana kallon da tunanin me ye na salatin? A razane tace "Alhaji, islamiyar fa ka ce ka dakatar da zuwa?"

A k'ufule yace "Haka na fad'a Safiya, ko kina da ja ne?"

Wata wawuyar ajiyar zuciya ta sauke tace "Me ya yi zafi haka? Islamiya?"

Mik'ewa yayi a hassale ya d'auki wayarshi da na'urar sannan ya kalleta yace "Na riga da na gama yanke hukunci, na kula wannan karatun ne ya ke d'auke mata hankali tana kasa fahimtar

wanda nake so ta fahimta, shiyasa na ciresu gaba d'ayansu dan hankalinsu ya tsaya wuri d'aya."

Mik'ewa tayi tsaye tace "U'uzubillah! Alhaji ka san me kake shirin aikatawa kuwa? Kai tsaye fa kamar kana k'ok'arin ingiza yaranka ne ga mummunar hanyar da ba zata b'illar da su ko ina ba sai halaka."

Cike da shashantar da zancen ya kalleta sama da k'asa yace "Allah ko?"

Sai kuma ya ja tsaki ya wuce ya barta tsaye yana fad'in "A ganinki kenan."

Da kallo ta bishi tana jin yanda hankalinta ke sake tashi dan gaskiya wannan babban bala'i neke tunkarosu, islamiya ? Inda za'a koya wa yaran sanin ubangijinsu? Shi ne zai tsigesu saboda karatun da anfaninsa iya duniya ne kawai, shi ma a haka ba kowa da yayi shi ke morarshi ba.

Kamar wasa sai kuwa maganar nan ta zama babba, Safiya da abun ya dameta ta yi iya k'ok'arinta wajen sake tuntub'arshi, amma a k'arshe mummunan kashedi ya kirta mata cewa zai d'auki tsatsauran matakin da ya dace a kan ta idan ta sake mishi maganar nan, hakn yasa ta tuntub'i wanda take ganin sun isa su fad'a masa su ji.

Duk shekarun da suka d'auka haka ba ta tab'a faruwa ba, amma sai dayawa suke ganin laifinta dan su ma bokon suka sha suka k'oshi, dan haka suke ganin me ye a ciki to? Abinda yake ganin ya fi mishi ne ya yi sai su zuba mishi ido, wannan tashin hankalin da zulumin da ta shiga na tsawon sati biyu ya haddasa mata rashin cin abinci da muguwar damuwar da ta kwantar da ita rashin lafiya, wanda daga k'arshe cikin jikinta ya zube a wata asuba ta idar da sallah.

Kamar kowane lokaci idan haka ta faru asibiti ya kaita aka mata wankin ciki, daga bisani lokitocin suka basu shawarar ko dai za'a juyar da mahaifarta ne saboda tana daf da kaiwa matakin da hakan zai iya cutar da ita, amma sam Alhaji Yusuf ya ce bai yarda dan gaskiya har yanzu ya na so ya ga wani sabon jaririn daga wajen Safiya, saboda mata ce da ba ya shakka ko k'yamar sake had'a zuri'a da ita, haka kuma ya yi bak'in cikin rasa wannan cikin da yake ganin har ya wuce wata uku amma gashi shi ma ya tafi, karo na bakwai kenan.

*SHEKARA D'AYA*

Hankali tashe ta k'araso wajen mai gadin tana fad'in "Sani dan Allah ba ka ga in da Saleema ta yi ba?"

A ladabce ya girgiza kai yace "Tun d'azu data fita dai nan ta yi..." Ya nuna mata hannunshi na dama ya d'ora da "To kuma ban ga dawowarta ba har yanzu."

Cike da d'imuwa tace "To ka ga dan Allah ka daure ka duba min ita a shagon nan na bayanmu, nan na aiketa ta siyo min madara ga shi har yanzu ba ta dawowa ba, ina tsoron kar wani abun ne ya sameta."

Cike da son kwantar mata da hankali yace "A'a in sha Allah ma ba abin da ya faru, bari na dubo na gani."

Cikin damuwa ta amsa da "Yawwa nago..."

Mak'alewa sauran maganar ta yi sakamakon tsayawar motar Alhaji Yusuf a k'ofar gidan, da sauri ta dawo cikin gida ta tunkari komawa falo, ba wai dan babu hijabi a jikinta ba ko tana tunanin ranshi ya b'ace kan tana magana da mai gadin shi, sam wannan ba ya a tsarinshi dama, hasalima da kan shi yake fita tare da su ya zab'ar musu kalar mayafan da yake so su saka. Tashin hankalin shine aikin da ya saka ta yi masa ba ta kammala ba gashi har ya dawo, shi kuma mutum ne da baya son wasa da cikinshi, duk yanda yake girmamaka indai za kai masa wasa da cikinshi to za ku samu matsala, dalilin da yasa kenan ko Ardayi na wajen aikinta ya kan umarceta ta sarrafa mi shi wani abun, dan baya son cin komai a waje.

Tun ba ta gama shigewa falon ba muryarshi ta dakatar da ita sanda yake fad'in "Me kike nema a waje?"

Cak ta tsaya tare da juyowa a hankali tana kallonshi har ya k'araso, zagaya hannunshi yayi ta k'ugunta ya jawota jikinshi yana kallon kyakyawar fuskarta da ta firgice da tsoro, d'an jaye jikinta tayi kad'an saboda k'ofar falon bud'e take, kuma mai aiki da su Hadeeya na nan zaune suna aiki, sannan ga mai gadi dake rufe k'ofar wanda shi ma zai iya hangosu.

Jin ba ta ce komai ba yasa shi sake fad'in "Je t'écoute (ina saurarenki)."

A duburbuce ta fara fad'in "Dama... Sani ne na ce ya d..uba min Sal...eema waje."

Kallon tuhuma ya mata yace "Ina Saleemar ta je?"

Hannunta ta kai ga wuyanta ta d'an shafo tace "Aiken ta na yi nan baya ta siyo min madara, ...shi ne fa...har yanzu ba ta..dawo ba."

Da mamaki a fuskarshi ya sake k'ura mata ido ya ja baya kad'an yace "Hajiar ta wa kika aika waje?"

Marairaicewa tayi tace "Ka yi hak'uri dan Allah."

A tsawace yace "Na yi hak'urin me? Ban fad'a muku kar wacce ta tura min yara waje ba idan ba makaranta za su tafi ba?"

Kamar za ta fashe da kuka ta sake fad'in "Ka yi hak'uri, ka kira ka ce na maka kunun madara ne, sai da na duba na ga babu madara a mangaza, kuma na fad'a maka amma ka manta, shine..."

A hassale ya sake fad'in "Shi ne kika aika min yarinya waje a wannan ranar? Ina mai aikin gidan take?"

A ladabce tace "Ka san yau girkin Ardayi ne, tana mata girki ne tunda ita tana wajen aiki."

A tsawace yace "To mai gadi fa? Shi ba mutum ba ne ?"

A sanyaye tace "To ai kai ka fad'a mana mai gadi iya aikinshi gadi ne kawai, kar wacce ta mishi aiken da zai sa ya bar bakin k'ofa."

Nunata yayi da yatsa yace "Wallahi idan wani abu ya samu 'yata kan ki zan huce."

Baki wangale tace "Kai na kuma? Dan na aike ta?"

Jinjna kai yayi yace "Kina wasa kenan?"

Saleema ce ta shigo gidan rik'e da leda a hannu sai Sani mai gadi a bayanta, da sauri suka nufeta in da Alhaji Yusuf ke duba duka jikinta yana fad'in "Uwata ba abinda ya sameki ko?"

Da mamaki Saleema ta kalleshi ta girgiza kai a hankali tace "A'a Abba."

"To me ya tsayar da ke?" Cewar Safiya na kallonta da kyau, sunkuyar da kai tayi tana rarraba ido, Sani ya kalla yace "Ina ka ganta?"

Cikin ladabi yace "Wani gida ne nan kusa da shagon da aka aiketa ta shiga shan ruwa."

Da mamaki Alhaji Yusuf ya kalli Saleema yace "...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_4_

Da mamaki Alhaji Yusuf ya kalli Saleema yace "Me ya sa baki zo gida ki sha ruwan ba? Gidan ya na da tsafta ne?"

D'aga kai kawai tayi tana ci gaba da rarraba ido alamar rashin gaskiya, Safiya dake kallonta sarai ta fahimci gidan da ta je, wato ta tsaya wajen Hafsatu mai d'inki ko? Girgiza kai kawai tayi ta mik'o hannu ta karb'i ledar aiken ta shige ciki, cike da farin ciki Saleema jin Abbanta bai mata fad'a ba, Mamanta ma haka sai kawai ta shige ciki da zumud'in wayewar garin gobe dan ta je ta nuna wa Hafsatu d'inkin da ta yi kamar yanda ta buk'ata.

*Tana* idar da sallah azahar ta fito kai tsaye k'ofa ta nufa wajen mai gadi tace "K'awata ta zo?"

"A'a." Ya bata amsa, juyawa tayi za ta koma sai yace "Ga ta nan Hajia."

Da sauri ta juyo da farin ciki ta kama hannun matashiyar da ba za su wuce tsara ba, kai tsaye d'akin Mahaifiyarta ta wuce da ita kamar kullum, tana zama kan kujera ta fara ciro litattafan da

suke karatu da su, d'auko na ta tayi ta zauna kusanta tace" Yau me malam ya koya muku?"

Nuna mata tayi tace" Gashi nan, shi ne zan koya miki ke ma, kuma malam ya ce wai ki maida hankali sosai."

Da fara'a ta jinjina kai tana jin dad'in yanda malamin na su ke nuna kulawarsa a kanta, tunda aka hanasu zuwa makarantar ya ke turo k'anwarsa tana d'ora mata karatun, ya yi iya k'ok'arinshi ma su had'u da mahaifin Saleema dan su yi magana kan kar a dagula mata karatunta amma Alhaji Yusuf ya k'i yarda su had'u, dan haka Saleema ta kawo wannan shawarar duk da yana tsoron abinda zai faru, amma dai gashi izuwa yanzu har an shekara d'aya ba abinda ya faru, alamu ne na mahaifin bai iya saka ido sosai a kan yaranshi ba kenan, dan da yana saka ido akan motsin 'ya'yan shi mata da yanzu ya fahimta duba da har bayan sallah isha'i a na zuwa a d'ora mata karatun.

*Washe gari*

Mik'ewar da ta yi daga kan teburin ya sa shi kallonta yace "Mamana ba dai kin k'oshi ba?"

"E Abba." Ta fad'a tana wucewa abun ta, da kallo suka bita har ta shige d'akin, jim kad'an ta fito daga d'akin da jakarta da ta b'oye a cikin hijabi ta nufi hanyar fita, Safiya ce ta kalleta tace "Ina za ki je kuma ?"

Littafin makarantar ta ta nuna tace "Mama wajen Khairat zan je ta koya min lissafin nan."

Harara ta wurga mata tace "Kuma shine sai yanzu da safiya za ki je musu ? Ki..."

Da sauri Alhaji Yusuf ya katseta da fad'in "Karatu fa ta ce za ta je, ki barta ta tafi."

Kallon Saleema ya yi yace "Uwata ta kaina, je ki kin ji sai kin dawo."

Ai da sauri ta wuce kamar za ta daka da gudu saboda farin ciki. Tana fita ba ta zame ko ina ba sai gidan Hafsatu, kayan da ta nuna mata yasa Hafsatu mamaki da ta tabbatar mata ita tayi duk da na yara ne, da mamaki ta sake kallonta tace "Amma ta ya kika d'inkasu?"

Cike da jin dad'in an yaba mata tace "Idan Mamanmu suka je karb'an d'inkinsu ne wajen tela sai na hau na yi."

Da fara'a a fuskar Hafsatu tace "Da gaske?"

Jinjina kai tayi alamar e, ita ma jinjina kan tayi tave "Masha Allah, kinga kam da Abbanki zai siya

miki tela cikin sauri za ki iya d'inki."

Kallon fuskarta tayi tace "To amma za ki dinga koya min?"

"Sosai ma." Ta fad'a tana jinjina kai, dariya tayi tace "To zan fad'a masa."

*Ko* da ta dawo ta samu Mamanta d'aki take fad'a mata "Mama, aunty Hafsatu ta ce wai na fad'a ma Abba ya siya min tela za ta koya min d'inki."

Da mamaki Safiya ta kalleta tace "To, ke kuma yaushe kukayi haka?"

Cike da shagwab'a tace "Yanzu ai na biya can."

Kallon tuhuma ta mata tace "Kin tabbata karatu kika je ?"

Jim ta yi tana kallonta da tunanin kar dai ta fad'a mata ta hanata ko ta fad'awa Abbanta, sai kawai ta d'aga kai alamar e tare da fad'in "Allah ko Mama."

Jinjina kai tayi tace "Ni dai ba zan fad'a masa wannan shirmen ba, ki bari har ki fara koyon d'inkin tukuna, idan kika iya sai a siya miki."

Takwaf takwaf tayi da fuska tace "Amma Mama ai dama cewa ta yi idan na je can na koyo na dawo gida sai na dinga aiki da telata, ta hakane zan fi sauk'in zama *mad'inkiya*."

Girgiza kai Safiya tayi tace "Saleema, abun da mahaifinki ya ke so ki zama daban, abin da ke kike so daban."

Sake girgiza kai tayi tace "Allah ya zab'a miki ma fi alkairi."

Dariya Saleema tayi cike da yarinta tace "Mama idan na iya d'inki kinga faba sai kun kai ba, ni da kaina zan muku ke da aunty da su Hadeeya." Murmushi kawai tayi a ganinta shirmen Saleema ne kawai.

*Bayan Wata uku*

Duk girman farfajiyar gidan nan ta su cike yake da maza da mata, abun mamakin kuma yanda mata da mazan ke cakud'e wuri d'aya, kafatanin taron babu macen da ke d'auke da babban gyale bare hijab, dukansu shiga ce ta alfarma dake nuna matsayin kowace da kuma rayuwar da take ciki, kusan kowace riga da siket ne jikinta ta sagala mayafinta a kafad'a, mai d'an dama

dama a cikinsu ce za ta d'orashi duka kafad'un biyu, inda fuskokinsu ke d'auke da rantsatsiyar kwalliyar da suka biya mak'odan kud'i aka cab'a musu ita, wasunsu ma har da zubo da gashi suke ya kwanta har kan wuyansu wanda aka kashe ma kud'i, jaka da takalmi masu sababin tsini kuma suka ce ja bani waje.

Ba wannan ne abun tsaya wa a kalla ba sai yanda gurin ba zaka gane ina matar wane ko waccen ba, saboda bariki da wayewa ya sa kowane namiji ya saki matarsa a wani wurin yana gaisawa da abokai da kuma matan abokan, inda su ma matan ke gaisawa da abokan mazan da kuma matansu.

Takon tafiyarta yasa dayawa daga cikin taron juyawa suna kallon mai tahowa, Ardayi ce cikin tsadaddar shiga wacce ta dace da yanayinta, kalarta da kuma jikinta, wanda hakan yasa ta sake haska wurin gwanin birgewa, iya d'an kwalin dake d'aure a kanta ne kawai, duk rabin wuyan rigar nan a waje yake yayin da siket d'in ya matse jikinta sosai, komai na jikinta ya bayyana ya fito mata da surarta. Alhaji Yusuf dake tsaye kusan abokanshi yana kallonta, murmushi kawai a saki ganin yanda abokanshi ke kallonta alamu ne na ta birge sai abun ya sa ya ji dad'i da jin cewa lallai ya yanko wulak'anci wannan wurin, duk da 'yar k'ibar dake gareta amma ba za ka ganta ka ce ita ta haifi su Hadeeya ba saboda iya d'aukar wanka.

Saleema na gefe zaune akan kujerar k'arfe mai zaman mutum biyu, daga nan take hangen irin bidirin da ake inda hankalinta ya fi karkata kan irin d'inkunan dake jikin mata, duk da k'arancin shekarunta amma tana mamakin yanda mahaifinta ya fi ba wa wannan rayuwa mahimmanci fiye da komai, ita dai a kan idonta ta ga ya kashe kud'in da suka ba million baya a kan abinda za'a tarbi bak'in nan kawai saboda su tayashi murna na girma da ya k'ara samu a wajen aikinshi kasancewarshi malamin kud'i, a iya saninta ita dai ba ta tab'a ganin wata bajinta da mahaifinta ya yi ba ga addininshi da zai nuna ya na kishin addinin na sa, dama dama ma idan azumi ya zo, a masallacin dake jikin gidan na su ya kan sa wa ana fitar da abun bud'a baki ga mabuk'ata, sai kuma abun sahur idan aka fara sallah tahajjud, wannan ne za ta iya cewa aikin alkairin dazata iya shaida mahaifinta na yi.

Maida kallonta tayi kan Hadeeya da ta shirya ko ta ce mahaifiyarsu ta shiryata cikin wata arniyar rigar kanti iya gwiwoyin Hadeeyar, ta yi kyau sosai dan ka rantse ma yar turawa ce, sai dai a ganin Saleema kamar ba ta dace ba, sam gani take yi shigar ba ta birgeta ba. A hankali ta sadda kanta kan takardarta fara tas sannan ta fara zana wuyan rigar da ta ga Mamanta ta saka d'azu ita ma da za ta zo wajen taron, dan wuyan ya burgeta sosai hakan yasa ta tsurawa rigar ido ta gama hardaceta a kan ta kafin Safiyar ta saka.

Kiran da aka masa a waya yasa shi d'agawa ya na d'an matsawa daga wurin ya amsa da "Ina jinka Abdul, ka zo ne ?"

Jim ya yi alamar ya na sauraren me maganar kafin yace "Ok ina zuwa."

Hanyar fita ya nufa yana fad'awa mai gadi "Bud'e k'ofa akwai wanda zai shigo."

Bud'e k'ofar mai gadi ya yi ya fita har k'ofar gidan yana dubawa, cikin wata tsadaddiyar mota bak'on ya fito tare da matarshi da ita ma ta gaji da had'uwa, gaisawa sukayi sosai kafin ya musu alama da su wuce gaba, suna shiga shi ma ya bi bayansu da niyyar shigewa muryar Hafsatu ta dakatar da shi daga niyyar shigewar tana fad'in "Ina wuni Abban Saleema."

Juyowa ya yi yana ganinta ganin dai ya d'an shaidata wasu lokuta Safiya na kai mata d'inki yasa shi d'an sakin fuskarshi ya amsa da "Lafiya lau, ina wuni ?"

"Lafiya lau, ina Saleema ?" Ta fad'a da fara'arta, ba yabo ba fallasa ya amsa da "Ta na ciki."

Murmushi ta yi tace "Saleema kenan, akwai k'ok'ari wallahi, idan ta yi wani abun ba za ka ce yarinya ce ba, shiyasa ma na ce ta fad'a maka a siya mata telarta, dan hakan zai fi kawo mata sauk'i."

Da mamaki da kuma rashin fahimtar inda zancenta ya dosa ya gyara tsayuwarsa yace" Tela kuma?"

Ba tare da tunanin komai ba tace" E, idan aka siya mata mai aiki da lantarki ma za ta fi gaskiya."

Har yanzu dai da mamakin ya sake cewa" Dama ta na koyon d'inki ne?"

D'an shiru ta yi sai kuma tace" E, ta yiwu ka manta dai, ai kusan wata uku kenan da ta fara zuwa, dan ma ba na koya mata wasu abubuwan saboda k'arancin shekarunta."

Wani kallo ya mata lokacin da idonshi suka fara yin launin ja na b'acin rai dan jin yaudara da ha'intarshi da Saleema da kuma mahaifiyarta sukayi, wato idan ya fahimta duk lokacin da Saleema ta ce mishi za tatafi karatu can ne ta ke zuwa? Jinjina kai kawai ya yi ya shige bayan ya furta "Nagode."

Ya na shiga inda ya hangi Saleema zaune ita kad'ai ta dasa kanta k'asa ta na zana abu a takarda ya nufa, ya na zuwa kam takardar ya fincika da k'arfi, hakan yasa rabi ta yage ta bi hannunshi rabi kuma a hannun Saleema da ta d'aga kanta tana kallonshi a tsorace. Kallon takardar ya yi ya ga ta zana sanfirin wuya, duk da bai gane komai ba amma ya fahimci dai abunda aka fad'a gaskiya ne dan ga shaida nan.

Tsaye ta mik'e tana zazzare ido ta na kallonshi, tsareta ya yi da ido yace "Me ye wannan?"

Rarraba ido ta fara yi na rashin gaskiya, kafin ta ce wani abu Safiya da ta hangesu ta kuma kula kamar ba lafiya ba ta taho tace "Lafiya Alhaji?"

Rai b'ace ya kalleta yace "Me ye wannan?" Ya nuna mata takardar? Kallon rashin sani da

fahimta ta ma takardar sai kuma ta girgiea kai tace "Ban sani ba, me ye wannan d'in?"

Nuna kanshi yayi yace "Ni ma kike tambaya?"

Sai kuma ya jinjina kai ya nunasu da yatsa yace "Ku jira a gama taron nan zan ji daku dukkanku."

A fusace ya wuce ya barsu inda Safiya ta kalli Saleema tace "...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_5_

A fusace ya wuce ya barsu inda Safiya ta kalli Saleema tace "Me kika masa kuma yanzu?"

A raunane tace "Ba abun da na yi, irin wannan zanen ne fa nake yi."

Ta fad'a tana nuna wuyan rigar Safiya, tab'e baki Safiya ta yi tace "Kin tabbata?"

Jinjina kai tayi tare da cewa "Allah ko."

Jinjina kai tayi tace "Shikenan." Juyawa tayi ita ma ta barta nan ta ci gaba da abinda take. Duk wannan shagali da abinci da aka shiga rabawa bai wani d'ad'a Saleema a k'asa ba, haka take abinda take ganin zai fisheta yayin da suma suke wanda ya fishesu, sai da dare ya yi sosai kafin su fara watsewa daga gidan.

*Mamakin* dalilin da yasa ya kirasu b'angarenshi take da kuma yanda ya taso Saleema a baccin ta, gashi ya musu tsaye k'erere har da wani rik'e d'amara a hannu alamar dai duka zai yi, sai dai ba ta san wa zai daka ba a cikinsu, ita ko Saleema ? Indai ita ce abun da bai tab'a faruwa ba ne, ko mari bai tab'a had'ashi da mace ba, bar shi dai ya rufeki da fad'a idan abu ya yi k'amari ya k'aurece miki, amma ban da duka.

Zuba masa ido ta yi tana jira ta ji me zai ce, sai da ya gama kumbura da kallonsu sannan ya kalli Safiya yace "Yaushe ki ka saka yarinyar nan koyon d'inki?"

Da mamaki ta kalleshi tace "D'inki kuma? Ni ban sakata koyon d'inki ba."

Wani kallo ya jefeta da shi yace "Amma ai da saninki take zuwa ko?"

Kallon Saleema ta yi da ta fara tsuru tsuru da idonta tana kakkame jikinta a sakan biyu kuma ta kalleshi tace "Ban gane ba? Me yake faruwa ne wai?"

A d'an fusace yace "Ni ne ma zan fad'a miki abinda yake faruwa? Safiya yarinyar nan wata uku kenan ta na zuwa gidan matar can mai d'inki, kina so ki ce baki sani ba ne?"

Sake juyawa tayi ta kalli Saleema da tsantsar mamaki tace "Saleema, d'inki kike koyo?"

Mik'ewa ta yi tsaye ta ja baya tana girgiza kai cike da tsoro tace "Mam...a, da..ma."

"Dama me ?" Ta fad'a a tsawace, zabura tayi ta fashe da kuka tace "Ki yi hak'uri Mama, ba zan sake muku k'arya ba."

Dafe baki Safiya tayi tace "Inna lillahi wa'inna ilaihi raju'un! Saleema k'arya kika mana dama? Da kike cewa za ki tafi karatu, dama ba karatun kike zuwa ba?"

A mugun tsawace tace "Me yasa Saleema? Me yasa kika mana k'arya?"

Cikin kuka ta kalli Alhaji Yusuf dake kallon Safiya yanda ta hahhak'e ta saye bala'in ta kasa barinshi ya furta komai, da sauri ta girgiza kai tace "Kiyi hak'uri Mama, ba zan sake ba daga yau, na rantse miki da Allah."

A hassale Safiya ta yi kanta tare da fizgar d'amarar (belt) dake hannunshi, kafin Saleema ta ankara ta damk'o hannunta rai b'ace zuciyarta na tafasa na k'arya da yanda k'aramar yarinya kamar Saleema ta yaudareta haka ta shiga labtawa jikinta bulala tana fad'in "Za ki k'ara daga yau? Ni za ki ma k'arya Saleema? Ni kika d'auka shashasha da ba ta san me take ba? Kin sake fita a gidan nan da sunan za ki je wajen d'inki ?"

Cikin kuka na bara-bara Saleema dake ta doka tsalle na azabar bulala take fad'in "A'a, A'a Mama, na tuba wallahi ba zan k'ara ba, na daina zuwa daga yau kar ki kasheni, wayyo ! Abba ka taimakeni."

Duk da shi ma ranshi a b'ace yake na turbar da Saleemar ke neman d'auka, amma kuma haihuwa ta fi gaban wasa, sai ya ji na shi b'acin ran ya fece inda zuciyarshi ta fara suya na yanda ya ga Safiya na dukanta. A sukwane ya nufosu ai kafin ya kai mata agaji Saleema da dama neman ceto take ta yi ram da k'ugunshi ta na lab'ewa bayanshi.

D'aga bulalar da Safiya ta yi za ta sake zuba mata yasa shi rik'e hannunta ram tare da jawota gaba d'ayanta ta fad'a jikinshi, tsit ! D'akin ya d'auka har Saleema dake kuka ma wacce ta tsura musu ido da tunanin kar dai dukan Mamanta zai yi? Ido cikin ido suka kalli juna duk idonsu sun yi jajir na mabambamta b'acin rai, sake damk'e hannunta ya yi sosai hakan ya tilasta mata sakin d'amarar ta na d'an rintse ido na zafin da ta ji, cikin tattausan murya yace mata "Dukan ya isa haka, kamar kin samu wata jaka za ki dinga narkar min 'ya a gabana, to kar ki k'ara."

Zamewa ta yi daga jikinshi cike da kunya tace "Ka ga ka mik'o min yarinyar nan na farfasa mata jikinta, gobe ba za ta sake min k'arya ba."

Harara ta dalla mata yace "Wallahi kika sake tab'a min yarinya ranki zai b'ace, ko ma me ta yi ai laifinki ne, shi ne za ki wani zak'alk'ale ki juye a kan ta dan kar na hukuntaki."

Kawar da kanta tayi gefe tana d'an gunguni, d'an k'aramin bakin na ta ya bi da kallo tare da lashe leb'enshi na k'asa, dafa kafad'ar Saleema ya yi ya mata alamar ta fita, dan ya kula yau Safiyar namansa take da fitina, har shi ne ma take ma gunguni haka? Cikin shashek'ar kuka Saleema ta ari na kare ta bayan mahaifinta ta fice a d'akin da gudu.

Bin ta da kallo Safiya ta yi tace ta nunata da yatsa cikin d'aga murya tace "Ai zan sameki d'akin

dan ubankkkk...."

Tsit! Ta yi dan sai da ta tasan ma fad'a ta tuna irin sub'ul da bakan da ta yi, wato a gaban shi ta zageta. K'in juyowa ta yi a hankali ta fara jan jikinta za ta fice a d'akin da sauri ya nufeta ya k'ara jawota jikinshi, tsura ma fuskarta ido yayi yace" Sofee dama tsaurin idonki ya kai haka? Hajiar ta wa? Kuma a gabana?"

Marairaicewa ta yi tace" Ka yi hak'uri dan Allah, wallahi sub'utar baki ce na manta."

Jinjina kai yayi yace" Ni dai ko? Hajia ta kika zaga a gabana, ba komai." Ya fad'a yana sakinta tare da fad'in" Je ki yi shirin bacci ki zo, na gode Allah da ya sa ranar kwananki ne kika zagar min uwata, hakn shi zai bani damar d'aukar fansata."

Turo baki ta yi ta juya za ta fita dan zuwa d'akinta ta shirya ta zo kamar yanda ya ce. Da kallo ya bita kafin ya girgiza kai ya na murmushi ya zauna bakin gadon.

*Washe gari*

A ladabce ta shigo d'akin tana fad'in "Asaalama alaikum."

Safiya dake kwance da k'yar ta tashi zaune tana amsawa da "Wa'alaiki salam."

Kusan gadon ta k'arasa ta tsuguna tace "Mama, kin ga safiya ta yi kuma ba inda muke zuwa, yanzu kinga na fad'a miki gaskiya, zan iya tafiya wajen aunty Hafsatu?"

Harara ta watso mata tace "Saleema jiya ya mukayi da ke? Ban ce kar na sake ji ko gani ba?"

A shagwab'e Saleema tace "Dan Allah Mama ki barni na tafi."

A tsawace tace "Ke tashi, tashi ki bani wuri, kuma wallahi kika sake min maganar nan ranki zai b'ace."

Mik'ewa tayi ta juya za ta fita ta bita da harara ta na fad'in "Ka ga min yarinya, ina zaman zamana ki hassalani kuma ba daman na zageki yanzun nan ubanki ya sake titsiyeni."

Gyara kwanciyarta ta yi tunda dai yau ba aikinta ba ne tana fad'in "A bar ni na ji da abinda ke damuna mana."

Alhaji Yusuf da ke jinme take fad'a yana daf da shigowa ne yace "A ma sake kuskuren zagar min uwata wallahi."

Harara ya dalla mata yace "Yar rainin wayo." Da mamaki ta kalleshi tace "Ni d'in?"

"Ke d'in mana, ko akwai magana ne?" Girgiza kai ta yi alamar a'a, Saleema da ba ta yi nisa ba ya k'wala ma kira ta dawo d'akin, tana zuwa ta tsaya tana kallonshi, cike da gargad'i da jan kunne ya zaro mata ido yace "Kina ji na? Daga yau sai yau kar na sake jin kin yi maganar zuwa wajen koyon d'inki, idan ba haka ba kuma wallahi da kaina zan hukuntaki."

A tsawace yace "Kin ji me na fad'a?" Da sauri ta d'aga kai alamar e, nuna mata k'ofa ya yi yace "Wuce."

Juyawa ta yi jiki a sab'ule ta fita a d'akin ta na jin ba dad'i sam, saboda burinta ne ake neman hanata cimma shi, amma ya zata yi da ya wuce ta hak'ura kawai.

*Tafiya* ta yi nisa, amma har yanzu babu abinda ya canza daga rayuwar su, islamiya sun cire rai da sake komawa, saidai Saleema dake mai wayo ce har yanzu ta na d'aukar karatunta wajen kanwar malaminsu, wanda a shekarun nan ta k'ara sanin abubuwa dayawa, musamman da yanzu ta k'ara wayo da shekaru, sai ya zama har wayar mahaifiyarta take d'auka ta kira malamin su sake tattaunawa kan karatunta. A karatunta na boko ma har yanzu ba abinda ya sauya, duk yanda take son ta birge mahaifinsu ita ma wajen ganin ta yi k'ok'ari abun ya ci tura, sai ma k'ara lalacewa da lamarin ke yi saboda ta hak'ura ta d'auke hankalinta daga karatun na boko, tana yi ne kawai ba dan ranta na so ba sai dan mahaifinsu, hakan ya sa shekara biyu ta na maimaita wani ajin har Hadeeya ta risketa, shima kuma sai Hadeeyar ta yi gaba tana neman barinta, abinda Alhaji Yusuf bai tab'a yi bane ya yi a wannan karan, wato bayar da cin hanci da kuma neman alfarma aka izasu tare da Hadeeya dan baya so ta barta a nan.

Yanzu dai haka suna ajin zana jarabawar BEPC, ya ma ta k'wak'waran kashedi in har ba ta ci jarabawar nan ba to shi kad'ai ya san me zai mata, hakan yasa ta d'an sake maida hankalinta ta na son ganin bai mata abinda ya bar wa ran na shi ba, sai daia inda ta koyi abun a nan take tashi ta barshi, ta na shiga d'aki za ta nemeshi ta rasa.

*Farkawa* ta yi don yin fitsarin da ya addabeta, ta na tashi zaune idonta suka sauka kan Mamanta ta d'ora goshinta k'asa ta na kai kukanta ga sarkin sarakuna mai kowa mai komai, da alama ba ta kwanta ba kenan tun da suka rabu da sai da safe, dama kuma idan ba kwanan Mamanta ba ne d'akinta take kwana dan ta fi jin dad'in hakan. Sauko da k'afafunta ta yi ta na ci gaba da kallon mahaifiyarta wacce ta ke da yak'inin ita kawai take wa addu'a, dan watannin nan ta cika saka damuwa a kan ta wanda ba ta san dalili ba, haka kuma da ta ga tana yawan tsayuwar dare da azumin nafila sai ta ce ta na yi ne saboda ta na so ta yi nasara a karatunta ita ma mahaifinta ya yi alfahari da ita.

Mik'ewa ta yi ta shiga ban d'akin ta yi abinda za ta yi ta fito, zaune ta sake yi bakin gadon ta na kallon mamanta da sai yanzu kad'ai ta d'aga. Bayan wasu mintuna ta sallame sallar dan ta ji me ya sa Saleema ba ta koma ta kwanta ba? Kallonta ta yi murya a tausashe sosai saboda daren

da ya tsala yace "Lafiya ba ki koma ki ka kwanta ba?"

Numfashi sosai Saleema ta ja kafin tace "Mama, ki kwanta ki huta mana, gobe za mu fara jarabawar, idan Allah ya k'addara zan samu zan samu."

Ajiyar zuciya Mamanta ta sauke ta na d'an murmushi na dattako tace "Ko da kun gama jarabawa Saleema ba zan daina yi miki addu'a ba, ina so na ga kema mahaifinki ya baki kyauta ko sau d'aya ne."

Girgiza kai Saleema ta yi tace "Mama, wai me yasa ni Abba ba ya so na ne? Saboda ba na da k'ok'ari a makaranta?"

Girgiza kai Mamanta ta yi tace "Ba haka bane, ya na so dai ya ga ke ma kina k'ok'ari ne."

Cike da damuwa a fuskarta tace "To amma Mama ilimi ba na Allah bane? Na yi iya k'ok'arina dan ganin nima na zama kamar su Hadeeya, amma abun ya gagara."

Cike da gasgatawa maman tace "Hakane Saleema, ilimi na Allah kula ya na ba wa wanda ya so, amma wasu lokutan idan ka sa wasa sai Allah ya bar ka da shirmenka."

Da tuhumammen kallo ta bita tace "Mama kina ganin ni ba na jajircewa ne? Ina fa k'ok'ari sosai, kawai dai abunda na sani na fi son karatun islamiyya saboda shi na fi ganewa a sauk'ak'e."

Murmushi ta sake yi cike da dattako tace "To shikenan, Allah dai ya bamu nasara wannan karan."

"Ameen Mama, zo ki kwanta to." Girgiza kai ta yi tace "A' a, ke ki je ki kwanta, ni zan ci gaba daga in da na tsaya."

Ita ma girgiza kai ta yi tace "A'a, ni ma bari in tayaki, ba zan iya bacci ba alhalin ki na tsaye a kaina."

D'an murmushi ta  sake yi ta mik'e tsaye dan ci gaba daga in da ta tsaya, ba jimawa Saleema ta fito bayan ta d'auro alwala ta zo ta shinfid'a sallaya ita ma ta bi sahu a gefen mahaifiyarta.

*Saboda comment d'in da ku ke suburbud'awa*🥰🥰 ga mai so ta yi magana dan shiga *grp d'ina*

*Alhamdulillah.*

24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_6_

*12:20* suka fito daga aji sun gama zana jarabawarsu, ranar da ake kwantsamawa ya sa ta nufi inda ke da ruwa dan sha ko ta ji sanyi saboda kakarewar da jarabawar ta mata a aji, dama dai ita ba wasu k'awaye gareta ba, to ta ya ma za su yi k'awaye? Bayan mahaifinsu ba kowace k'awa ya ke barinsu da ita ba sai mai ilimi irin na su, idan kuma ba ki da to ko kin zo wajensu zai sa mai gadi ya hanasu shiga, hakan ya sa ma tsakaninta da k'awa makaranta a gaisa a yi raha kawai a wuce wurin, ita ba waya gareta ba duk da shekarunta *goma sha takwas* a duniya, amma mahaifinta ya hana mata waya ya ce a haka za ta ji haushi ta yi k'ok'ari ita ma saboda ya ga yanda waya ke da tasiri a rayuwar matasan yanzu, hakan yasa ya siya ma su Hadeeya manyan wayoyi uta da Hameeda amma ban da ita, wai a dole sai ta ji haushi, amma abunda bai sani ba shi ne ko a jikinta, tunda dai ta na aiki da ta Mamanta ai shikenan.

Ta na zuwa gaban fanfon sai da ta aje yar jakarta k'arama sannan ta cire hijabinta ta zauna bakin dandamalin ta fara d'aura alwala, a iya saninta da ganinta dai ba kowa wajen, dan haka ma ta dinga alwalarta a tsanake har da ture d'an kwalinta ta shafa kai.
Ta na idawa ta mik'e ta na karkad'e hijabin na ta da ya d'auki lemar ruwa, a cikin karkad'eshin da take ne ta d'an juyo da kan ta kad'an. *Kwatsam* idonta su ka sark'e da na balagaggen namijin da ba ta tsammaci ya na wurin ba, da mugun sauri ta durmiya hijabinta ta juya bayanta cike da mad'aukakiyar kunyar da ta kasa misaltawa, gaban Mamanta kad'ai ta ke iya zama da yar rigar nan da ke jikinta, gashi yau ta yi saken da waccen *Alhudahuda* ya gama kalle mata jiki.

Da k'yar ta sunkuya ta d'auki jakarta ba tare da ta yarda ta sake kallon wajen ba, dan irin kallon da ta ga ya na mata abun ya bata tsoro, gashi ta na jin kunyarshi sosai, saboda wasu lokuta ana turoshi ajinsu ya kula da su idan babu malami, dalilinta na kiranshi alhudahuda kuma shi ne irin darasin da yake koya musu na lissafi mai matuk'ar wuya, hakan ya sa da an turoshi ajin za ka ga yan mata da samari kowa na kawo masa rub'abb'en lissafin da ya kakare masa a kwanya dan ya warware masa. Ita kam tsakaninta da shi ido ne shi ma a akasi idan sun sark'e, kamar yanda ba ta damu da shiga abinda bai shafeta ba, haka ta kula shi ma ba ya shiga sabgar da ba'a saka da shi ba, dalilin da yasa kenan ko sannu ba ta tab'a had'asu ba, kuma ta ji ma an ce shi ne shugaban matasa na makarantar.

Sum sum sum! Ta nufo hanyar wucewa wacce dole ta gefenshi za ta ratsa ta wuce, hakan yasa ta k'ara sadda kanta k'asa dan ba ta so su had'a ido, sai da ta zo daf da shi har ta d'an wuce kad'an *Huzeifa* da ya shiga halin d'imuwa da tashin hankalin da bai tab'a riskar kanshi ba ya yi k'arfin halin d'an matsawa kad'an da tunanin kar ta k'arasa warware masa alwalarsa ya na ambaton "A'uzubillah!"

Duk da ba ta tsaya ba amma sai da ta saci kallonshi ta gefen ido da son gano me ya ke wa a'uziyya? Ido suka sake had'awa dan shi mamakinshi bai wuce "Wai dama haka ta ke a cikin dogon hijabin nan?" Ba, shi ya na ganinta ba ruwanta ashe bama-bamai ne a cikin hijabi, tsakani da Allah da Annabi ya d'auro alwalawarsa ya zo da niyyar d'an tab'a karatu kafin 12:30 ta yi ya yi sallah, sai kawai ya wani sameta zigidir haka daga ita sai siket da k'aramar riga, anya kuwa ta san halin da ta sakashi a ciki? Shi fa idan ka cire matan banza da ya ke gani a tv wanda ya ke iya k'ok'arinshi wajen ganin ya kare kanshi daga kallonsu, da kuma ko da ya kallesu ba abinda yake ji, shi bai tab'a ganin irin haka ba, k'annan shi ma mummunan kashedi ya kirta musu kan zama haka a cikin gida. Yanzu ga shi yarinyar da ko sunanta bai sani ba ta gayyato masa da wata lalurar da bai san ya na da ita ba.

Wannan kallon mamakin da Saleema ta hango a k'wayar idon shi ya sa ta tunanin ko dai ji yake shi ma malaminsu ne ? Nufinshi kuma ta gaisheshi? Sai kawai zuciyarta ta raya mata ai ba komai ba ne, gaishe shi ya ci albarkacin malaman. D'an tsayawa ta yi ta sake kallon inda ya ke amma ba ta kalli fuskarshi ba tace "Ina wuni."

Tsura masa ido ta sake yi ganin mak'walaton wuyanshi ya yi sama da k'arfi alamar ya had'iyi yawu sannan ya yi k'asa kamar wanda ya had'iyi kunama, da sauri ta d'aga k'afafunta za ta bar wurin ta ji rikitacciyar muryarshi mai bala'in sanyi da taushi wacce ta dace da yanayinshi na sahihin namiji mai sassauk'ar k'ira yace " *Ya sunanki*?"

Cak ta tsaya tare da juyowa a hankali ta sauke ido a kan shi, kamar ba za ta amsa mi shi ba sai kuma a sanyaye ita ma sosai cike da ladabi da kamun kai tace "Sunana kuma?"

Ido kawai ya iya lumshewa alamar e, d'an kawar da kanta tayi gefe sannan tace " *Haleematu Yusuf Saddi*."

A kan labb'anshi ba tare da ya san maganar za ta fito fili ba ya sake furta "Haleematu."

Kallonshi ta yi da kyau sai kuma ta juya ta ci gaba da tafiyarta, bai daina kallonta ba har said ya ji zuciyarshi na tambayarshi "Haba Huzeifa, wannan kallo ai ya wuce k'ai'da."

Da sauri ya d'auke kan shi yana jan d'an gemunshi da ya tara dan koyi da sunna tare da fad'in "Astagfirullah! Allah na tuba ka yafe min, a'uzubillah, shaid'an me ka yi haka? Ya aka yi ka samu nasara a kai na yau?"

Dab'as ya zauna a dakali ya na ci gaba da furta neman tuba ga mahaliccinshi kan ya gafarta masa, dan ya tabbata da shi ta ke fuskata da ta ji kallon ya fara cutar da ita, wanda kuma aka hana a shari'a cewa _" Bai halata ka dinga kallon musulmi ba kallo wanda zai cutar da shi, sai dai in ya kasance fasik'i ne, to k'aurace masa ya zama wajibi."_

In da a farkon karatun littafin Akhdari kuma aka lissafi a jerin abubuwan da baligi kuma ak'ili ya kama ya kiyaye shi ne _" Kallon ajnabiya (manisanciya-wacce ta ke ba muharramar ka ba), sannan ka kiyaye jin dad'in zancenta._

*Yau*  kam suna cikin farin ciki na gama jarabawarsu, ko ba komai sun samu hutu su ma daga ranar da ake k'wlawa, musamman ma Saleema da take ganin wahalar banza take, sai dai farin cikin na ta ya koma ciki sanda mahaifin na su ya umarcesu da su shirya zai sa dreba ya kaisu gidan *Alhaji Auwal* wanda zai iya cewa mai gidanshi ne a fannin siyasa, dan shi ya kama hannunshi ya durmiya a cikin tafiyar, duk da a girme ya girmeshi nesa ba kusa ba, dan ko Yayan Alhaji Yusuf d'in ya girma amma suna mutumci da mutumta junansu.

A tsanake mamanta ta kalleta tace "Saleema, lafiya ki ke ta had'e fuska?"

K'ara turo baki ta yi gaba ta na k'ok'arin saka rigarta duk da sanye take da hijab saboda kunyar Maman da ta ke ji ba za ta iya tub'ewa a gabanta ba tace "Ni wallahi Mama ba na son zuwa gidan nan, dan kar Abba ya ce na rainashi zan tafi kawai."

Murmushi Safiya ta yi da mamakin wai Saleema ba za ta iya saka riga a gabanta ba dan kar ta lafiyayyen k'irjin da ya cika mata gaba tace "To wai me ya sa ba kya so? Can ma gidan hutu ne fiye ma da na mahaifinku."

Juyowa Saleema ta yi ta kalleta tace "Mama, ba wannan ne matsalar ba, kin san ko k'auye zan iya rayuwa, kawai dai yaran nan na sa ne ni wallahi ba su kwanta min a rai ba."

Da mamaki Maman tace "Su wa kenan?"

Cike da yatsina fuska tace "Yan mazan mana, duk ba su da tarbiya wallahi."

Rik'e hab'a Maman ta yi da mad'aukakin mamaki tace "Ikon Allah! Saleema yaushe ma ki ka musu sanin da ki ka gane haka? Shin *Mu'az* d'in da ko shekara bai yi da dawowa daga karatu ba? Ko kuma *Mu'awwaz* d'in da ke da tsantseni da share mutane?"

Ta na gama saka rigar ta cire hijabin ta na saka zip tace "Dukansu Mama, wallahi kura ce da fatar akuya, dukansu rainawa mutane hankali suke, ba ma kamar tuzurun nan."

Dariya Maman ta sake har da k'yalk'yalawa tace "Wa ye tuzuru kuma?"

Ba alamar wasa tare da ita tace "Shi Mu'az d'in mana, shekara talatin ba aure amma ya na nuna bai damu da komai da kowa ba, hmmm ! D'an rainin hankali kawai."

Maman ta dai abun dariya da mamakin yanda ta hak'ik'ance ta na ta sababi take, to ita ba ta ma san yaushe ta musu wannan sanin ba haka? Tabbas sun tab'a zuwa gidan amma fa tun ba ta kai shekara goma ba a duniya, duk da ta san ta bata da mantuwa kan abin da ya shafi rayuwar duniya da karatunta na islamiyya, amma dai ba ta tunanin har yanzu ta na tune da abinda ya faru shekara *tara* da ta wuce.

Haka ta gama shiryawa amma sam ba ta so haka ba saboda ita ta gama fahimtar duk wani da Abbansu ke alak'a da shi ta kusa sosai to d'an boko ne da ke da wayewa, sai dai na wani ya fi na wani kawai. Ta na gama shiryawa ta fito farfajiyar, a nan ta samu su Hadeeya har da mahaifin na su a tsaye da alama so ya ke ya ga tafiyarsu da kuma Mamansu gefe ta na amsa waya.

Sanye take da doguwar riga wacce gaba d'aya gabanta yake a bud'e, ma'ana aka masa doguwar tsaga har zuwa cibiyarta, sai siket d'in atamfar da ya rufe mata cibayar inda a baya kuma yake yage da tsaga shima har idan tana tafiya kamar za ka hango gwiwoyinta, k'aramar jakarta ta rataya ta tsakiyar wuyanta da hannu, sai takalmin kalar jakar masu d'amara da rufaffiyar sama, kwalliya ce ta ban mamaki ta d'auka sai dai ko d'an kwali babu a kan ta, hasalima d'an kwalin rik'e yake a hannunta, a hakan wai shi ma wani kalan tsarin ne.

Kayan sun matseta sosai yanda suka fito da kyakyawar surarta da kuma kyawun fuskarta, masha Allah kuma abun ka ga farar fata sannan mai kaurin jiki, hakan yasa Hadeeyar ta zama basu da maraba ita da Saleema da ta bata shekara uku da haihuwa saboda su na da kumari.

Cike da rashin jin dad'in yanda ta ga yan uwanta sun shiryo ta kalli Hadeeya a tausashe tace "Haba Hadeeya, wannan wace irin shiga ce? Kina 'yar musulmai amma ki fita haka kanki babu rufi? Idan ma ba zaki saka hijab ba ko gyale ne ki saka mana."

Cikin tsiwa da raini da kaud'i Hadeeya ta kalleta tace "Ke kuma malama ina ruwanki da shigata? Kina da matsala da hakane? Ka ji min mata kai, so kike na yi irin shigarki kamar wata matar aure?"

Kafin kowa ya yi magana Ardayi da aka mata kiran gaggawa a wajen aiki ta k'araso da sauri kai tsaye mahaifinsu ta tunkara cikin shagwab'a tace" Bébé, kira ne da wajen aiki ana buk'atata yanzu, zan tafi sai na dawo..."

Ta yi maganar ta na fad'awa jikinshi ta sumbaci labb'anshi tare da d'agowa tace" Ba zan jima ba Bebe, sai na dawo."

Saleema da tun da ta ga ta nufeshi ta d'auke kanta saboda kunya, shi kan shi yanzu da shekaru su ka k'ara ja ya kan ji nauyi idan irin haka ta faru, sai dai Ardayi ta saba kuma ba ta ganin hakan a matsayin wata matsala.

Hannu kawai ya d'aga mata bai iya furta komai ba har ta k'arasa kusan su Hadeeya da ba ta san akan me suke magana ba ta rumgume su su ma musamman Hamdeeya har tana fad'a mata "Shoyerta (autata) ki kula da kan ki."

"To Momma." Ta fad'a cike da farin cikin za ta tafi unguwa na wasu kwanaki, suna kallo ta shiga motarta ta bar gidan.

Sai lokacin Hameeda da ita ma dai wata arniyar shigar riga da siket na shadda ne jikinta tace" Kama da matar auren ma wacce ta haihu, dan wannan hijabi da ta saka sai matan aure masu 'ya'ya, dubi fa daga nan baya har k'asa yake ja mata."

Kallon hijabin na ta sukayi kam mai hannaye wanda ya mata kyau sai kawai suka bushe da dariya suka tafa hannu Hadeeya na fad'in" Wa ya ga ta Allah."

Murgud'a baki Hameeda tayi ta harari Saleema tace" Wai a haka za ta bi mu, ki ga fuskarta ko hoda ba ta murza ba sai k'yallin mai take, mtssss! Ni wallahi da Abba da ma ka hanata zuwa."

Wani kallo Saleema ta ma Hameeda sai kuma ta kalli mahaifin na su da duk da yana jin me ke faruwa amma hankalinshi na ga waya yana latsawa tace" Abba ka a yaran nan magana mana, dubi fa shigarsu?"

Wayar da ya d'ora a kunne ya sa shi nuna mata su wuce su tafi kawai dreba na jiransu, cike da takaicin halin ko in kula ta fara yin gaba ta shige motar.

Tsaki Hameeda ta sake ja har suka k'arasa kusa da mota inda dreba ke jiransu suka shiga ya jasu zuwa gidan.

*______________*

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_7_

Tabbas sun yarda Alhaji Auwal ya fi mahaifinsu kud'i nesa ba kusa ba, dan daga irin ginin da ya tarwatsa za ka fahimci haka, da kuma irin kayan alatun da suka k'awata gidan, ba su daina kalle kalle ba har mai aikin da ta musu jagora zuwa cikin gidan suka shigo k'aton falon.

Saleema da ke baya cikin sharb'eb'en hijabinta kallo d'aya ta ma uwar gidan ta saki murmushi saboda tuna shekarun baya da su ka sameta tana cikin ganiyar k'uruciyarta mace yar gayu da wayewa, amma yanzu shekaru sun lak'ume duk wannan ji da kan da k'uruciyar, ba abinda ya rage mata face dattijuwar fuskarta mai d'auke da gilashi.

Kusanta suka fara zuwa inda take zaune, Hadeeya da Hameeda daga tsaye suka gaisheta da "Ina yini?"

Hamdeeya kuma kusanta ta zauna dan ta san matar ita ma tana wangale mata baki sai dai ba ta ce mata komai ba, yayin da Saleema dake gefe ta durk'usa kamar za ta yi zaune tace "Ina wuninku Mama."

Da fara'a da kuma jin dad'in gaisuwar ta Saleema ta kalleta cike da kulawa tace "Lafiya lauSaleema, kina lafiya?"

"Lafiya lau." Ta fad'a cike da kunya, maida hankalinsu sukayi kan wata dattijuwar da ke shigowa falon hannunta rik'e da waya, kallo d'aya suka mata ita ma suka gaisheta kasancewarta amaryar gidan. Cike da yauk'i da jan aji ta wani yatsina fuska tace "Lafiya lau, har kun iso ?"

Kafin kowa ya ce wni abu Hameeda ta kalleta tace "Aunty ina *Ummeeta*?"

Cike da yatsina fuska tace "Ta na ciki." Ta fad'a tana nuna mata k'ofar da ta fito, mik'ewa Hameeda ta yi ta nufi d'akin suka bi bayanta da kallo, wani d'an murmushi amaryar ta saki saboda sak ta hango Hameeda da d'anta Mu'awwaz a matsayin ma'aurata, a ganinta ba k'aramin kyau za su yi ba. Dan haka ma ta wuce inda za ta je ta na ayyana abubuwa da dama a game da ganin Hameeda, dan sam shigarta ba ta d'auketa bakin komai ba sai kawai wayewa da zamananci, sannan ta na da labarin ilimin yaran daga wajen mahaifiyarsu.

Hajia *Rabi* ce ta kalli su Hadeeya tace "Ku wuce ciki kuma, kun san ana rana duka yaran su na bacci."

Tab'e baki Saleema ta yi a ranta ta ayyana "Tunda an saba musu ba."

Mik'ewa sukayi Hajia Rabi ta kalli mai aikin tana fad'in "Ki nuna musu inda aka gyara musu, idan

su ka yi wanka sai ki kai musu abinci."

Kallonta Saleema ta yi sanda suka kama hanyar d'akin tana mamakin to wankan me za su yi? Ba fa daga wani garin suke ba, tafiya ce da ba ta wuce minti ashirin ba, amma dai ba ta ce k'ala ba suka wuce cikin.

*______________*

K'aramin littafin dake d'auke da kala-kalan abincin da aka mik'o masa ya girgiza kai tare d'an murmushi yace "Um-um! Nagode da wannan ma."

Kyab'e fuska *Sharhasila* ta yi kamar za ta yi kuka tce "Haba dai Yallab'ai, ka zab'a mana, ni fa zan biya."

D'an sunkuyar da kai ya yi kamar mai tunani sai kuma ya d'ago ya sake girgiza kai yace "Ya isa haka Baby, kin san bana son zuwa irin wuraren nan cin abinci, hasalima ni na fi jin dad'in cin abincin gida."

Had'e fuska tayi tare da kawar da kai sam abinda ya fad'a bai mata ba, to ita ina za ta iya wani girki? Tabb'! Kallonshi tayi tace "Yallab'ai, amma dai ka san ba ni zan dinga girki ba idan mun yi aure ko?"

Da mamaki Huzeifa ya kalleta yace "Ban gane ba? To wa zai yi? Ni?"

D'an murmushi ta yi cike da shashanci tace "A'a haba, ina nufin sai mu samu yar aiki."

Iska ya feso a bakinshi yana jin wani b'acin rai na hauhawa masa, to shi bai san wane irin aure ne za su yi da Sharhasila ba, dan tana tak'amar ita yar mai kud'i ce, kuma ita ta nunashi ta ce tana so, sai ya zama zai zaunata mulkeshi ne? Abubuwa na hauka da kidahumanci ta ke kawo masa fa, wannan wane irin abu ne?

Kallon kyakyawar fuskarta ya yi wacce ta fad'a masa wuni ta yi wajen gyaran jiki da kwalliya wai dan za su had'u wurin cin abincin nan kawai wanda shi a wajenshi bai da wani anfani, cikin tausasa murya yace "To me yasa ke ba za ki dafa ba?"

Turo baki ta yi irin shagwab'ar nan cikin harshen faransanci tace "Amma Bebe ai kasan ni aiki nake zuwa ko? Yaushe zan maka girki sannan na yi aikina? Ba zan iya ba gaskiya."

Shi ma a harshen faransancin yace "To ai macece ke, kuma ba'a yi auren ba, zaunawa za ki yi

kafin lokacin ki tsarawa kan ki rayuwarki, kar ki maida hankali kan abinda ba zai anfani lahirarki ba, Sharhasila wannan aiki da kike moriyarki da shi iya duniya ne kawai, idan ki ka fi k'arfin shed'an ne za ki nemi lahirarki da aikin, dan haka a ganina tun ba'a d'aura aurenmu ba ki tsarawa kanki komai ta yanda za ki ba wa komai lokacinshi yanda ya kamata."

K'ank'ance ido yayi sosai ya na ci gaba da kallonta yace" Kin san wani abu? Mutum ne ni mai matuk'ar son kulawa, hakan yasa mahaifiyata ke fad'a min wai wasu lokuta kishi nake da k'annaina..."

Yar dariya ya yi ya d'ora da" Gaskiya ne, sai na ji idan ina magana da ita bana so kowa ya mana kutse bare a tilasta mata raba hankalinta gida biyu, sannan ina da matuk'ar son abincin gida, ma'ana ina son abinci irin su tuwo, d'an wake, faten doya, biski, dambu...da sauransu."

Tsareta ya yi da ido yace" Da fatan dai duk kin iya wannan? Idan ma ba ki iya ba ina fata za ki koya saboda ni."

Tunda ya fara magana ta zuba masa ido ta na kallo, dogon bayanin nan da ya zauna ya na mata sai ta ji kanta ma ya fara ciwo, to ita kam ta rasa hadisi na nawa ya karanta mata, a gaskiya ba ta ma gama fahimtar zancen shi ba, dan haka ta na buk'atar k'arin bayani.

D'an gyara zama ta yi tana kallonshi tace "Bebe ban gane ba, ka min dalla-dalla mana, ka na nufin ni ma sai na koyi iya tuk'a tuwo kenan?"

Murmushi ya mata yace "B za ki iya ba kenan?"

Kawar da kai ta yi tana nazari na wasu dakik'u, a gaskiya duk yanda take so da k'aunarshi ba za ta iya wannan wahalar ba, amma kuma sanin waye Huzeifa ya sa ta d'an yi wata shawarar, tunda dama ba shi ya fara cewa ya na son ta ba, ita ce ta ji ta na k'aunarshi saboda kyawawan halayenshi har ta masa tayin soyayyarta, da fari kam ya nuna baya ra'ayi saboda kasancewarta 'yar mai kud'in unguwarsu, amma da ta dage ya kuma shawarci mahaifiyarshi sai ya amince har yanzu suke shirin zama mata da miji nan da kwanakin da ba zasu gaza goma sha biyar ba. Dan haka ta kalleshi da murmushi a fuskarta tace "Bebe, ai kasan soyayya ta sa na ce ina sonka, dan haka ba abinda ba zan iya yi maka ba."

Fad'ad'a Murmushin shi ya yi yace "Nagode sosai, ai na d'auka ba za ki yi ba."

Da irin zolaya tace "Ni na isa? Idan fa ka fasa aurena?"

Dariya ya yi cikin tattausar muryarshi yace "Ba zan fasa aurenki ba, sai dai na miki kishiya bayan auren."

Zaro ido ta yi ta dafe k'irjinta cike da tashin hankalin da ya ziyarceta lokaci d'aya tace "Bebe, dan Allah ka daina min irin wasar nan bana so..."

Tsal! Ta taso daga kan kujerarta ta dawo kusa da shi sai dai dake babu wata kujerar sai ta durk'usa k'asa ta rik'o hannunshi, da sauri ya d'an jaye hannunshi saboda gudun matsala, dan baya son ya sake shiga halin da ya shiga d'azu daga kallon wata.

Sake rik'o hannun na shi tayi ta rik'e gam tana kallon idonshi da na ta idon da sukayi jajir suka tara ruwa alamar kuka, cikin rikitacciyar murya ta dinga mitsika hannunshi ta na fad'in "Ka na ji ko Bébé ? Dan Allah ka daina irin haka bana so, ka ga ba zan iya kishi da wata a kan ka ba, dan Allah ka min alk'awarin ba za ka tab'a min kishiya ba?"

Da mad'aukakin mamaki ya kalleta sosai ya na nazartarta, daga bisani numfashi ya sauke yana ci gaba da kallonta yace" Tashi ki zauna, kina ga fa kallonmu a ke."

"Ni ban damu ba su kallemu, ka min alk'awari ka ji mijina." Ta fad'a da alamar fashewa da kuka, jinjina kai ya yi yasake nuna mata wurin zaman da d'aya hannunshi yace "Dan Allah ki zauna sai mu yi magana."

Da sauri ta mik'e ta zauna ka kujerar ta zuba mi shi ido ta na kallo kamar wanda take son gano ta inda yake fitar da numfashi. A hankali Huzeifa ya d'an girgiza mata kai cikin sanyayyar muryar da hakan d'abi'arsa ce yace mata" Ba zan iya miki wannan alk'awarin ba *Sharha*, saboda ni d'an adam ne ban san me Allah ya tsara min a gaba ba."

Jin hakan daga bakinshi ya sa ta fashewa da kuka da iya gaskiyarta kawai ta kifa kanta a kan teburin, cike da damuwa da jin tana muzantashi cikin mutane ya k'ara tausasa murya yace" Dan Allah Sharha ki daina kukan nan, kin ga tashi mu bar nan in dai kuka za ki min."

Kamar ba ta san ya na yi ba haka ta dakeshi, mik'ewa ya yi ya sake maimaita" Tashi mu je na ce."

Nan ma shirun ta masa, ranshi ne ya d'an fara b'aci dan haka ya zagaya kusanta ya d'auki jakarta da wayarta da makullai dake aje, bai tsaya jiran komai ba ya finciki hannunta suka fita a wajen dan shi fa duk taushinshi mutum ne kuma da baya son iskanci, sam ba zai lamunci ta mayar da shi wani lusari ba dan baya da kud'i sannan *mad'inki ne* shi, haka kawai ba za'a raina masa wayo ba, ta ya ma zai mata wannan alk'awarin? Ta san me alk'awari yake nufi a shari'ance? Ta san me zai faru da shi idan Allah bai nufeshi da cikawa ba? Ba ma duk wannan ba shi fa gaskiya *mace mai addini* ya ke da burin samu, hakan yasa ya ke tunanin ko ya aureta idan bai sameta yanda ya ke buk'ata ba to indai ya samu halin k'ara aure to zai k'ara, sai kuma ta nemi katse masa hanzarinsa da wani tunaninta irin na hayudawa haka kawai.

Tuk'i kawai yake a motar ta ya na kallonta jefi-jefi, yanda ta d'aga hankalinta akan tashin d'aukar mata alk'awarin nan da irin kukan da ta yi, a ganinshi ko iyayenta aka ce sun rasu iya hakan ne kawai za ta yi, idonta sun yi jajir sosai sun kumbura abu ga jar fatar da ba ta saba da hayaniya ba. Ajiyar zuciya ya sauke yana kallon gabanshi yace "Ki yi shiru Bebe, kukanki fa ya na tab'a

min zuciyata sosai."

"To idan ka hakane ka min alk'awarin mana." Ta fad'a kamar za ta matso daf da shi ta sumbace shi, d'an tab'e baki kawai ya ui ya girgiza kai bai ce mata komai ba, cikin tausa murya tace "Bebe me ye a ciki ne wai? Alk'awari fa kawai za ka d'auka da fatar baki."

Wata nauyayyar ajiyar zuciyar ya sake saukewa yace "Sharhasila hadisin Anas d'an Malik fa ya ji daga bakin Manzon Allah (S. A. W) ya ce" Alamomin munafiki guda uku ne, idan zai yi magana sai ya yi k'arya, idan ya yi alk'awari ya sab'a, idan aka amince mi shi ya ci amana..."

Kallonta yayi fuskarshi d'auke da damuwa sosai yace" Duka wannan alamomin za su tabbata a kaina idan na miki abinda kike so yanzu, na farko idan na fad'a miki ni na san k'arya na miki har cikin raina, idan kuma ban cika alk'awarin ba kin ga na sab'a, sannan na ci amanar yardar da kika min, to me ye ribar hakan? Me zai sa na jefa kaina a wannan halakar ? Alk'awari d'aya da zan iya yi miki shine, ko bayan aurenmu zan zama mai mi yi miki uzuri, sannan ko da Allah ya jarabceni da k'ara aure, to zan ci gaba da kare martaba da kimarki a idon d'ayar, ba zan tab'a bari ki zubar da hawaye ta dalilina ba kuma da sanina, sai dai abisa rashin sani, wannan alk'awarina ne gareki."

Wata arniyar harara ta maka masa ta gefen ido dan ita sam abinda ya fad'a ta kunnen da ya fi kusa da shi ya shiga ko d'ya kunnen bai kai ba ya fita abunshi, ya zai tsareta da wasu zantukanshi na daban kawai da wasu tatsuniyoyi? Ba ta ce mishi k'ala ba har suka isa k'ofar gidansu.

Fita duk sukayi inda ta zauna mazaunin dreba shi kuma ya kalleta yace "Ni zan idasa gida a k'afa, sai da safe."

A shagwab'e tace "Ba za ka kirani ba?"

Shafa sumar kanshi ya yi yace "E to...kin san fa jibi za mu fara jarabawarmu (BAC) karatu yayi zafi sosai, amma dai zan kok'arta na kiraki."

Turo d'an k'aramin bakinta ta yi tace "Tom, sai na ji ka."

Da haka suka rabu ita ma ta shige k'aton gidansu kowa da abinda yake ta sak'awa da warwarewa a zuciyarshi, inda Huzeifa ya fi maida hankali kan irin zaman da zaiyi da yarinyar da take ganin mahaifinta mai kud'i ne, shi kuma d'an ladanin da ya rasu ya barshi da nauyin k'annanshi da mahaifiyarsu wanda ya ke ciyar da su ta hanyar d'inkin da yake d'an samu idan ba ya karatu, yarinyar da aka ma hanya duk da takardunta ba su kai ba amma take aiki a babban reshen kamfanin shiga da fitar kud'i na *Al'izza*, shi kuma yanzu ne ma yake karatun, dan ko ya samu jarabawar nan yana da burin ci gaba da karatunshi.

*Ku yi hak'uri da rashin ganin update jiya, hakan ya faru ne sakamakon wasu uzurirrika.*

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_8_

Kiran da aka mana cewa mu zo mu ci abinci ya sa Saleema fitowa daga ɗakin bayan idar da sallah isha'i, rufe ƙofar ɗakin ta yi ta fara takawa a hankali, cikin nutsuwa ta ke saukowa daga matakalar benen har ta sauko ƙasa, za ta nufi teburin cin abincin da ta hangi mutanen gidan ta

dan tsaya saboda jerawa da sukayi da Mu'az shi ma zai nufi teburin.

Ɗan satar kallonshi ta yi ta gefen ido ta taɓe baki, Mu'az dake kallonta ya na so ya san wacece wannan? Cikin shan-ƙamshi da tsareta da ido yace "Sannu."

Kallonshi ta yi sosai, haɗaɗɗen saurayi mai ilimin boko da wayewa irin ta zamani, sa kawai ta ɗan ɗaga masa kai alamar "Kai ma sannu."

Da mamakin yanda ta amsa mi shi ya bita da kallo sanda take ƙarasawa wajen teburin, tana isa ta dan dakata tare da faɗin"Ina wuninku."

Alhaji Auwal ne ya fara amsawa da fara'a yace" Lafiya lau ma puce, kin sauko?"

Cike da kunyar sunan da ya kirata da shi ta ɗan jinjina kai sannan ta ja kujerar da Hajia babba ta nuna mata ta zauna. Dara-daran idonta ta ɗaga ta kalli Mu'az da shi ma ya ja kujerar da ke fuskantarta ya zauna ya na binta da ido kamar maye, ɗauke kai ta yi tana ɗan gunguni ciki-ciki.

Ummeeta ta kalla da suke maƙale da juna ita da Hadeeya tace "Sannu Ummee."

Yatsina fuska Ummee ta yi tace "Sannu."

"Abba ita ma wannan ƴar tonton ce?"

A sanyaye sosai ta maida dubanga zuwa ga wanda ya yi maganar, wato ɗaya sheɗanin ne ba? Mu'awwaz ko? Haɗa ido su ka yi hakan yasa ta yi saurin ɗauke kanta, Alhaji Auwal da ke murmushi ne yace "Wai ba ka ganeta ba abokina? Mai sunan Hajia ce fa."

Waro ido sosai Mu'awwaz ya yi yana kallon Saleema yace "Abba Saleema fa? Ita ce ta koma haka?"

Wani mugun kallo ta aika masa cike da takaicin rashin sako hijab ɗinta da ba ta yi ba, hakan kuma ya faru ne da tunanin doguwar riga ce jikinta kuma ban da samari ake cin abincin, murguɗa masa baki tayi duba da shi kan shi fa shekara biyu zuwa uku ne ya bata, amma abu ga ɗan hutu ya zama wani karbcece masha Allah, ka rantse ba su yi wasar ƙasa tare ba.

Hajia babba ma dake murmushi cike da dattako tace "Girman mace ai ba wuya, kai ma da ke namiji ba gashi ka haɗemu wajen tsayi ba."

Mu'az da ke ta kallonta yana taunar leɓe ne yace "Gaskiya kam, gashi ta girma...sosai."

Da sauri Saleema ta kalleshi, amma sai ya dinga aiko mata da wani kallo irin na iskanci a ganinta yana kashe mata ido ɗaya, ɗan cire takalminshi ya yi daga ƙafa ya zuro ƙafar ta ƙasan teburin ya zunguri ƙafarta, da sauri ta jaye ƙafar ta na waro ido ta kalleshi sosai, sake kashe

mata ido ya yi hakan ya hassalata ta wurga masa harara.

Hajia ƙarama da ta miƙo masa abinci amma bai kula ba ne tace "Mu'az."

Da sauri ya kalleta sai kuma ya girgiza kai yace "Um um! Zan sha kayan marmarin nan kawai, kun san sun fi..."

Sai kuma ya kalli Saleema yana ɗaukar tuffa dake kusanshi sannan yace "Sun fi dadɗi da ƙara lafiya ko ya ki ka ce mai sunan tsofaffi?"

Buɗe ɗan bakinta tayi kamar za ta yi magana, sai kuma ta yi shiru dan bata san me yake nufi da abinda ya faɗa ba. Hadeeya da kujerarta ke kusa da ta shi a ɓangaren ce ta kalleshi tace "Yaya ka ci abinci fa, wannan ba zai riƙeka ba."

Kallonta yayi da fara'a a fuskarshi yace "Hadeeya ko?" Jinjina kai tayi alamar e tare da sakin murmushi, hannu ya miƙa mata alamar su gaisa yana faɗin "Kina lafiya?"

Ba tare da tunanin komai ba ta miƙa masa hannun suka gaisa, hannayen na su Saleema ta kalla sai kuma ta kalli Hadeeya, girgiza kai ta yi ta sunkuyar da kanta ta fara wasa da cokalin hannunta, babban abun takaici shine yanda ya yi haka a gaban iyayenshi amma ba wanda ya nuna ya damu.

Muryar Alhaji Auwal ce ta saka ta ɗaga kanta sanda yake faɗin "Mu'awwaz idan kun kamala ka tafi da su alimentation idan akwai abunda suke da buƙata sai ku siyo."

Jinjina kai Mu'awwaz yayi yace "To Abba."

"Ka barshi ma ni zan kaisu." Cewar Mu'az yana ci gaba da kallon Saleema, bai san me yake ji ba a kanta ba, sai dai ya ji yana sha'awar komai na jikinta, duk da ba kyawun fuska ne da ita ba na nunawa a jarida, ba kuma jar fata gareta ba kamar ƴan uwanta, amma dai komai na ta ya birgeshi musamman da ya fahimci ya fi sauran ƴan uwan na ta nutsuwa da kamun kai.

Wani kallo Mu'awwaz ya masa dake nuni da bai ji daɗin abinda Yayan na shi ya masa ba, wannan ai katse hanzari ne, ya na tunanin ya fita da ƴan mata su shanawarsu, musamman ma Hameeda da ta fi ɗaukar hankalinshi, sai kawai ya ce shi zai kaisu? Wallahi ba dan ya na tsoron ya yi magana ya kabta masa mari ba, da ya masa magana sai dai a yi duk wacce za'a yi. Da harara ya bi Mu'az ɗin da ya miƙe yana faɗin "Ummee ina jiranku a waje."

Saida ya ƙara matsowa kusan Saleema ya ɗora hannayenshi a kan teburin ya sunkuyo sosai kamar zai sumbaceta, jaye fuskarta tayi daga kallonshi tana yatsina fuska cike da kunya, duka mutanen kallonsu suke, su Hadeeya mamakin yanda ya ke ma Saleemar su ke, ko bai gane ita ɗin ba mai aji ba ce? Yayin da amarya ta ke taɓe baki da tunanin "Ɗan iska kawai, a gaban mutane ma sai ya nuna halin iskancin da tambaɗewa."

Hajia babba kuma murmushi take a ran ta tana ayyana "In har Saleema za ta zama alkairi gareka zan fi kowa farin ciki." Dan kuwa ta fi kowa sanin ɗanta, ba ta taɓa ganin ya wa mace haka ba, shi Alhaji Auwal kuma murmushi kawai ya ke saki a fuskarshi, ko ba komai ƴaƴan Alhaji Yusuf za su ji daɗin zama gidan.

Cikin sanyin murya Mu'az yace mata" Ina jiranki, ki fito da wuri."

Juyawa ya yi kawai ya fice a falon, kasa ɗaga kanta tayi bare ta kalli mutanen wurin, sai da ta ji sun maida hankulansu kan abincin sannan ta ɗan ɗago ta kalli Alhaji Auwal, cikin taushin murya da ladabi tace" Am! Abba."

Cike da kulawa ya kalleta yace" Na'am ƴata."

A sanyaye tace" Ina ganin su tafi kawai, ni zan zauna a gida."

Da mamaki a fuskarshi yace" Me yasa? Ke ba kya buƙatar komai ne?"

Ɗaga kai tayi alamar e, wata harara Hadeeya ta jefo mata cike da takaicin me yasa wau ita take da kidahumanci ne? Kuɗi ne fa za'a kashe musu, ɗauke kai ta yi cike da baƙin ciki, Saleema kuma da ta kula da kallon ba ta biyata ba bare ta samu damar faɗa mata wata maganar marar daɗi.

Hameeda a da saida ta harari Saleema cike da rashin kunya tace "Abba ka ƙyaleta ita dama haka take, mu za mu je mu siyo abinda mu ke so."

Kallon Hameeda ya yi da mamakin yanda ta ke magana akan Yayarta haka, shi fa duk bokonshi da iskancinshi ya na so ya ga ƙarami na girmama babba, girman da ubansu ya ke bashi ne matsayinshi na wanda ke sama da shi a komai ya sa suke kamar abokai, ko Mu'awwaz da ke namiji bai yarda ya raina Mu'az ba tunda ya na gaba da shi, bare ita wannan da ba ita ke bi ma Saleema ba. Ɗauke kai kawai ya yi da tunanin idan ya ƙara ganin haka zai tsawatar mata, dan sam ba ya lamuntar irin haka.

Shigowar wata matashiyar yarinya da ba za ta wyce tsarar Hameeda ba yasa Saleema kallon ƙofar, Alhaji Auwal ma cike da kulawa ya kalleta yace "Kin kai musu abincinsu?"

A ladabce yarinyar da sai yanzu Saleema ta fahimci ƴar aiki ce tace "E Alhaji na kai musu, sun tafi masallaci ma sai da na jirasu."

Jinjina kai ya yi yace "To da kyau, kin gama aikin ki ne yanzu?"

Cikin ladabi tana ta rarraba ido tsakanin Alhaji Auwal ɗin da kuma amaryar sa da ke binta da kallon ƙyama a ɗan tsorace ta amsa da "E na idar."

"Shikenan za ki iya tafiya." Ya faɗa yana ci gaba da cin abincin shi, tsaf Saleema ta kula da inda yarinyar ta kalla a matuƙar tsorace, a hankali ta ɗan ƙyallara idonta ta kalli inda idon yarinyar ke kallo. Karaf! Idonta suka sauka kan Mu'awwaz da ke ta ma yarinyar signa da ido, da sauri Saleema ta sake kallon yarinyar ta ga ta juya ta fita, taɓe baki kawai ta yi da tunanin wannan shi ne abinda Mamanta ta faɗa cewa Mu'awwaz ya cika tsantseni, wato shigar da ke jikin yarinyar ya ke ƙyamata? A karo na biyu sake taɓe baki ta yi ta ɗauki cokalinta za ta ci gaba da cin abinci, Mu'awwaz ta ga ya miƙe ya na faɗin "Na ƙoshi."

Kallonshi amarya tayi tace "Bebe, ba ki ci sosai ba fa?"

Ba tare da ya ko kalleta ba ya kama hanyar fita ya na ɗaukar tuffa ɗaya yace "Ya isheni."

Da kallo Saleema ta bishi mamaki ya lulluɓe na tunanin wai su mutanen nan ba sa jin kunyar kiran kowa Bebe ne? Haka matar Babansu ma take kiran ubansu Bebe, sai ka ce wani ɗan goye.

Su Hadeeya ma miƙewa sukayi suka ce "Mu je mu shirya kar mu tsayar da Yaya."

Su uku ne suka nufi ɗakin su dan shiryawa, Saleema kuma da ta kalli Alhaji Auwal ne tace "Abba, ya na ga yanzu gidan babu yara?"

Murmushi ya yi ya saki kallon amarya yace "To ai yaran da kika sani su ne suka girma yanzu, ga Mu'awwaz nan kin gani ya zama saurayi, ga Ummee, Safwan ne kawai kuma ya na ƙasar waje karatu."

Jinjina kai tayi kawai ta ɗan tsakurar abincin ta na jin duk ba daɗi sai ita kaɗai yanzu a cikin iyayen, fitowar su Hameeda yasa ta juya dan ganin da wace shigar aka fito?

" A'uzubillah!" Ta fara ambata a ranta, dan kuwa a cikin shigar ta Hameeda ce kaɗai ta ga da ɗan dama-dama, saboda ita ce ta sa doguwar riga irin na material ɗin da ake ɗingawa da ɗan-kwalinta, ɗinkin ya bi jikinta yanda ya fito mata da surarta, kallabin kuma ta ɗorashi a kan ne kawai amma ba ta ɗaure ba. Amma shigar Ummee abun ya munana sosai, dan riga da wando ne da suka kamata, wandon ma irin wanda ya ɗan ɗage mata bai sauka ba sosai, sai takalma dake ƙafarta ƙafa ciki, kanta kuma wata ƴar yaloluwar hula ce ta ɗora sai gashinta na doki da ya bayyana.

Ajiyar zuciya ta sauke ta kalli fuskokin iyayen, dukansu fara'a ce a fuskarsu har da tagomashin faɗa musu "Sai kun dawo."

Da gudu Hamdeeya ta tashi ta bi bayansu tana faɗin "Ni ma zan je."

Dariya Alhaji Auwal ya ƙyalƙyale da ita yace "Tafi a hankali to kar ki faɗi."

Suna fita ya ɗauki wayarshi ya turawa Mu'az saƙo cewa ya karɓi makullin morarshi hannun dreba akwai kuɗi ciki sai su tafi.

Saleema da har yanzu ta kasa daina kallonsu da mamaki ne yasa ta ɗan numfasa, a ladabce sosai cikin nutsuwa bayan ta aje cokalin hannunta tace "...

*Ku yi haƙuri da wannan.*

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_9_

A ladabce sosai cikin nutsuwa bayan ta aje cokalin hannunta tace "Abba, ku yi haƙuri dan Allah idan abinda zan faɗa zai ɓata muku rai..."

Da hannunta ta ɗanyi alama tace "Sai na ga kamar ba ku damu da yanda su ka fita ba kamar dai yanda yanke faruwa a gidanmu, Abba a ganinku haka dai-dai garesu a matsayinsu na ƴaƴa mata? Ina ganin kamar rufin asirinku da na su shine ku tayasu kare mutumcinsu..."

Ganin duk sun ƙura mata kamar mamakinta suke ko kuma dai wani abun sai ta tsagaita, ɗan sake kallonsu tayi cike da kunya musamman ma amarya da ta ga kamar ta na mata kallon jin haushi, sunkuyar da kanta tayi ƙasa tace" Ina ƙara baku haƙuri, na yi aiki da faɗar Manzon Allah (S. A. W) ne, ya koya mana hani ga mummunan aiki idan ka na da iko, sannan ya faɗa mana idan za ka iya ka hana da hannayenka, idan ba zaka iya ba da harshenka, idan ba zaka iya ba ya ce to da zuciyarka, ma'ana ka ƙyamaci abun a zuciyarka, shiyasa na mu ku magana amma ban yi da raini ko ɓata muku ba."

Mamar Ummee da take ganin kamar da ƴarta Ummee ne take, dan ita bata ga aibun shigar su Hadeeya ba ma sam, cikin fushin da ta kasa ɓoyewa ta kalli Saleema tace" Kinga ƴan mata ki yi abinda ya shafeki, bana son mutum mai shiga sabgar da babu ruwansa, ina aibun shigarsu a nan? Yaranki ne mu da za ki zaunar da mu kina mana wannan maganganun? Oho! Idan na fahimceki so ki ke ki ce mu ɗin ba mu san abinda ya dace ba sai ke."

Dogon tsaki ta ja ta miƙe tsaye tana ɗaukar wayarta ta juya ta bar wurin, da kallo Alhaji Auwal ya bita kafin ya maido kallonshi kan Saleema da ba ta ji dadɗi ba tace" Abba dan Allah ka bata haƙuri, ita dama gaskiya ɗaci ne da ita, mafi alkairin mutane kuma shi ne wanda za'a faɗa ma gaskiya ya ɗauka har ya yi anfani da ita."

Ajiyar zuciya ta sauke jiki a sanyaye ta miƙe tsaye ta kallesu tace" A ci lafiya."

Juyawa ta yi za ta fita a falon Hajia Rabi tace" Ina kuma za ki je?"

Juyowa tayi da fara'a tace" Zan fita waje ne."

Jinjina kai Alhaji Auwal ya yi yace" To, amma ki kula da kanki."

Ƴar dariya tayi tace" Ba ƙofar gida zan fita ba, iya farfajiya ne kawai."

A tare suka jinjina kai cike da jin ƙaunar yarinyar, in har suka ƙi abinda ta faɗa to ba su da wata hujja ta ƙin ta, sannan ba ita su ka ƙi ba sai gaskiyar da ta faɗa, dan haka ma suka ji ta birgesu duk da su ma ba su ga aibun shigar ta su ba sai yanzu ne da ta faɗa hotunan shigarsu ke dawo

musu a kai, musamman ma ta Ummee da ta fi munana.

*Ta na* fita a hankali ta shiga ɗan zagayawa ta na jin ina ma tana da waya da ta kira Mamanta, amma sai ta yanke shawarar idan Hadeeya ta dawo za ta karɓi ta ta sai ta kira dan su gaisa, saida ta kai ƙarshen katangar da a saninta nan ɗin bayan gida ne sai ta dakata saboda akwai duhu wurin, juyawa ta yi da nufin ƙarasawa wajen motoci da ta ga akwai haske ta ko ina. Sai dai kamar gizo kunnuwanta su ke jiyo mata abun da ya kayar mata da gaba duk da ba ta san me ye ba? Amma dai ta shiga zulumi da ɗumbin mamakin wa ye haka? Me kuma ya same shi da yake irin haka? Alhalin daga ji muryar ƙosasshen namiji ne.

Cikin sanɗa ta ɗan fara leƙa kanta, ba ta ga komai ba sai dai ta ɗan ƙara jin sautin kusa da ita, tako ta yi da bai wuce uku zuwa huɗu ba ta sake leƙawa dan a tsorace take. Da bala'in sauri ta rufe bakinta da tafin hannunta na hagu ta saki siririn numfashin da ya fitar da sauti kamar wacce ta sha yaji, gaba ɗaya ta ƙwalalo idonta tsabar kaɗuwar da ta yi na ganin wannan lamari, take jikinta ya ɗauki rawa tamkar mazari, da mugun gudu zuciyarta ta shiga bugawa, dan a rayuwarta ba ta taɓa mummunan gani irin wannan ba na yau.

Tabbas ba ta tsiraicinsu ba saboda duhun da ke mamaye a wurin, sai dai hasken wata wanda dama ɗaya ne a cikin dalilin da ya sa ubangiji ya saka mana shi dan ya haska mana abunda ya shigarana duhu a yanar idonmu, ta hakane ta gane su waye a wurin da kuma abinda suke aikatawa. Riskar yanayin da bai taɓa samu ba yasa su kansu suka tsorata sosai, yarinyar durƙushewa ta yi ita kanta jikinta ya ɗauki ɓari, inda shi ma ya shiga kiciniyar saka wandonshi, jikinta na makyarkyata ta juya da sauri sosai ta tunkari komawa inda ta fito, tana jin ya biyota yana kiran "Sssaleema, Saleema dan Allah... Saleema dan Allah tsaya ki saurare ni, na roƙeki S..."

Shigewar da ta yi falon da sauri ya sa dole ya ja birki ya tsaya ya na hangenta, ganin ta nufi sama alamar masaukinsu za ta shiga ya sa ya daki iska yana buga ƙafarshi da mugun haushi ya furta" Shiiiit!"

Dafe kanshi ya yi ɗaya hannun kuma ya riƙe ƙugu ya na safa da marwa a ƙofar ɗakin ya rasa me zai yi, juyowar da zaiyi yarinyar ta taho har yanzu jikinta ɓari yake duk ta rufe fuskarta da tsohon hijabinta alamar kuka take, saida ta zo kusa da shi ta durƙusa cikin kuka tace "Dan Allah na roƙeka ka ƴantani hakanan, na gaji da wannan rayuwar, yanzu haka ni da mhaifiyata da ƴan uwana muna samun abun da za mu ci dai-dai gwargwado."

A rikice Mu'awwaz ya zuba hannayenshi biyu cikin aljihu ya lalaba ya ciro kuɗi, miƙo mata yayi cikin tashin hankali yace" Karɓi, daga yau kar na sake ganinki gidan nan, ki tafi kar ki sake zuwa."

A razane ta ɗago ta kalleshi sannan ta kalli kuɗin, a ƙalla za ta iya jan jari da su, da haka za ta tsira daga sharrinshi, karɓa ta yi ta miƙe tana faɗin" Nagode."

Juyawa ta yi za ta fice sai kuma ya canza shawara, da gudu ya tari gabanta yana faɗin" Kin ga! Gobe ma ki dawo, saboda nasan halin Abba da sa ido a kan komai, idan ya ji ba ki zo ba zai sa a bincika masa, ni kuma ina tsoron kar yarinyar can ta faɗa masa abinda ta gani."

Ƙasa ta yi da kanta alamar hukuncin nan bai mata ba, ita kam da ya barta ta tafiyarta shikenan, amma ita kanta kunya ba za ta barta ta zo gobe ba, cikin taushin murya ya sake faɗin" Dan Allah ki zo gobe kin ji, bana so Abba ya yi zargin wani abu aka miki."

Kallonshi ta sake yi irin kallon nan na da ke nuni ko dai wani abun za ka sake min? Kamar ya fahimci kallon kuwa sai yace" Na rantse miki da Allah ba abinda zan miki, wallahi haka ba za ta sake faruwa ba."

Fuska a gintse ta ɗaga kai alamar to, sannan ta raɓashi ta wuce ta bar gidan tana kuka na takaicin yanda ta rasa mutumcinta dan kawai ta ciyar da ahalinta, yanzu gashi dalilin haka ba ta san me zai faru ba a gaba.

*10:46* su Hadeeya suka dawo gidan, har sun fito daga motar Mu'az ya bi Hadeeya da wani kallo yace "Ƙanwata zo ki ji."

Juyowa tayi ta na sakar masa fari da ido ta dawo ta zauna, ganin bata rufe ƙofar ba yasa shi zura hannu ta gabanta kamar wanda zai taɓa mata ƙirji ya rufe ƙofar yana kallonta yace "Sirri za mu yi."

Murmushi tayi ta sassauta murya tace "To Yayana ina jin ka."

Daf da ita ya matso sosai ya na wani kashe mata ido yace "Ki na da saurayi?"

Ɗan jim ta yi kafin ta kalleshi ta na ɗan lumshe idonta saboda kusancin ya yi yawa sosai tace "Ina da, amma..."

"Amma me? Kina nufin ki ce Yayan na ki ba zai samu shiga ba?" Yanda ya yi maganar ya na kamo hannunta yana matsawa ya sa ta kasa cewa komai sai rarraba ido take, sake matsowa ya yi har numfashinsu ya fara gyauraya sannan yace "Uhumm! Ina jin ki."

Dake hakan bai taɓa faruwa da ita ba, duk yanda take samun kusanci da namiji ba ya wuce ƴar gaisuwa da hannu ko dafa kafaɗar juna da dai irin haka, kaa cew komai ta yi, hakan yasa shi sake faɗin " *Deeya*."

A hankali ta ɗan ɗago kanta da niyyar saka idonta cikin na shi ta faɗa masa wacece za ta ƙi namiji kamar shi? Sai dai kafin ta gama ɗagowar ya yi wuf da bakinta ya sumbata.

Ɗuf! Hadeeya ta yi dan yau ta gamu da gamonta, zazzaro ido ta yi a tsorace sai dai ba ta yi yunƙurin dakatar da shi ba, a hankali ya raba bakinshi da na ta yana kallon yanayin da ya jefata alamar dai sabon shiga ce, sake kashe mata jiki yayi da faɗin "Ki na sona Deeya?"

Yanda ta yi kiskirim ta kasa motsawa ya sa shi sakin murmushi yace "Haba dai babbar yarinya, ya ki ke abu kamar ba ki waye ba, kar ki badani mana."

Ƴar dariya yayi mai sauti ya jawo kanta gaba-ɗaya ya manna a ƙirjinshi yana shafa kanta yace "Shikenan to ƙanwata, yanzu ki shiga ciki gobe da safe sai ki faɗa min shawarar da ki ka yanke."

Ɗagata ya yi daga jikinshi ya buɗe mata ƙofar, jiki a mace ta fita kamar wacce aka ma dukan tsiya, saida ya ga shigewarta ya jawo ƙofar ya rufe yana wani munafikin murmushi ta gefen laɓɓa yana ayyana" Na san ma za ki amince, wannan tarkon ya fi ƙarfin tsallakewarki, da sannu zan samu sabuwar babyn da za ta dinga ɗebe min kewa."

Dantse leɓɓenshi yayi yana jinjina kai sannan ya ja motar ya bar gidan, dan yau kam ba ya jin a zai kwana a gidan, duk da ba mata yake nema ba, shi dai barshi da ƴan wasannin nan da mace, dan a zaman da ya yi ƙasar waje ya koyi hakan, dan mutum ne mai ƙyamar hakan kasancewarshi likitan da ya karanci mecece mace? Yana matuƙar jin ƙyamar shiga hurumin da ba na shi ba, amma Hadeeya ya ga yarinya ce ɗanya shakaf, dan haka zai yi ƙoƙarin yi mata wayo ya fara buɗe hanyar da kan shi kafin ya gama tantancewa ya samo matar da ta dace da tsari da zubin yanayinshi da kuma tunaninshi. Duk da ya ga Ƴaƴar su Hadeeya ta ɗazu (Saleema) ta na da irin ƙirar da yake so, wato kakkauran jiki da kuma manyan mazaunai har ma da ƙirji, ama zai fara tabbatarwa kanshi wani bai fara kai ko da hannunshi a kan kayan ba kafin ya sallama mata.

*Saida* tatabbatar su Hadeeya sun yi bacci sannan ta miƙe daga kwancin da ta yi tana ta hango abunda idonta suka gane mata, ita a zahiri dai ba ta taɓa ganin kusancin mace da namiji fiye da haka ba bayan na matar Babansu da shi Baban na su sai yau, ƙiri-ƙiri Allah ya nuna mata Mu'awwaz da yarinyar da ba ta gama sanin me ye aikinta ba a gidan yana saduwa da ita a tsaye, a tsayen ma a jikin bango bayan ba matarsa ba ce. Alwala ta ɗauro ta zo ta kabarta sallah kamar yanda ta wa mamanta alƙawarin za ta ci gaba da addu'a dan Allah ya bata nasara a kan jarabawar da sukayi, sau biyu kenan ta na rasa wannan jarabawar, idan ta sake faɗuwa yanzu Hadeeya kuma ta yi nasara ba ta san me Abbanta zai mata ba.

Ƙarfe 02:30 na dare ta samu ta canza kayanta ta saka riga da wando na bacci sakakki sannan ta nufi inda Hameeda take dan gadon ɗaya Hadeeya ce da Ummee, ta kwanta kenan za ta ɗan ja bargo saboda sanyin acn ɗakin kawai ta ji an murɗa ƙofar alamar za'a shigo.

Zazzaro ido tayi mugun tsoro ya kamata da tunanin wa ye a wannan daren? Me ya zo ɗakin ƴan matan a wannan lokacin? Kurawa ƙofar ido ta yi saida ta ga an buɗo da gaske dai ana shigowa ta matsa da sauri ta haɗe a jikin bayan gadon ta kai hannu ta ɗan zungurar Hameeda dan ta

tashi. Dake da kanta ta kashe wutar ɗakin sai mai ƙaramin haske, hakan yasa ya na shigowa suka haɗa ido, ai zabura ta yi tana neman durkowa a gadon tana faɗin "Kkk... Kai kuma? Malam..."

"Shiiiiiiii!" Ya ɗora yatsarshi a laɓɓanshi alamar tayi shiru, ta kan Hameeda ta wuntsila ta sauka a gadon tana sake nunoshi da yatsa tace "Ka ga malam ka fita a nan, ni ban ga komai ba kuma ba wanda zan faɗa ma, idan ma kasheni ka zo yi to ka yi haƙuri."

Takawa ya ƙara yi har ya kai daf da gadon cikin raɗa yace "Saleema ki zo dan Allah za mu yi magana, ba cutar da ke zan yi ba."

Da mamaki tace "Magana..." Da yatsa ya sake mata alamar "Shiiiii! Yi magana a hankali."

Sassauta murya tayi tace "Maganar me za mu yi a wannan lokacin? Ka ga ni ba zan saurareka ba, kawai ka fita a nan wallahi ko na maka ihu."

Da sauri ya durƙusa ƙasa yace "Dan Allah Saleema kar kiyi, ki zo muje mu yi magana, iya nan ƙofar ɗakina saboda bana so mu tashesu."

Ƙura masa ido tayi kamar mai nazari, amma sai yayi saurin katseta ta hanyar haɗe hannayenshi alamar roƙo yace "Dan girman Allah Saleema?"

Da sauri ta ɗaga masa hannu tace "Shikenan to na ji, ka daina haɗani da ubangijina kan ƙaramin abu."

Zagayowa tayi tace "Mu je to."

Da sauri ya miƙe ya fita ƙofar ɗakin ya tsaya, jim kaɗan ta fito sam rikicewa ya sa ta manta ba ta fito da hijabi ba sai hular dake kanta kawai mu raga-raga irin ta bacci, sa'arta ɗaya kayan a sake suke basu fito da surarta ba.

Tsayawa ta yi jikin bango ta na satar kallonshi, ita wallahi kunyar kallonshi ma take ji, amma shi da alama ba haka ba tunda har ya zo inda ta ke, ɗan matsowa ya yi kusanta yace "Saleee.."

Ba ta bari ya ƙarasa ba ta ja baya tace "Ka ga ka faɗa min komai daga nan."

Murmushi ya yi ya ɗan ƙarewa surarta kallo, to ai kayan da ke jikinta wanda bai san mace ba ne kawai ba zai fahimci irin kayan alatun da ke ɓoye a cikin suturar ba, amma shi da ya gama sanin sirrin ya gama hango komai, cikin sakin fuska yace" Saleema, abunda kika gani ɗazu na ke so ki manta dan Allah, sam ba abinda kike tunani bane, kuskure ne wallahi kula jiya ne ya fara faruwa, amma na miki alƙawarin ba zai sake faruwa ba, kuma dan Allah ki min alƙawarin ba za ki faɗa ma kowa ba?"

Wani kallo ta jefo masa da mamakin kalamansa tace" Kuskure? Mu'awwaz zina ka kira kuskure? Kasan kywa da Allah ma cewa ya yi karmu kusanceta bare har mu je ga inda take, kai ka je kusa da ita kuma ka abka, amma za ka ce kuskure?"

Girgiza kai tayi cike da takaici ta sake kallonshi tace"...

*Allah ya na tsare duk wanda ya kamalta kare kanshi daga aikata alfasha.*

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_10_

Girgiza kai tayi cike da takaici ta sake kallonshi tace "Mu'awwaz abunda ka aikata zunubi ne babba, sai dai har yanzu kana da damar tuba a wajen Allah, game da ni kuma kar ka ɗaga hankalinka, ba zan tona abinda Allah ma ya rufe ba, ni ma kuma ina so ya rufa min asiri duniyata da lahirata, na maka alƙawarin babu wanda zai ji wannan maganar, amma fa idan ka yi alƙawarin kai ma na farko kenan kuma na ƙarshe."

Cike da yaudara yace" Na miki alƙawari Saleema, na farko kenan kuma na ƙarshe, wallahi ba zan sake ba."

Jinjina kai tayi tace" Shikenan, Allah ya sa."

Raɓashi tayi ta wuce tana faɗin" Sai da safe." Da kallo ya bi bayanta yana ɗan taune leɓenshi na ƙasa, abunda zuciyarshi ke raya mishi shine" Lokacin da ka san wata a ranar ka ke ganin wata sabuwar halittar."

Murmusawa kawai yayi ya sauka daga matakalar ya kama hanyar ɗakinshi da tunanin ba ma zai iya da Saleema ba, ba wai dan ta fi ƙarfinshi ba, sai dan gani yake ko aura masa ita aka yi wannan za ta fi ƙarfin iyawarshi saboda suffarta, amma kuma wani ɓangare na zuciyar nuna masa yake zai iya tunda dai mace ce.

*Washe Gari*

Kamar daga sama ta ji ana sallame salla, a zabure ta tashi zaune ta na rarraba ido, dubanta ta kai ga agogo dan ganin lokaci, sai dai inda agogon take babu haske sosai bare ta fahimci, hannu ta kai ta ɗauki wayar Hameeda ta duba, rufe baki tayi cike da rashin jin daɗi tace "Kenan dai sallah ce aka idar?"

Da sauri ta aje wayar ta sauko a gadon tana daddaɓa Hameeda, a ƙala sai da ta daddaɓata sau biyar kafin ta motsa tana faɗin "Ummm! Wai me ye?"

Da sauri tace "Ki tashi har an gama sallah."

Ta na gama faɗin haka ta nufi ban ɗaki dan rabon da ta tuna ranar da ta rasa sallah irin haka har ta manta, ma fi yawan lokuta dama Mamanta ke tashinta daga bacci, sauran lokuta kuma ita ke tashi da kanta da taimakon wayar Mamanta, juyowa tayi ta kalli Hameeda da ta sake gyara kwanciyarta tace "Dan Allah ki tashi Hameeda, ki tashe su suma su yi sallah."

Shigewa ban-ɗakin ta yi ta gabatar da abinda za ta yi ta fito a gaggauce, yanda ta barta haka ta sameta, ganin za ta ɓata lokaci wajen tashinsu ita ta makara su su rasa yasa kawai ta canza kayanta ta kabarta sallarta, duk da farilla ce a kanta yanzu, amma saida ta fara yin raka'atanil fijir saboda ta ji fatawar da aka ce indai ka saba yin raka'a biyu kafin fitowar alfijir, to ba laifi idan wani dalili ya sa sallah ta kubce maka ka yi kafin ka yi ta farilla, har ta idar da sallata su Hadeeya ba su motsa ba, cike da takaici ta miƙe ta koma ban-ɗakin ta ɗauko ƙaramar buta da ruwa a ciki, dan su ne kaɗai za su iya tashinsu, ta na zuwa kam ɗaya bayan ɗaya ta dinga watsa musu suna tashi a zabure kamar waɗanda aka firgita.

Cike da tsiwa da rashin kirki Ummee tace "Malama me ye haka? Wannan wane irin jahilci ne? Ya mutane suna bacci za ki tashesu da ruwa? Ba ki da hankali ne?"

Ɗan cije leɓe Saleema ta yi ta lumshe idonta, hakan ya bata damar haɗe abunda ke ranta kafin ta buɗe ta kalleta tace "Ku yi sallah, lokaci na wucewa."

Hadeeya ce tace "Saboda hakane ki ka tashemu? Dan baki san darajar ɗan adam ba."

Da alamu irin na ba ta jin daɗin maganar ranta kuma ya fara ɓacewa ta kawar da kanta kaɗan tace "Da sallah ku ka je kuka gabatar ya fi muku alkairi."

Juyawa tayi tana cire hijabinta Ummee tace "An ƙi a yi sallar to, dole n..."

Fauuuu! Cikin zafin nama Saleema ta kashe fuskarta da mari, a kiɗime Ummee ta dafe kunci tana kallon Saleema, Hadeeya da Hameeda ma a tsorace da kuma mamaki suke kallon Saleema, yo ko su dake ƙannenta ba ta taɓa marin ɗaya daga cikinsu ba, hasalima ko faɗa irin wannan na yara ba su cika yi ba. Girgiza kai Saleema tayi cikin jin haushi tace "Kin gani, kin hassalani, kina ƴar musulma ne za ki furta wannan kalmar? Kin kuwa san hukuncinki a wannan lokacin?"

Ummee da takaici ya gama kasheta a mugun haukace ta nuna kanta tace "Ni kika mara?"

A tausashe ka rantse ba ita ce ta mareta ba tace "An mareki, ki rama mana."

A harzuƙe Ummee ta sauko daga kan gadon ta yi hanyar fita tana faɗin "Na zan rama da kaina ba, amma zan kira wanda zai rama min."

Taɓe baki Saleema tayi da tunanin Allah yasa ma rayuka su ɓace ta samu damar tafiyarta daga wannan gida mai cike da kuraye ta ko ina, wa ya sani ma ko gado sukayi? A nutse ta gyara ɗaurin ɗan-kwalin doguwar rigar da ta saka ta jawo silifas ɗinta ta saka, ta kala hanya za ta fita ta juyo ta kalli su Hadeeya da har yanzu ke kallon kamar ba sa hayyacinsu tace "Sallar fa?"

Da sauri Hameeda ta sauko daga gadon ta nufi ban-ɗakin da alamar ta tsorata, Hadeeya kula

saida ta murguɗa baki kafin ta sauko ta nufi ban-ɗakin ta tsaya tana jiran fitowar Hameeda. Murmushi tayi da ke nuna "Ku shiga hankalinku tun wuri."

Za ta fita a ɗakin amarya ta banko kai cike da masifa hannunta riƙe da hannun Ummee, a bayanta kuma Alhaji Auwal ne da Hajia babba a gefenshi.

Kallon kallo suka dinga yi kafin amarya ta nuna Saleema tace "Ke! A kan wane dalili ki ka marar min ƴa?"

Saleema dake mamakin ganin yanayinsu dukansu, kayan da ke jikinsu bai nuna alamar su kansu sun yi sallah ba, dama-dama ma Hajia babba da alamar ruwa a jikinta, wataƙila alwala ta yi dan ko hular kanta bata ɗora dai-dai ba, cike da kunya ta kalli amaryar a ladabce tace "Aunty, sallah na tashesu su yi ba su tashi ba, shi ne ita ta ke faɗin wai an ƙi a yi sallar, shiyasa na mareta."

Da ɗumbin mamaki amarya tace "Shiyasa kika mareta? Ke baki san fuska daraja ne da ita ba? Kawai sai ki mareta dan ta ce an ƙi."

Da mamaki Saleema ta kalleta tace "Fuskar ce ke da daraja? Wa ya faɗa?"

Cike da sababi amarya tace "Ai ko a wa'azi ana faɗa cewa babu kyau dukan mace a fuska saboda tana da daraja."

Wani ɗan murmushi Saleema tayi cike da raha tace "To aunty ai wanda ya ba fuskar daraja shi ne kuma ya ce shi kaɗai yake so a turmusa fuskar nan ƙasa dominshi, kenan ya dace ta ce ba za ta yi ba?"

A hassale amarya ta sake nunota da yatsa tace "Ke Saleema! Tunda kika zo gidan nan dama na fahimci wani tsageran iskanci kike ji, to ni bana son irin haka, ki tsaya a matsayinki kawai, amma ya za ki zo gidan uban yarinya kuma ki mareta, ina aka taɓa haka?"

Gyara tsayuwa Alhaji Auwal yayi wanda da farko jikinshi ne yayi sanyi, duba da an mari ƴarsa akan ba ta yi sallah ba, to ya kenan shi idan ta ji bai tashi ba sai kukan Ummee ne ya tasheshi shi da uwar Ummeen? Cikin nutsuwa ya kalli Ummee yace" Ke je kiyi sallah."

Sai kuma ya kalli Saleema yace" Shikenan ya wuce, kowa ta je ta yi sallah."

Cike da damuwa Saleema tace" Ni na yi sallah Abba, amma dai ka faɗa musu su dinga tsayar da sallah a kan lokacinta, kamar Ummee da su Hadeeya idan aka umarcesu suyi sallah su ka ƙi kuma ba tare da wani uziri ba, sannan sun yarda babu abun bauta da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammad Manzon Allah ne, aka tabbatar sun yarda da duka shika-shikan musulunci, to fa wasu suna ganin kashesu za'ayi ta hanyar cire musu kai, wasu kuma suna ganin a'a za'a jinkirta musu ne su yi sallar sannan ya kashesu..."

Tausasa murya tayi sosai sannan tace" Abba, yanzu duk lamarin da aka tanadar wa wannan hukuncin bai kamata mu riƙeshi iya ƙarfinmu ba? Manyan Malamai magabata akwai masu fahimtar wanda duk ya bar sallah ta kubce masa da-gangan to ya zama kafiri, idan har zai yi sallah ta gaba ko ya ranka wannan sallar to a ganinsu sai an kuma bashi kalmar shahada, inda wasu malaman ke ganin a'a ba ka kafirta ba, sai dai ko kayi sallar ba lallai ubangiji ya amsheta ba saboda kayi kan lokacinta ba, dan haka wasu suke ganin kar ma kayi shi ya fi."

Raunana murya tayi kamar za ta fashe da kuka tace" Ta ya bayan na san wannan zan zuba ma ƴan uwana ido suyi wasa da sallah, bayan dukaninmu nan mun san ita ce kawai ta bambamta mu da kafiri, indiyawa su na azumi dan buƙatunsu da al'adunsu, mu ma musulmi munayi, krista suna raba dukiyarsu ga mabuƙata, akwai daga cikin waɗanda ba su da addini da suke zuwa ziyarar ɗakin Allah, imma dan buƙatarsu ko kuma ganin al'ajabin wurin da ɗaukar rahoto, sannan kafirai dayawa sun yarda akwai Allah kuma shi ya haliccesu kamar dai mu, sannan sun yarda Annabi Manzonsa ne, imani da shi ne kawai ba su yi ba, to ku faɗa min a nan me ya rabamu da su? Sallah ce kawai ko arne ya ga mai yin ta zai sa wannan musulmi ba tare da ya yi tambaya ba."

Kallon Ummee ta yi da jikinta ya mutu sosai tace" Ki tsayar da sallarki, za ta zame miki haske a ƙabarinki, sannan idan sallarki ta yi kyau a sikelin lahira, to hisabi ma bai zama lalle gareki ba."

Ita kanta amarya da bala'i ne ya kawota sosai jikinta mutu ta ji zuciyarta na dukan tara-tara tunawa da yanda ita ta ɗauki sallarta, sai kawai ta juya jiki a sanyaye ta bar ɗakin, haka Alhaji Auwal da Hajia Rabi ma suka fita suna jin gaba-ɗaya yarinyar ta gama ɗauresu da wasu manya-manyan igiyoyi da ba zasu iya kwance kansu ba.

Ganin haka Saleema ta fita a ɗakin ta hauro ƙasa tare da Hajia babba wacce yanzu ɗakinta ke ƙasa sablda wuyar da hawa saman ke mata, cikin ladabi ta tabayeta "Mama, zan iya shiga madafa?"

Murmushi ta sakar mata tace "Me zai hana Saleema, ki shiga ki ɗauki duk abinda kinke so."

Girgiza kai Saleema tayi tace "A'a Mama ba dan buƙatata ba ne, abun kari zan haɗa, na ga mai aiki ba a nan take kwana ba."

Girgiza kai tayi ita ma tace "A'a Saleema, ki bari na gama sallah sai na ɗora, dama sai rana ta yi take zuwa, iya shara da wanke-wanke da sauran ayuka take yi, amma girki mu ke yi sai dai ta taimaka mana da wani abun kawai, dan Alhaji baya son cin abincin mai aiki."

Ƴar dariya tayi tace" Hakan ya yi kyau, kamar Babana shi ma haka yake, amma ki bari ni zan ɗora, idan da buƙata ku sai ku ɗora na Abba idan kun ida sallah."

Faɗaɗa murmushi tayi tace" Nagode Saleema, Allah miki albarka."

Da fara'a ita ma ta amsa da" Nagode Mama, amma me za'a dafa?"

Da fara'a tace" Saleema ko me kika dafa ma ai ya yi, ki duba a madafar akwai duk abun buƙata, idan kuma kin rasa wani abun ki min magana."

Jinjina kai tayi cike da ladabi ta wuce madafar inda ta fara da abinda ta gani kuma ta iya sarrafawa. Hajia Rabi na idar da sallah ta fito za ta shiga wajen Alhaji dan tambayarshi abinda zai ci, Mu'az ne ya shigo gidan dan bai kwana a gida ba, tsaye tayi har ya ƙaraso yana gaisheta da "Ina kwana Mama."

Na wasu daƙiƙu ta fara zuba masa ido kafin tace "Ba'a gida ka kwana ba ko?"

Ba tare da damuwar komai ba ya amsa da "E Mama."

Ba alamar wasa a tare da ita dan bata so ya kawo mata wargi duba da tambayar da za ta mishi ba ta taɓa kwatanta yi masa ita ba sannan tace "Ina ka kwana?"

Da sauri ya saka idonshi a cikin na ta kamar wanda aka ba wa tsoro, sai kuma ya saka fuskar mamaki yace "Mama, me ya sa kika tambaya? Wani abu ya faru ne?"

Sake haɗe fuskarta tayi tace "Sai wani abu ya faru zan tambayeka?"

Ɗan girgiza kai yayi yace "E to Mama, na ga dai haka bai taɓa faruwa ba ai."

Tsareshi tayi da ido tace "Amsar tambayata?"

Ɗan matse bakinshi yayi yace "Abinci na fara ci a restaurant, sannan na wuce majalisarmu, ba mu tashi a nan ba sai ƙarfe uku na dare, daga nan mu ka ƙarasa gidansu *Zeid* a can na kwana."

Wani sakaran murmushi ta yi tace "Ka kwana ko ka rintsa? Ai ka gama kwananka tun a majalisa."

Gyara tsayuwa ta yi tace "Sallah da, ka yi sallah kafin ka shigo?"

Ƙanƙance ido yayi yana mata kallo mai kama da hangen nesa yana so ya gano me ke damun Mamanshi yau? Cikin mamaki yace "Na yi sallah Mama."

Harara ta galla masa tace "Yanzu ka yi ko?"

Sosai ƙeya yayi alamar kunya bai ce komai ba, girgiza kai tayi tace "Allah ya shirya."

"Ameen Mamana." Ya faɗa yana binta da kallo, ganin za ta yi nisa ya matsa kusanta yace "Mama."

Juyowa tayi tana kallonshi amma ba ta ce komai ba, da ɗar-ɗar din amsar da za ta bashi yace "Mama wani abu ya faru ne?"

Da mamaki tace "Me ka gani?"

Sunkuyar da kai ya yi yace "Na ga ai kina ta min wasu tambayoyi ne kamar ƙaramin yaro ko wata mace."

Wani kallo ta mi shi tace "Au! Ina matsayin mahaifiyarka ba zan tambayeka ba tunda ka wuce munzalin?"

Girgiza kai yayi yace "A'a Mama ba haka nake nufi ba, abun dai ne ya zo min wani iri, baki taɓa haka ba fa Mama."

Jim! Ta yi ta kalleshi kuma ta san gaskiya ya faɗa, gyara tsayuwarta ta sake yi tace "Gaskiya kam, ni ma kuma na san tambayoyin da na maka sabon abu ne, amma dan Allah da na tambayeka ba ka ji daɗi ba?"

Murmushi ya sakar mata tare da dafa duka kafaɗunta ya ɗora haɓarshi a wuyanta yace "Na ji daɗi sosai Mamana, hakan ya nuna min yanda ki ka damu da ni."

Turo ɗan bakinta tayi gaba cikin shagwaɓa tace "Zuwan yarinyar nan ya zamar mana alkairi, daga jiya zuwa yau ta haska mana abubuwa da dama da suke shige mana duhu, musamman ma a kan sallah da ta tunatar da mu yanzun, sai na ji kamar zan zauna na yi ta kuka saboda kurakuren da muka tabka a baya, amma in sha Allah na ɗauki niyyar gyarawa da wannan nasihar da ta mana."

Hannu ta zura ta bayanta ta shafi kumcinshi a shagwaɓe sosai tace" Gaskiya yarinyar kirki ce, ina ma za ta zama surukata?"

Da mamaki ya ɗaga kanshi kaɗan yace" Mama, wacece wannan?"

Hararan wasa ta jefa mi shi tace" Wa fa ban da Saleema."

Wani ƙasaitaccen murmushi ya saki tare da maida haɓarshi a kafaɗarta, haka kawai ya ji wani shauƙi da daɗi na sunan da ta ambata, shiru ya yi ya lumshe ido a kafaɗarta kamar bacck zai ɗauke shi. Tureshi tayi tace" Kai ɗagani, har yanzu ban shiga madafa ba."

Takwaf-takwaf ya yi da fuska yace" Mama yunwa fa na ke ji, shiyasa na shigo da wuri."

Nuna mishi ƙofar madafa ta yi tace" Ka shiga madafa ba za ka rasa abun da za ka ci ba."

Turo baki ya yi gaba ya nufi hanyar madafar ita ma ta ƙarasa in da za ta je sam ta ma manta da Saleema na madafar.

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_11_

Yana shiga madafar ya tsaya cak! Ya na ƙare mata kallo daga baya, rumgume hannaye ya yi da

tunanin to ita haka take shigarta kullum? Ko kuma dai baƙunta ce ta sa haka? Sai kuma wata zuciyar ta raya masa "Idan baƙunta ce ai ƴan uwanta ma baƙuntar suke, me ya hanasu kama jikinsu kamar ita?"

"Tarbiyya ce kawai." Wata zuciyar ta bashi amsa, abaya ce jikinta da kallabinta wanda sam jikinta bai bayyana ba, a hankali ya sauke hannayenshi daga ƙirjin ya shiga takawa gareta, bayanta ya tsaya ya ɗan dubi tukunyar da ke kan wuta wacce take soya naman da ta samu a fridge, tsilalar da yake na jajjagen da ke jikin naman kuma aka saka cikin mai me zafi, wannan tsuwar ce ta hanata jin tako daga bayanta saboda tana ta ƙoƙarin kare kanta kar mai ya ki ƙonata.

Ba ta ankara ba, ba ta san da faruwar abun ba, hannaye bibbiyu kawai ta ji sun zagaya kumkuminta an kwantar da kai a bayanta cikin wata tattausar murya yace " *Leema* sann..."

Tunda ta ji irin ruƙunƙumewar da aka mata ta sa ma ranta mace ba za ta mata haka ba, ko da ta ji muryar Mu'az tun bai gama maganar ba ta juyo a mugun tsorace kuma a fusace ta ɗauke fuskarshi da mari ta bayan hannunta. Kallon kallo su ka tsaya kowa da irin fitinannen kallon da yake aika wa ɗan uwanshi, ita kam mamaki da ɓacin rai ne suka lulluɓeta cike da dana-sanin zuwa gidan nan da ta yi wanda sam babu alkairi a ciki sai jafa'i da ta ke gani kala-kala.

Shi kuma mamakin ƙarfin halin ta da kuma tsoron da ya ke hangowa a idonta mai ɗauke da ɓacin rai na aljabi yasa shi sakin murmushi, a hnkali ya jaye hannunshi daga kumcinshi ya ɗa ja baya kaɗan, cikin raha alamar dai abun bai wani ɓata ransa ba yace "Na samu abinda na ke so, wannan shi ne abinda ya kamata na gani a tare da wacce na ke so sa'ilin da wani wanda bai da hurumi a kan ta ya kai hannunsa jikinta, hakan alamu na cewa za ki iya yankar duk wanda ya yi ƙoƙarin taɓa min *halaliyata*."

Wasu mugayen hawaye ma su zafin gaske ne suka kwaranyo mata daga kurmin ido na takacin wannan rana da ta risketa, tunda ta balaga ko Mamanta kunya take ji ta rumgumeta bare kuma Abbanta, amma yau ƙato da ba ta da haɗin komai da shi ne ya kwanta a bayanta tamkar wata matarsa. Hannu tasa ta share hawayen ta furta "الحمد لله الذي بنعمته تتم الصالحات (Godiya ta tabbata ga Allah wanda saboda ni'imarsa ce kyawawan ayyuka suke cika)."

Da sauri ta yi azamar raɓashi za ta bar wurin duk da kuwa ta na jin naman da take suya ya na neman ƙonewa, da sauri ya tare gabanta har tana neman faɗawa kan shi ya yi saurin faɗin "Dakata."

Da sauri ta kalleshi cikin muryar kuka da kuma ƙunar da ke cin zuciyarta tace "Ka matsa min a hanya, idan ba haka ba wallahi zan maka ihu."

Cike da isa ya rumgume hannaye a ƙirji yana murmushi yace "Bismillah, yi, ko ba ihu ba? Yi ihu ki ce kwarto ne ni."

Da mugun sauri ta liƙe kunnuwanta tana fashewa da kuka ta durƙushe ƙasa tana faɗin "Dan Allah ka rabu da ni, ka tafi ka bani wuri, wai me yasa ba ku da ɗa'a ne? Ku wasj irin karnuka ne?"

Da wani mugun sauri ya finciko hannunta da alamar ya ji zafin kalmar ta ƙarshe, ba tare da ya saki hannunta ba ya haɗata da bango ya matse mata wuri sosai, tsabar tsoron da ya kamata yasa ta duƙar da kanta ta gandarawa hannunshi cizo. Amma da ke ranshi ya ɓace da ta haɗashi da kare sai ya yi kamar bai ji ba, matse hannunta ya sake yi sosai har ta saki ƙara tana matse fuskarta, Mu'az kam mutum ne mai son raha da barkwwanci, sai dai akwai abun da sam ba ya ɗauka kuma a take ranshi ke ɓacewa. Cikin jin zafi ya kalli fuskarta yace "Wa ye kare? Ni ki ke haɗawa da dabbar da ake ajiyewa dan tsaro kawai?"

Wani kukan ta sake sakawa mai ban tausayi tana neman sulalewa ƙasa a ƙasan maƙoshi ta furta "Hannuna."

Da sauri ya kalli hannunta da ya matse, a hankali ya sassauta mata riƙo yana jin tausayinta na mamaye zuciyarshi, saida ya saki hannunta gaba-ɗaya sannan ya sunkuyar da kai yace "Ki yi haƙuri, kuma nagode da marina da ki ka yi."

Juyawa ya yi har zai fita sai kuma ya tsaya, a hankali ya tako ya dawo gabanta ya tsaya duk da ta rufe fuska tana kuka, cikin tattausan murya mai kashe jiki yace " *Ina son ki*."

Da sauri ya juya ya fita a madafar ya ma manta me ya shigo da shi da fari, tana jin ya fita da sauri ta ƙarasa gaban gas ɗin ta kashe wutar, tana kwashe naman ta na sako da hawaye har ta kammala abinda ta fara sannan ta barsu a nan ta fita a madafar, tana haurawa sama tana tunanin tafiyarta gida ne, ba zata iya zama a gidan nan ba ko kaɗan, ba ta sani ba ko mahaifinsu ya san haka gidan yake ya turosu? Amma dai ba ta zauna ba ita kam, dan in suka zauna daga ita har ƙannenta cikunna ne za su bayyana garesu nan da kwana kaɗan, dan ita tsoronta kar shi ma uban haka ya ke ya fara ƙare musu kallo.

Tana shiga ɗakinsu da kuka ta share hawayenta ta nufi inda jakarta take da kayanta da basu wuce guda uku ba bayan na bacci, Hadeeya na kwance da waya a hannunta, Hameeda ma kwance take suna kallon hotuna a waya ita da Ummee, da kallo duk suka bita sanda ta ɗauki jakar tana tattara kaya tana zubawa ciki, saida ta gama tsaf ta ɗauki zunbulelen hijabinta ta saka, ta ɗauki jakar kenan za ta fita Hameeda da ta fi damuwa da abinda ta ga Saleema na yi tace "Ina za ki je?"

Juyowa ta yi ta kalleta tace "Gida, sai kun zo."

Da mamaki Saleema tace "Gida kuma? Abba fa cewa ya yi..."

Cike da raini Hadeeya tace "Ki barta ta tafi mana, ai ta san Abba ya faɗa mana zai turo a ɗaukemu bayan kwana biyu, shi ne dan ta rainashi za ta ce za ta tafi yanzu."

Dogon tsaki ta ja ta maida hankalinta ga abinda take, Hameeda kuma ci gaba da kallonta tayi har saida ta fita a falon, tana sauka ƙasa Hajia Rabi na fitowa daga madafa, dama kuma ta shiga ne dan ɗorawa Alhaji abinda ya buƙata, ta samu abun kari an gama shiryawa amma ba ta ga Saleema ba, fitowarta dan ta duba ɗakinsu ne sai kuma suka haɗe.

Cike da kulawa da kuma fara'a a fuska tace "Yawwa Saleema, na duba ciki ai ban ganki ba, ashe har kin gama girkin? Kai gaskiya Saleema kin yi ƙoƙari, dama haka kika iya girki?"

Hijabin da ta jawo tana ƙara goge fuskarta yasa Hajia Rabi ganin jakar dake hannunta, da mamaki ta matso kusanta tana faɗin" A'a! Saleema ina za ki je da jaka kuma?"

Sunkuyar da kanta tayi cike da kunya da shaƙaƙƙiyar murya tace" Mama gida nake so na tafi, ina kewar Mamana ne... "

Da sauri ta riƙo hannun Hajia tana ci gaba da faɗin" Dan Allah Mama kar ki hanani tafiya, ina so na ga Mamana ne."

Sosai Hajia ta shiga mamaki da kuma zuba mata ido tana nazarinta da kuma son gano gaskiyar kalamanta, cike da kokonto tace" Saleema, wani abu aka miki ne a gidan da ba ki ji daɗi ba?"

Da sauri ta girgiza kai tace" A'a Mama, ba abinda aka min, nk dai kawai ki barni na tafi."

Sakin hannunta tayi ta ƙara riƙe jakarta ta ɗan raɓata tace" Nagode Mama, sai anj..."

Riƙota Hajia tayi tace" A'a Saleema, ba zan barki ki tafi ba, ko dai ki faɗa min abinda aka miki? Ko kuma na kira Alhaji na faɗa masa."

Kamar za ta durƙusa ƙasa ta shiga gurfanawa tana faɗin" Mama, Mama kar ki faɗa mana dan Allah, Mamata na ke ji kamar tana cikin wani hali, ki barni na je na duba idan na sameta lafiya sai na dawo."

"Ina za ki je?" Alhaji Auwal ya faɗa daga bayansu yana fitowa, tare suka kalleshi sai da Saleema ta sauke ƙaƙƙarfan numfashi, saida ya ƙaraso gabansu ya tsaya yana kallon Saleema yace "Ina na ke jin kina cewa za ki tafi?"

Tsareshi tayi da ido ta girgiza kai alamar ba komai, kallon Hajia ya yi yace "Me yake faruwa?"

Kallon Saleema tayi sannan ta kalleshi tace "Wai gida za ta tafi, na tambayeta me aka mata ta ce ba komai."

Kallon Saleema ya yi da ke ta fiƙi-fiƙi da ido yace "Me aka miki?"

A raunane tace "Ba komai Abba, dama kewar Mama na yi."

Wani kallo ya watsa mata kafin yace "Je ki aaje jakar, ba haka mukayi da Abbanki ba, idan kuma kin dage za ki tafi sai na kira na faɗa masa."

Da sauri tace "A'a Dan Allah, kaa yi haƙuri Abba na fasa tafiyar."

Hanyar ɗakin ta kama sai kuma ta juyo tace "Amma Abba Mu'a..."

Sai kuma ta ga kamar bai kyautu ta faɗa musu ba, dan haka ta juya da sauri kawai ta barsu nan tsaye suna binta da kallo har ta shige sannan su ka bar wurin.

*Bayan minti 20*

Hamdeeya ce ta shigo da sauri ɗakin tace "Saleema wai in ji Abba ki zo."

Kallonta tayi kamar ta ce ba za ta zo ba, dan ta fi jin nutsuwa a zaman ɗakin, amma sai ta jinjina kai tace "Ina zuwa."

Da gudu Hamdeeya ta fita kafin ta miƙe jiki a sanyaye ta ɗauki hijabinta akan riga da siket ɗin da ta saka yanzu bayan ta yi wanka, cikin nutsuwa da dattako ta shiga taka matakalar, ba ta ɗaga kai ta kalli inda ta ji mutanen suke ba, sai dai daga yanda take ji akwai ido sosai dake yawo a jikinta, bata kuma tantance su waye a wurin ba.

Saida ta gama sauka sannan ta ɗan ɗaga kanta dan ta san inda za ta dosa, fahimtar Alhaji Auwal ya na kan teburin cin abinci ya sa ta nufa can ɗin, tun kafin ta ƙarasa yace "Yawwa zauna."

Kanta a sunkuye kamar wacce ta aikata abun kunya ta ja kujerar da ta kula ba kowa a kai ta zauna, hannayenta da suka fito waje sanadiyar hijab ɗin ta mai hannu ta ɗora akan teburin ta na wasa da yatsunta cike da kunya da ladabi. Hajia Rabi da ke kallonta cike da birgewa da ƙaunar yarinyar tace "Saleema, ki saki jikinki kin ji, ki ci abinci."

Sai lokacin ta ɗaga kanta dan kallon Hajiar, sai dai a lokacin ta kula da waɗanda ke wurin, Alhaji Auwal ne da amaryarshi, sai Hamdeeya da ita Hajiar da kuma wannan *kuren*, ba ta yarda ta haɗa ido da shi ba dan jikinta ya bata kallonta yake, a hankali ta ja farantin gabanta ta ɗauki cokalin ta fara tsakurar abincin. A sace ta kalli Hamdeeya cikin raɗa tace "Ina su Hadeeya?"

Nuna mata wani ɗakin ta yi dake nan ƙasa tace "Suna ɗakin Yaya Mu'awwaz."

Wani irin faɗuwar gaba ta ji ya ziyarceta, da sauri ta ƙwalalo ido tace "Me suke yi?"

Taɓe baki ta yi tace "Ni ma ban sani ba."

Ɗaga idonta tayi da niyyar kallon Alhaji Auwal, sai kuma idonta suka sauka cikin na Mu'az da ya rumgume hannaye ya na kallon duk wani motsinta, shi da ma saboda ita ya tsaya wurin ba dan ya ci abinci ba, wani irin kallo ne ya ke mata ya na jin shi dai kawai birgeshi ta yi lokaci ɗaya ba dan kyanta ko nasabarta ba. Suna haɗa ido ya sakar mata murmushi cike da tsokana yace "Za ki ci abincin? Ko na ɗura miki?"

Ɗan waro ido tayi da mamakin rashin kunyarshi, sai kuma ta ɗauke kai ta sake kallon Alhaji za ta nemi izininshi, kafin ta yi magana Mu'az ya sake faɗin "Abba."

"Na'am." Ya faɗa yana maida kallonshi ga gareshi, Mu'az kuma Saleema ya ƙurawa ido ba tare da yanayi na wasa a tare da shi ba yace "Na ce ko ka yi wa ƴarka miji ne?"

Shi da Hajia Rabi tare suka saki murmushi suna kallon Saleema, inda amarya ta yatsina fuska ta kalli Mu'az ɗin ta na ganin me ye na wannan tambayar? Sam a ganinta bai ma kamata a ce Mu'az ya yi wannan tunanin akan wannan yarinyar ba, dan ta na da labarin rashin iliminta da wayewarta, yatsina baki tayi tana kallon Alhajin da yake faɗin "A'a, me ya sa ka tambaya aboki? Ko dai ƴar ta wa ta sace tsoka ma fi mahimlanci ne a jikinka?"

Wata ƴar dariya yayi ya sunkuyar da kai sai kuma ya ɗago yace "Ni dai  Abba idan ba ka mata miji ba, to ku taimaka min kar na ƙara zama tuzuru a gidan nan, idan shekarar nan ta wyce ban yi aure ba gallabarku zan yi."

Saleema da ta yi mutuwar zaune da ido kawai ta ke binshi kamar wani sabuwar halitta ne ta gani, Alhaji Auwal kuma dariya kawai ya ke sai Hajia Rabi da ta ɗan dakeshi a kafaɗa tace" Marar kunya kawai, me za ka yi to?"

Saleema ya kalla ido cikin ido ba tare da shayin komai ba yace" Ba zan bari ta zama ta kowa ba, zan mayar da ita *mallakina* ko ba ta so."

Yanzu kam da ke ranta ya gama ɓaci na takaicin bawan Allahn nan, zabura ta yi ta miƙe da sauri ta nufi hanyar madafa, dan gani take idan sama za ta hau za ta jima ba ta kai ba, da kallo duk suka bita har ta ɓacewa ganinsu, cike da izgili da raini amarya ta kalli Mu'az tace "Wannan yarinyar fa ba ajinka ba ce, ba ta da ilimi sannan ga ta ƴar ƙauye, ka nemi dai-dai da kai mana."

Kallonta yayi irin kallon nan na nidai ban saka bakinki ba, sannan ki min shiru ko ki ji ba daɗi, ya mata wannan gargaɗin da ido ne dan kar ta hassala shi ya faɗa mata magana Abbanshi ya ce ya rainata, dan haka yake so ta masa shiru kawai. Fahimtar kallon yasa ta ɗauke kai ta na sake yatsina baki da tunanin "Ita ina ma za ta yarda Mu'awwaz ya ɗauko mata ajawo irin yarinyar can?"

Da haka ma ta yanke shawarar tunkarar lahaifiyar yarinyar da maganar, dan ta san su ɗin amare na musamman ne, idan suka yanke hukuncin to mazan za su ce ya yanku ne kawai.

Alhaji Auwal da farin cikin hakan ya kamashi kallon Mu'az ya yi yace" Karka damu aboki, indai da gaske kake ka shirya za mu je wajen mahaifinta sai mu nemo aurenta."

Cikin jin daɗi Mu'az ya ba wa mahaifin na shi hannu suka tafa yana faɗin" Yawwa aboki, na ji daɗi, idan mukayi sa'a ma ya amince nan kawai za ta zauna sai dai na mata lefe da gado."

Dungure masa kai Hajia Rabi tayi tace" Sheɗani, wato ba za ka bata damar sallama da iyayenta ba kenan?"

Sosa ƙeya yayi yace" Wane sallama kuma Mama bayan ga waya? Ta je daga bayan idan ta gama jego."

Buɗe baki Hajia tayi da mamaki da kuma kunyar maganar sa, Alhaji Auwal na dariya yace" Abokina da alama yanzu kam ƴar manuniya ta fara azalzalarka ka yi aure ko?"

Bushewa sukayi da dariya shi da Mu'az sai Hajia Rabi da ta miƙe tana faɗin" Allah ya shiryaku shirin addinin musulunci."

*Saleema* kuma na shiga madafa ta samu mai aikin nan tana wanke-wanke, a hankali ta rage saurin da ta shigo da shi na bala'i da gwaramar da bawan can ke haɗa mata da bata san dalili ba ta fara takawa har zuwa kusa da ita tana kallonta, ƙarara tsoro ya bayyana a matashiyar kamar za ta arta a guje, saida ta samu tabbacin yarinyar da ta gani jiya ce sannan ta shiga ƙare lata kallo daga sama zuwa ƙasa.

Bayan abubuwan nan da ita ma Allah ya hore mata guda biyu, wata cikakken ƙirji da mazaunai ba ta ga wani abu da yarinyar ke da shi da za ta birge Mu'awwaz da ake ikrarin na da tsantseni da ƙyanƙyami ba, numfashi kawai ta sauke da ta tuna wa'azizzika da take saurare da suke magana kan mata da miji, ita kam ta san akwai wani babban tasiri da magana-ɗisu dake da tasiri a jikin namiji wanda a jikin mace kaɗai ake samunsu, dan abun ya girmi tunani ka ga ma'aurata sun yi faɗa baja-baja da rana, amma da dare ya yi su sulhunta kansu, musamman ma namiji da shi ya fi fara neman sulhun. Ko shakka ba ta yi cewa wannan yarinyar ma Allah kaɗai ya san *BAIWAR* da ke tattare da ita da ya sa har ta ɗauki hankalin Mu'awwaz, yaro ɗan ƙwalisa, ga kyau ga nasaba ga kuɗi da ilimi.

Lura da kamar ta na tsoron Saleema ya sa ta sakin murmushi tace "Me ye sunanki?"

Da sauri ta ɗago ta kalleta ido har sun cika da ƙwalla tace "Hajia dan Allah ki yi haƙuri, ka da ki tona min asiri, wallahi ba laifina ba ne."

Cike da raha Saleema tace "Sunanki fa kawai na tambaya, amsa ce mai sauƙi."

Marairaicewa tayi tace " *Nafissa*."

Kallon tsanake ta mata tace "Nafissa, ba ki san cewa ke mace ba ce? Abinda ki ka aikata jiya zai iya zama silar rugujewar duka zuri'arki, wannan abun da ki ka bashi ba tare da aure ba, shi ɗin dai shi ne mutumcinki da za ki yi tutiya da shi, me ya sa kika bayar da shi a arha haka?"

Sunkuyar da kai ta fara yi cike da nadamar rayuwarta da kuma dana-sani, cikin kukan da ba shi da anfani a yanzun tace"...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_12_

Cikin kukan da ba ya da anfani yanzun tace "Ni ma ba'a son raina ba ne, iyayenmu sun rasu kuma ina da ƙannai guda uku duka mata, sai na yi aiki sannan in ciyar da su, shi ne sanda na fara aiki a gidan nan Alhaji Mu'awwaz ya ce zai bani aikin da zai linka min abin da za'a biyani, na ɗauka wani aikin ne ashe dam...ashe wai..."

Lumshe ido Saleema ta yi tana sauke numfashi kamar wacce ta sha wahala, cikin matsanancin kuka Nafissa ta ci gaba da cewa" Tun daga lokacin ya ke min barazana da kar na sake kowa ya ji abin da ke faruwa, duk da ina biyan buƙatuna da na ƴan uwana da kuɗin da yake bani, amma dai ina jin ba daɗi sosai kan abin da muke aikatawa."

Kallonta Saleema tayi da mamaki tace" Dakata! Dakata! Na ji kina cewa daga lokacin, kina nufin ba jiya ne ya fara faruwa ba?"

Ɗagowa tayi ta kalleta tace" Ko kaɗan, wata uku kenan yanzu da hakan yake faruwa."

Da tsabar mamaki Saleema ta rufe bakinta da tafin hannu tace" Wata uku? Ki na sakar masa jikinki kamar wanda ya biya sadakinki?"

Ɗauke hannun tayi ta kawar da kanta, cikin kuka Nafissa tace" Hajia ina cikin wani hali ne, ƙanwata da take bi min ta fara fita ban san ina take zuwa ba, hakan ya ɗaga min hankali da na taɓa ganinta a tasha tare da wata ƙawarta da kula irin karan motocin nan, sai na ke jin da duka mu taru mu lalace, gwara a ce ni kaɗai abun ya shafa, shiyasa na ci gaba da biye masa ya na bani isassun kuɗin da na ke musu duk abun da su ke so, kuma rabin abin da na samu kishiyar Mamanmu ta ke ƙwacewa."

Juyowa Saleema tayi ta fuskanceta tace" Wai tsaya! Dama ba ku kaɗai ku ke rayuwa ba?"

Girgiza kai tayi tace" A'a, tare da kishiyar Mamanmu mu ke, mahaifinmu ya rasu shekara ɗaya da ta wuce, tun daga lokacin rayuwa ta sake mana zafi, matar Babanmu da ƴaƴanta gallaza mana kawai suke, gidan da muke ciki ma a rabon gado su aka ba wa, yanzu haka muna zaune gidan ne muna biyan kuɗin hayar ɗakin da mu ke ciki."

Cikin jin haushi da takaici Saleema ta ɗan daki teburi ɗin gabanta tace" Sheɗaniyar mata."

Kallon Nafissa ta yi tace" To amma ba ku da wasu ƴan uwana?"

Cike da jimami ta ɗan murmusa tace "Akwai, amma rashin sa'armu shi ne, mun zo a lokacin da ake wasa da zumunci, kowa na shi kawai ya sani, kafin rasuwar mahaifina har aurena aka

tsayar, amma da ya rasu kuma matarshi da ƴaƴanta suka handame ɗan abun da ya bari a duniya, haka ina ji ina gani aka fasa aurena."

Cike da takaici Saleema tace" Saboda me wai?"

Kallon fuskar Saleema tayi tace" Saboda babu wanda zai min kayan ɗaki, iyayen wanda zan aura kuma su ka ce sam ba za'a yi haka da sj ba, wai shi ne zai min kayan kenan? Ba dan dukanmu muna so ba suka soke aure, yanzu ma har ya yi aurenshi.."

Ta ƙarasa faɗa ta na wasu hawayen, cike da tausayawa Saleema tace" Kun yi karatu ne?"

Jinjina kai tay tace" E, amma ni shekara ɗaya kenanda na daina, saboda fafutukar da na ke ba za ta barni na yi karatu, a ƙalla wannan gida na uku ne nake aiki, kafin shi kuma na yi wanki da daka, har sarrafa awara na dinga yi na mutane ma su siyarwa, sannan na yi aikin wanke-wanke a ƙarƙashin mai siyar da abinci, sannan na yi aiki a gidan wata Hajia da ita ma take siyar da abinci, muna tayata girki tana ba mu abinci da kuɗi, na ji daɗin aikina sosai a gidan duk da ba wasu kuɗi na ke samu ba, sai dai akwai maza da ke shigowa gidan siyan abinci, tun a nan na ke fuskantar farmakin maza, sai kawai na haƙura da aikin dan na tsira da mutumcina, ashe Allah ya rubuta ba a can zan rabu da shi ba sai a nan."

Da sauri ta kalli Saleema da ta ji shasheƙar kuka, ai kam hawaye ta ga tana yi sosai, da sauri ta matso kusanta ta dafa kafaɗarta tace" Hajia ki yi haƙuri kin ji, ni dai dan Allah ki rufa min asiri kar ki faɗa ma kowa, na miki alƙawarin ba zan sake amincewa da shi ba."

Cikin kuka mai ban tausayi Saleema ke faɗin" Mu na rayuwa a babban gida cikin farin ciki, za mu ci abinci da safe, sannan mu nemi abun taɓawa idan rana ta yi, idan aka jima za mu ci abincin rana, zuwa yamma kaɗan mu sake cin wani abun dan marmari ko sha'awa, idan dare ya yi mu ci na dare, wasu lokuta mu kan ci abinci kala uku ko biyu, baya ga kayan daɗin da mahaifinmu zai siya mana, ban taɓa buɗa wurin ajiyar mahaifiyata ban samu kayan ƙwalam da maƙuashe ba, ban san me ye yunwa ba a rayuwata... Ashe wasu na can suna fafutuka da abin da za su ci? Ashe wasu yara marayu na can na neman abin da za su rayu da shi? Ta ya na yi wannan kuskuren? Ta ya?"

Wani matsanancin kuka ta fashe da shi ta zube ƙasa, hankali tashe Nafissa ta tsuguna ta na bata haƙuri, sai Saleema ta bata tausayi sosai da jin cewa lallai wannan ta musamman ce a cikin ahalin nan, wai kukan nan a kan damuwarta ne? Kuka sosai Saleema ke yi kamar ranta zai fita har saida Nafissa ta tuna da muhimmin abu da take ta yi saurin faɗin "Hajia dan Allah ki daina kukan nan, kar ma su gidan su zo su ɗauka wank abu na miki su koreni, dama tun jiya ya ce kar na sake zuwa, amma saboda ba ya so a zargeshi ya ce na zo yau, amma daga yau ba zan sake dawowa gidan nan ba, ni yanzu zan je na kaiwa Alhaji maganinshi lokacin shan shi ya yi."

A hankali Saleema ta ɗago kanta ta kalleta tace" Ba za ki daina aiki ba, za ki ci gaba da zuwa

kamar kullum, Mu'awwaz kuma zai biya a kan abin da ya aikata, na miki alƙawarin ƙwato mi ki ƴancinki."

Miƙewa sukayi a tare Nafissa na kallonta tace" A'a Hajia, kar ki sa kanki a haɗari saboda ni, ki barshi shi da Allahn da ya halicceshi, ba ni kaɗai ya wa haka ba bare na fi kowa jin zafi, tun kafin ya fara nemana na taɓa kamashi da wata ƴar ƙanwar Mamansa a ɗakinshi, hakan halinshi ne, idan ki ka matsa za ki iya rasa na ki mutumcin ke ma."

Wani murmushi ta yi tace" Bai isa ba, Allah ne ya ce "Wanda ya dogara da shi to ya isheshi." Ta ya wani ƙaramin alhaki kamar Mu'awwaz zai cutar da mu yanda ya ke so kuma ya kasa girban abin da ya shuka? Ba zai yiwu ba."

Jinjina kai Nafissa ta yi cike da jin ƙaunar matashiyar lokaci ɗaya tace" Hajia zan tafi na kai wa Alhaji maganinshi, zan dawo yanzu."

Da mamaki ta kalleta tace" Dama Alhaji bai da lafiya ne?"

Da sauri tace" A'a ba wannan Alhajin ba, mahaifin mai gidan."

Waro ido Saleema tayi tace" mahaifin mai gidan? Dama a gidan nan ya ke? Ko wane gidan ki ke zuwa kullum kai masa magani?"

Girgiza kai ta yi tana fara'a tace" A'a, a nan bayan gidan yake."

Jinjina kai Saleema tayi duk a tunaninta gidan tsohon a nan unguwar yake bayan gidan Alhaji Auwal, dan haka ma ta gyara fuskarta tace" Muje na rakaki."

Jinjina kai tayi ta buɗa wata drower ta ɗauki magunan sannan suka fita a madafar tare. Yanda su ka barsu nan suka same su, sai dai su Hadeeya sun fito daga ɗakin suna zaune kan kujera, ganin Hameeda da Hamdeeya sun sa Mu'awwaz tsakiya duk sun shige jikinshi suna kallo abu a waya, kuma kowa na kallonsu ba mai tunanin komai, ga amarya da hakan ma ya mata daɗi a ganinta suna fahimtar junansu kenan.

A sukwane Saleema ta yi kansu, ta na zuwa duka hannayensu ta kamo ta jawosu da ƙarfi ta watsar a gefe, hakan ya sa Hamdeeya fashewa da kuka ta tashi da gudu ta nufi Hajia Rabi, rai ɓace Saleema ta nunawa Hameeda yatsa tace "Ki yi nesa da shi, idan ba haka ba ranki zai ɓace."

Miƙewa Hameeda ta yi za ta yi magana sai kuma cikin hargagi Saleema tace "Wannan zaman ɗa'a ne da kunya? Ki na mace kadarar da ta fi kowace kadara daraja ne za ki wani shige jikin wanda ba ki san halinsa ba, to ki kiyaye."

Wani dogon tsaki ta ja tare da wurgawa Mu'awwaz da ke kallonta baki sake harara sannan ta

fice ko ta kan iyayen ba ta bi ba, wani salihin murmushi Mu'az ya saki tare da ɗan girgiza kan shi ya miƙe ya koma ɗakinshi dan ƙarasa shiryawa ya fuce aikin shi.

Amarya kuma da abun ya ƙona mata rai fiye da kima miƙewa ta yi ita ma ta kalli Mu'awwaz tace "Biyoni ɗakina."

Jiki a mace ya miƙe ya bi bayanta inda sauran suka bisu da kallo, ajiyar zuciya Alhaji Auwal ya sauke yana tunanin lamarin yarinyar nan da zuciyarshi ke neman raya mi shi ko dai *waliyiya* ce.

Suna shiga ɗakin cikin ɓacin rai ta kalleshi tace "Kai, kana son Hameeda ne?".

Mamaki tambayarta ta bashi sosai, sai ya ɗauke kai cike da rashin ba wa abun mahimmanci ya zauna bakin gadonta yace "Wane irin so kuma?"

A hargitse tace "So dai so, so wanda ka sani."

Taɓe baki yayi yace "Ban taɓa jin haka ba, wataƙila ko nan gaba."

Miƙewa ya yi zai bar ɗakin tace "Dan ubanka magana na ke magana."

Tsayawa ya yi ya kalleta yace "Ina jinki."

Kallonshi tayi sosai ba tarz da damuwa da yanda ya ce kna jinki ba ɗin kamar wata ƙawarshi tace "Idan na sama maka aurenta za ka amince?"

Tsura mata ido ya yi yana mata kallon nan na nesa yace "Wai me ye matsalar? Auren me kuma ina zamana a haka? Shekarata nawa ne duka da za ki wani ce ki min aure?"

Da sauri ta matso ganin kamar ta na hassalashi ta dafa kafaɗarshi cikin rarrashi tace "Haba yarona, kai ba ka ga Hameeda kyakyawa da ita ba, ga ta da wayewa da ilimi, ga sura mai kyau da iya kwalliya ga hasken fata kamar dai kai ɗin."

Kashe masa ido ɗaya tayi tace "Haba dai na wa, ka duba da kyau ka gani mana."

Shiru ya mata ya na sauke numfashi tare da tunanin abin da ta faɗa, samun kansa ya yi da murmushi sanda sheɗan ya raya masa "Hameeda ai kamar tuffa ce, ka yarda ka aureta ko dan ka yi ta gatsar abar ka duk sanda ka so."

Wata sahihiyar dariya ya saki ya kalli amarya yace "Shikenan to na amince."

Ya faɗi hakane dan auren Hameeda ba shi zai hanashi gudanar da rayuwarshi yanda ya so ba, wani irin daɗi ne ya kasheta da fara'a tace "Yawwa ɗan mamanshi, je ka yanzu bari na kira

mahaifiyarta na faɗa mata."

Juyawa ya yi ya fice ta bishi da kallo musamman ma ƙugunshi dake ɗauke da saɓulallen wando irin na gayu. Ɗaukar wayar tayi ta dannawa Ardiya kira dan ta ji yanda za su ƙarke.

*Wajen* Saleema kuma ganin sun zagaya ta inda jiya ta kama Nafissa da Mu'awwaz yasa ta faɗin "Wai a cikin gidan yake dama?"

"E, nan baya ɗakinsu ya ke." Da mamaki ta sake kallonta sai kuma ta maida hankalinta kan ƙofar da Nafissa ta tura suka shiga ciki, mangaza (store) ne na ajiyar kayan abinci da sauran abun buƙata, kallo ta dinga yi har suka ratsa kayan Nafissa ta bubbuga wata ƙofa, daga ciki ta ji muryar dattijo da za ta iya kira da tsoho aka ce "Shigo."

Tura ƙofar Nafissa ta yi ta shiga da sallama, Saleema da al'ajabi da kuma tunani suka mamayeta a lokacin a ƙasan maƙoshi ta furta "Assalama alaikum."

Tun daga bakin ƙofa ta ke kallon ɗakin, ba wani datti a ɗakin dan aikin Nafissa ne kula da ɗaki, sai dai yanayin da ta ga tsohon, bayan ga manyanci ga rashin isassar lafiya, sai ya ba ta tausayi lokaci ɗaya. Ƙarasawa su ka yi Saleema ta tsuguna ta na kallon tsohon da ya rame sosai, maganin Nafissa ta bashi kamar yanda take bashi kullum, saida suka gama har za su fita Saleema ta kalli tsohon ta ɗan riƙe hannunshi tace "Baba, kana jin daɗin zama a nan kai kaɗai kuwa? Sai na ga shiru ya yi yawa wurin."

Murmushi ya mata irin murmushin nan da ake ce ma na babba da yaro, girgiza kai ya yi alamar sam baya ji, amma kuma a bakinshi sai yace "Ina ji ƴata."

Ita ma murmushin ta mishi, dan ko ya fita shekaru zai iya ninketa ta bai-bai, ta ɗan karance-karance wanda ta hakan za ta iya fahimtar sigar kowane kallo indai ta lura da kyau, jinjina kai ita ma tayi alamar shikenan kawai sannan ta saki hannunshi suka fita a ɗakin. Suna hanyarsu ta shiga ta kalli Nafissa tace "Ta ya za su bar tsohon nan a bayan gida? Bayan gidan ma a ɗakin ajiye kayan abinci? Haba dan Allah."

Cike da jimami ta girgiza kai tace "Ko da na zo gidan nan a nan na same shi, kuma ni na ke bashi magani kullum."

Daf da ƙofar shiga falon suka haɗe da shi, faɗuwar gabanta da kauce masa dan wuce a tare suka gudana, amma sai ya tsaya a hanyar bai da niyyar wucewa ko kauce musu, harara ta dalla masa ta juya da niyyar barin wurin gaba-ɗaya har ya tafi ta dawo, amma ta na juyawa ruff! Ya damƙo hijabinta wanda hakan ya tilasta mata tsayawa ta juyo, takowa yayi ita ma ta shiga ja baya tana jan hijabinta da faɗin "Ka ga malam sake min hijabi."

Nafissa na ganin ya gusa a hanyar ta yi saurin shigewa ciki, ganin ya na biyota kuma ya ƙi sakin hijabin yasa ta nuna ɓacin ranta sosai a fuska tace "Sake min hijabi na ce." Ta faɗa tana fizge

hijabin, ƙwayar idonshi ta kalla ta nunashi da yatsarta manuniya da sigar gargaɗi da fushi tace "A rayuwata ban taɓa tsintar kaina a yanayi na fushi ba sai da na zo gidan nan, idan ka na son na ci gaba da girmamaka matsayinka na wanda ya fi ni shekaru, to ka kiyaye yi min watan-gaririya da mutumcina, dan kimata ba abar wasarka ba ce, idan kuma ka ci gaba to zan nuna mata abin da mahaifiyata ta ce na yi wa duk wanda ya kawo min wargi game da mutumcina... Ka fahimta?"

Kashedi ta ke masa! Gargaɗi mai lasisi ta ke buga masa! Amma wani farin ciki da daɗi irin na bugawa a mujalla ya ke ziyartarshi a tsayen nan, tabbas ba kyakyawa ba ce kamar ƴan uwanta, amma rufaffen jikin nan da kamalar fuskarta, sun fi mi shi *lu'u lu'u* haske da sheƙi. Tsintar kansa ya yi da sakin murmushi ya zuba hannayenshi a aljihun ɗamammen wandonshi da ya dace da shi ya na ci gaba da kallonta, cikin sanyayyar muryar da bai san ya yi magana da ita ba yace "Na faɗa miki ina son ki, me ki ka ce?"

Wata harara ta wanka masa tace "Ni? Allah ya tsareni, me zan yi da kai?"

Murmushi ne ya suɓuce masa tare da ɗan sunkuyar da kan shi, yo in ba haukan yarinyar nan ba, shi ne za ta ce me za ta yi da shi? Ta dubeshi da kyau mana, ko ƴar uwarta Hadeeya ba ta fishi jar fata ba duk da ta na mace, a haka ma dawowarsa ƙasar nan ne rana ta fara lalata masa fata, sannan ya na da ilimi da kuɗi, to me take nema a jikin namiji? Da ba za ta samu a wurinsa ba.

Hijabin da ke jikinta ya nuna da yatsa yace "Me ya sa ba kya cire wannan abun ko dan ki huta?"

Murguɗa masa baki tayi tace "Saboda shi ne mutumcina."

Kallon tuhuma ya mata yace "Me ye mutumcin gaba-ɗaya?"

Cikin ido ta kalleshi tace "Shi ne kimata."

Taɓe baki yayi yace "Me ye ita kimar ke nufi?"

Numfashi ta feso ta ƙanƙance ido tace "A wajena kimata ita ce madogarata."

Da mamaki na fasahar harshen yarinyar yace "Madogara? Me ye ita kuma?"

Ba tare da shayin komai ba tace "Aƙidata."

Tsareta ya yi da ido kamar ba zai yi magana, dan abun da ya fahimta ba za ta rasa abun faɗa ba, sai kuma ya numfasa yace "Me aƙidarki ke nufi?"

"Addinina." Ta faɗa kamar dama jira take ya sauke maganar ita ta ɗauka, da mamakin amsarta ta ƙarshe ya nunata daga sama har ƙasa yace "Idan na fahimce ki dai-dai kina so ki ce ke

karan-kan ki ke ce addinin?"

Da sauri ta girgiza kai tace "A'a, ba ni ba ce, nufina a nan shi ne, duk wani da yake amsa sunan musulmi, to ya kamata q na ganinshi gaba-ɗayansa a ga musulunci, a tattare da musulunci kuma akwai, imani da tauhidi."

Girgiza kai yayi yana murmushi yace "Maganarki nan fasa min kai take, na fahimci wasu kalaman na ki amma ban gane wasu ba."

Rumgume hannayenta tayi a ƙirji tace "Ka yi imani da Allah?"

Cike da tabbaci yace "Sosai ma, ko shirka ban taɓa kwatanta yi ba."

Kallon fuskarshi tayi da ɗan jin ya birgeta ta wannan fannin sannan tace "Ka yi ƙoƙarin tsayawa a kan wannan saiɗarar, dan laifin shirka shi ne laifin da Ubangiji ba ya gafartawa mai yi idan har ya mutu bai daina ba, sannan ranar ƙiyama idan har ba'a samu da-idai da ƙwayar zarra na shirka a aikin bawa ba, sannan aka samu sallarsa cikakkiya, to akwai yiwuwar ya zama ɗaya daga cikin waɗanda Allah zai saka aljanna da rahamarsa ba tare da hisabi ba."

Wani kallo ya aikawa fuskarta mai cike da birgewa yace" Sallah..." Sai kuma ya sauke numfashi ya ɗan sosa ƙeya yace" Zan yi ƙoƙarin tsayar da ita a kan lokacinta, babu sallan da ke kubce min, matsalata ɗaya wasu lokuta sai lokacinta ya kusa fita ko ma ya fita na ke gabatar da ita."

Waro ido tayi tace" Subhanallah! Kasan kuwa illar da ke cikin yin hakan?"

Cike da rashin sanin babban abu ya ke aikatawa yace " Ai ina yi ba wai ba na yi bane, kawai dai..."

Dakatar da shi tayi da cewa"...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_13_

Dakatar da shi ta yi da cewa "Hakan ai babbar matsala ce, in har da gangan ka ke bari sallar sai lokacinta ya wuce, to ya za ka ji idan aka ba ka tabbaci wannan sallar da ka yi ba a kan lokacinta ba Allah ba ya karɓa?"

Ɗan buɗa baki ya yi da yanayin mamakin nan sai kuma ya yi murmushi yace" Danƙari, da an samu matsala babba ai."

"Dan haka sai ka kiyaye." Jinjina mata kai yayi da fara'a yace "Zan kiyaye."

Ɗan murmushin yaƙe ta mishi ta raɓa za ta wuce, da kallo ya bita yace "Nagode."

Juyowa ta yi tace "Akan me fa?"

Da murmushi a fuskarshi yace "A kan komai ma."

Ɗaga girarenta tayi sama sannan ta yi shigewarta, sai da ya ga shigarta kaɗai ya kama gabanshi shi ma ya na jin yarinyar na ƙara shiga gaba-ɗaya zuciyarsa, ruhinsa da ma gangar jikinsa.

Bayan sun gaisa sosai a tsanake ta fara da "Ƙawata, dama wata shawara na ke so mu yi da ke, ban sani ba ko za ki yi amanna da abin da na zo miki da shi."

Duk da ba gabanta take ba amma fuskarta a sake tace "Haba ƙawata, ai tsakaninmu babu haka, ki faɗa ko ma menene ni na san zan amince, saboda ra'ayinmu na zuwa ɗaya a mafi yawancin lokuta."

Numfasawa amarya tayi tace "Hakane, dama Mu'awwaz ne ya nuna sha'awarsa ta son auren Hameeda, shine na ce ya bari na fara tuntuɓarki da maganar, dan na san burinki a kan yaran nan, ba yanzu ki ke so suyi aure ba har sai sun cimma wani matsayi na rayuwa, amma na ce ya bari yanda mukayi sai ya ji."

Wani daɗi ne ya ziyarci Ardiya har saida ta dafe ƙirjinta ta waina ido tamkar ta na gaban mijinta cike da farin ciki tace" Haba ƙawata, wannan abun arziki har sai kin nemi shawarata? Kai tsaye fa kina iya turowa a nema masa aurenta, ai Mu'awwaz ɗana ne kamar yanda Hameeda ta ke ƴarki, duk so na burina kuma in dai a kan ki ne ai zan iya ruguje shi, sannan fa karki manta Mu'awwaz yana da ilimi sannan ya san mahimmancin boko da ribar da ke cikinta, ina da tabbacin ba zai hana Hameeda ci gaba da karatunta ba."

Da farin ciki amarya tace"Tabbas haka ya ke ƙawata, ai ko bai tsaya mata ba ni mai taimaka ma ta ce a kan karatunta har mu ga ta tsaya da ƙafafunta, kuma na ji daɗi sosai, hakan na nufin zumuncinmu zai ɗore ta hanyar sake zama surukan juna."

Da haka sukayi alƙawarin sanar da mazajen na su idan suka dawo sukayi sallama kowace ranta fess tamkar an mata bushara da aljanna, domin kuwa burikansu ne za su cika ta hanyar haɗa auren nan na *ƙwarya* ta bi *ƙwarya*. Ardiya a ganinta nasararta ce kuma sa'ar ƴarta ce samun namiji kamar Mu'awwaz, matashi mai matasan shekaru, ga kazar-kazar da birgewa, ga shi kuma ɗan babban gida, a ko ina Hameeda ba za ta ji kunyar nuna mijinta ba musamman a cikin ƙawaye.

Tana kwance kan doguwar kujera ta gama waya da Mamanta tana ɗan wasa da wayar Nafissa ta fito daga madafa ta tsuguna gaban Hajia Rabi tace "Hajia na idar, ki kawo saƙon."

Fuskarta ba yabo ba fallasa ta jawo ƙaramar jakarta a gefenta tace "Yawwa, har kin gama duka?"

"E." Ta faɗa a ladabce, kuɗi Hajia ta fito da su ta bata tana faɗin "Yawwa gashi, kuma dan Allah ki yi sauri ki dawo, sannan ki shiga ɗakina akwai rigata wacce aka kawo ranar da ta yi yawa a

wuya, ki kai masa sai ya rage min ita."

"To Hajia." Ta faɗa tana miƙewa ta yi hanyar ɗakin, jim kaɗan ta fito hannunta riƙe da leda, Saleema na ganin haka ta aje wayar ta tashi zaune tace "Mama zan iya zuwa tare da ita?"

Kallonta tayi ta kalli Saleema tace "Me ya sa za ki tafi tare da ita? Wajen mai ɗinki ne za ta je."

Amariraice tace "Mama na gaji da zaman ne ni kaɗai, kuma ai na ga ba ƙasa za ta tafi ba."

Ba wai dan ranta ya so ba tace "Shikenan, tashi ku tafi, amma kar ku jima." Dan ita a ganinta ƴar aiki ba tsararta ba ce da za su fita har su jera tare a gansu. Cike da zumuɗi Saleema ta shiga ɗakinsu ta ɗan fesa turare sannan ta ɗauki hijabinta kalar ruwan ƙasa mai hannayen roba da hula mai kallabi, tsaf ta ɗaure abunta a baya inda a baya kuma har ƙasa ya ke ja idan ta na tafiya saboda tsayi, fitowa tayi ba tare da ɓata lokaci ba suka kama hanya dreba ya ja su zuwa shagon.

Ganin irin tafiyar da aka yi yasa Saleema kallon Nafissa tace "Wai yanzu tun daga can su Hajia ke kawo ɗinki har nan?"

"E, ya yi nisa ne?" Nafissa ta faɗa tana kallonta, girgiza kai tayi tace "Gaskiya akwai nisa, wannan ya za su yi idan mai ɗinkin ya saɓa musu alƙawari? Sai a yi ta kai da kawowa kenan?"

Dariya Nafissa ta yi tace "E to gaskiya sai na ce mi ki ba'a saɓa musu alƙawari, bai taɓa min ɗinki ba bare na bayar da shaida, amma dai daga yanda Hajia babba da Hajia ƙarama suke sa ni zuwa karɓo musu ɗinkinsu, ya tabbatar min da shi ɗin mai alƙawari ne, dan ban taɓa zuwa ya ce bai ida ba, shiyasa ba na zuwa da fargabar abin da zan tarar."

Jinjina kai Saleema tayi ta ɗan maida dubanta ga titi. Dammmm! Ta ji gabanta ya yanke ya faɗi, da sauri ta wara idonta a ƙofar da tunanin ko wani abu ne ke faruwa a wajen, sai dai ba abin da ta gani kuma ba ta ga fuskar da ta sani ba, a hankali ta sulale ta jingina kanta a madubin ƙofar ta na ci gaba da kallon hanya, a can ƙasan zuciyarta kuma a nutse ta ke jin gabanta na ci gaba da bugawa zuciyarta kuma na harbawa a tsanake. Nauyayyar ajiyar zuciya ta sauke ta lumshe ido tare da furta "Hasbunallahu wani'imal wakil, La'ilaha illa anta subhanaka inni kuntum mina zalumin!

Daga cikin kwana dreban ya faka motar suka fito saboda rashin sarari a inda shagon yake, hakan yasa suka ɗan tako a ƙafa suka tsallako titi, daf da titi shagon yake ga kuma samari da ke zaune ƙofar shagon da alama ma har da maɗinka, amma a haka kuma gida na kallon shago sai ƙaramin masallaci a gefen gidan, Nafissa ce ta kalli samarin da ke zaune tace "Sannunku."

"Yawwa Sannu." Suka amsa mata, ƙarasawa sukayi da sallama a bakunansu suka shiga ana amsa musu. Ɗan tsayawa ta yi tana sake buɗa idonta dan tabbatarwa kanta abin da take gani,

tabbas dai shine tunda gashi shima ya mata kallon sani duk da ya ɗauke kanshi kamar wanda aka tsorata, dogon bencin da ke cikin shagon ta zauna kamar yanda Nafisa ta zauna ta na faɗin "Ina wuni malam Huzeifa."

Taushin muryarshi da yanda ya amsa ba wani sakin fuska da irin rahar nan ta samari ya sa ta ɗan saci kallon fuskarshi, kan gemunshi ta sauke ido da ke baƙi-ƙirin ya masa kyau a fuska duk da duhun fatarshi, ta na ji Nafissa na tambayar an ida, da sigar ban haƙuri yace "Ki ɗan yi haƙuri kaɗan Nafissa, shi na ke ƙarasawa yanzu, idan akwai in da za ku je za ki iya tafiya sai ki dawo."

"A'a zamu jira, ba in da za mu je." Ta faɗa tana gyara zamanta, jinjina kai ya yi yana rintse idonshi da ƙarfi sosai, to fa a dole zuciyarshi da sheɗan ke son fizgar idonshi ya kalli yarinyar da fitina ce kallonta a wurinshi, shiyasa ba ya so ya kalleta bare ya ji irin abin da ya ji ranar, dan ya fahimci abun a jikin *wannan kaɗai ya ke ji*, dan suna haɗa ido farkon shigowarta gabanshi ya faɗi tsikar jikinta ta yamutsa.

Shiru shagon ya ɗauka, Saleema ƙarewa komai na shagon kallon take, ji take ina ma tana ɗaya daga cikin maɗinkan shagon nan, garin kalle-kallen har ta juyo da kanta ta sauke a kan shi ya na ɗinkinshi a nutse da tela ta lantarki da ko ƙararta ba'a ji sosai. Ba tare da saninta ba ta saki baki cike da birgewa take kallon yanda ya ke ɗinkin ta na jin kamar ta ƙwawa masa *BAIWARSA*.

Tunda ya lura shi take kallo jikinshi ya ɗauki makyarkyata yake ji ina ma yana da ƙarfin halin da zai iya kallonta yace "Dan Allah sarara min haka, kawar da idonki a kaina."

Sai dai jikinshi ɓari yake sosai ta yanda idonshi suka fara disashewa yana neman yin abin da bai dace ba a ɗinkin mutane, Allah ne ya ji tausayinshi ta hanyar jefo ɗaya daga cikin samarin da ke zaune ya na faɗin" Sannunku."

Da sauri ta juyo sai kuma ta ɗauke kanta jin Nafissa ta amsa masa har suna ɗan hira yasa ta sake maida hankalinta gareshi ta na kallon aikin da yake, cike da tsokana matashin nan yace" Ustaza ba gaisuwa? Da alama sarauniyar jan aji ce ko?"

A hankali ta juyo ta kalleshi sai kuma tace" Sannu." Kawar da kai tayi tana yatsina fuska, hakan yasa matashin faɗin" Sai da na roƙa? Wai me yasa ƴan matan yanzu ba ku san gaishe da mutane idan kun gansu?"

A take yanayinta ya nuna sam ba ta jin daɗin takuratan da yake neman yi, ta nutsu tana kallon abin da ta jima ba ta yi ba kuma take kwaɗayi, amma sai wani canzen iska yake mata.

Cike da jin haushi tace "Ciwon kawunanmu ne mu ka fara sani, ta ya kawai za mu yi arhar da maza zaune a titi za mu wuce sai mun gaishesu? A cikin can akwai Yayana ne? Ko akwai Kawuna a ciki? Ko kuma Baffa na? Ba ko ɗaya? To a kan me sai na bayyanar da al'aurata

gareku dan na birgeku?"

Irin a ɗan zafafen nan ta ɗauke kanta daga gareshi, karaf! Suka haɗa ido da Huzeifa da ya dakata da ɗinkin yana kallonta da mamakin dama akwai ƴan mata ma su irin wannan tunanin? Ganin sun haɗa ido a tare suka kawar da dubansu kowa na ɗan ƙyafta ido, matashin ya kalla ya wanka masa harara mai cike da gargaɗin da ya fahimta ya kuma juya ya fice a shagon.

Kallonshi Saleema ta sake yi cikin nutsatsiyar murya da taushi sosai tace "Malam, am... Na ce, a nan kuna koyar da ɗinki ne?"

Kallon fuskarta ya yi yana mamakin ashe dai ta ganeshi? Ya ɗauka ta manta shi shiyasa shi ma yayi kamar bai ganeta ba, a hankali ya fara girgiza mata kai sannan ya maida dubanshi ga aikinshi yace "A'a, ba ma koyarwa."

Cikin sigar rarrashi tace "To amma ai kai ka iya ɗinki, ba za ka koya min ba? Ina son koyon ɗinki sosai."

Wani *sahibin* kallo ya aika mata yace "Kin taɓa koya ne a wani waje?"

Cike da zumuɗi Saleema ta gyara zama tace "Na taɓa koya amma tun ina yarinya, amma kuma ban manta abubuwan da na koya ba, sai dai shekara takwas kenan yanzu, ina buƙatar koyon irin ɗinkin zamani."

Wani malalacin murmushi ya yi a ganinshi wannan ɗin mai kama da ƴaƴan masu kuɗi, ita ce za ta koyi ɗinki? Ganin bai kulata ba ya ci gaba da abin da yake ya sa ta ƙara cewa "Malam, ka faɗa min ko na wa ake biyanka sai na biya ni ma ka koya min?"

Kallonta ya sake yi ba ko ƙyaftawa, a kunyace ta sadda kanta ƙasa da mamakin kallon me yake mata haka? Nan ma dai bai amsata ba, dan haka ta ɗaga idonta tare da wanka masa harara... Sai dai tana fara hararan na shi na jin haushin ya ƙi kulata caraf suka haɗa ido, da sauri ta juya kanta tana kallon titi cike da kunyar kamata da yayi.

Nafissa da tunda suka fara magana ba ta tanka mata ba cewa tayi "Haba malam Huzeifa, ba za ka koya mata ba?"

A hankali ya girgiza kai ba tare da ya kalleta ba yace "Ba na koyawa mata ɗinki."

"To amma me yasa?" Cewar Saleema da sauri tana juyowa, satar kallonta yayi da tunanin wai me zai yi da za ta fahimci ba ya son suna doguwar hira ne? Ta kasa gane akwai wani abun al'ajabi a cikin nutsatsiyar muryarta wanda yake sa wa gaɓɓan jikinshi na amsawa zuciyarshi na dokawa da sauri, tsoro ya ke kar ya biyeta su dinga zancen ne har ya kauce ƙa'ida. Kura masa ido da tayi alamu ne na amsarshi take jira, a hankali ya ɗauke dubanshi daga gareta cikin

sanyayyar murya kamar wanda ba ya da lakka yace "...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_14_

A hankali ya ɗauke dubanshi daga gareta cikin sanyayyar murya kamar wanda ba ya da lakka yace "Haka kawai."

Ɗan taɓe baki tayi ta kalli Nafissa da ke faɗin "To amma ai za ka iya fara wa da ita."

Ko kallon Nafissa bai yi ba ya ci gaba da aikinshi dan ba zai iya abin da suke buƙata ba, sun ɗauki mintin da ya kai goma zaune wata mace ma ta zo karɓan ɗinkinta, a mutumce ya gaishe da matar da kuma alamar sani a tsakaninsu, kujerar da ke gaban wata tela ya nuna mata yace "Zauna ko, bari a ɗauko kayan."

Zaune tayi shi kuma ya leƙa ta tagar da ke gabanshi wajen samarin dake zaune yace "Kai zo nan."

Jim kaɗan matashin nan na ɗazu ya shigo yace "Gani."

Kallonshi yayi yace "Ka ɗauko kayan Hajia."

Ƙarasa shiga shagon ya yi ya buɗa drower da suke aje kayan, a sauƙaƙe ya ɗaukosu tare da ɗaukar leda ya saka a ciki ya bata, godiya ta yi ta fita shi ma saurayin zai fita Saleema tace "Kai ma ka iya ɗinki?"

Kallonta ya yi yana dariy yace "Sarauniyar jin kai, ɗinki ai a jininmu ya ke, a nan shagon Babana ya rasu, yanzu haka idan kika shiga gidan can za ki samu ƙannaina suna yanka wasu ɗinkuna ko suna gamewa, yayin da ƙanena ke saka mana duwatsu idan akwai buƙatar hakan."

Kallon gidan da ya nuna mata tayi tace" Can ne gidan na ku?"

Ɗaga kai yayi yace" E."

Da sigar tausayi tace" Allah sarki, Allah jiƙan Babanmu."

Da fara'a ya amsa da" Ameen. "

Huzeifa kuma saida ya kalleta sanda ta ce *Babanmu*, ko a ina kuma ya za ma na su? Amma ko ba komai girmamawarta ga na gaba da ita ya birgeshi, uwa uba yanda ta kwatanta tsohon wasu da na ta, har matashin zai fita tayi saurin faɗin" Ba ka ji ba?"

Tsayawa yayi yana kallonta, a ɗan kunyace tace" Dama ina da sha'awar koyon ɗinki ne, ko zan iya koya a wajenku?"

Cike da lura ta fahimci ya kalli Huzeifa, sai kuma ya kalleta yace" To ki yi magana da babban Yaya, idan ya amince ba damuwa."

Da sauri Saleema ta juya ta kalli Huzeifa da za ka rantse ba ya gane yarensu, dawo da kallonta tayi ga matashin tace" Yayan ka ne?"

Ɗaga kai ya yi yace" E, shi na ke bi wa, shi kuma shi ne babba a gid..."

Ɗan gyaran muryar da Huzeifa ya yi ya ankarar da shi ya kalleshi, rufe baki yayi da tafin hannu yace" Yi haƙuri Yaya."

Ficewa ya yi a shagon hakan yasa Saleema juyawa ta kalli Huzeifa ranta ɓace kamar ta ce" Wai me ye matsalarka?" Sai dai sam babu fuska a tare da shi bare ta yi maganar.

Yanzu kam ba wani jimawa ya gama ya miƙe tsaye, cikin drower ya ɗauko sauran an gogesu tsaf ya haɗa da wanda ya ida ya saka a leda, miƙawa Nafissa ya yi yace" Gashi, dan Allah ki basu haƙuri na jinkirin da aka samu."

Karɓa Nafissa tayi tace" Ba komai, ga ragowar kuɗin." Ta faɗa ta na miƙa mishi, karɓa ya yi ya sa aljihu yace" Ki musu godiya."

Miƙewa sukayi suka fita a shagon, Saleema ba ta sake juyowa ba bare su kalli juna, shi kuma yana tsaye har suka tsallaka titin suka shiga kwanar da mota ke jiransu yana kallon hijabinta da ke taɓa diga-diginta duk in ta ɗaga ƙafar, saida suka ɓace mi shi ya koma ya zauna kan kujera yana godiya ga Allah da ya bashi damar cika alƙawarin da ya ɗauka na ɗinkin nan tunda ga shi har ya kammala ya bayar.

*Suna* isowa kai tsaye ɓangaren suka tunkara, daf da za su shiga motar Alhaji Auwal ta danno kai cikin gidan, dakatawa Saleema ta yi yana gaba biyu daga cikin mutanenshi na bin shi a baya, tarbanshi tayi cike da ladabi tace "Sannu da zuwa Abba."

Da fara'a sosai ya amsa da "Yawwa sannu Baby, ya gidan?"

Cike da kunya ta amsa da "Lafiya lau Abba, ya aiki?"

Cikin jin daɗi ya amsa da "Aiki da wahala yarinyata, amma tunda na dawo gida yanzu zan ɗan huta."

Murmushi tayi tace "Allah ya baku ladar ɗawainiya da mu."

Jim ya yi yana kallonta kamar mai son gano wani abu a fuskarta, sai kuma ya jinjina kai yana murmushi yace "Ɗawainiya da ku Baby ai dole, iyalinmu ne ku fa."

Ganin ba ta da niyyar shigewa ciki yasa ya nuna mata yace" Mu je ko."

Nuna masa hanyar bayan gida ta yi cike da son karkato hankalinshi tace" Abba zan je na ga Papi ne."

Ɗan zabura ya yi kamar wanda ya manta da tsohon, sai kuma ya mata murmushi yace" To

shikenan, ni ma zan shiga yanzu na gansu idan na yi wanka."

Jinjina kai tayi alamar to ta juya ta nufi bayan gidan, shima ƙarasa shiga ya yi ya samu Hajia Rabi na mitar ina Saleema ta tsaya, shi ne ya bata amsa" Ta shiga wajen Baba ne za ta ganshi."

"Baba kuma?" Ta faɗa da mamaki kafin ta ɗora da "Me ya sa ba za ta zo ta huta ba?"

Taɓe baki ya yi alamar bai sani ba ya nufi ɗakinshi, fitowar amarya daga ɗakinta ne ta kalli Hajia babba tace "Kamar Alhaji na ji ya shigo?"

"E, ya shiga ciki." Ta bata amsa ba yabo ba fallasa, dan tsakaninsu ba wani shaƙuwa ba ce tsakaninsu da ake ma juna dariya ko sanin sirrin juna, ganin ta nufi ɗakin yasa ta faɗin "Ga kayan nan an karɓo daga ɗinki."

Da fara'a ta dawo da baya tana faɗin "Dukansu kuma?"

"Um." Ta amsa mata tana zama kan kujera, kayan ta buɗa ta shiga dubawa tana cewa "Kai! Gaskiya Huzeifa ya na da kirki, kin san ban ɗauka zai gama aikin nan a ɗan lokacin nan ba?"

Ɗan murmushi kawai tayi tace "Ai ya wuce haka."

"Gaskiya kam, kuma ga shi kamar dai yanda mu ka faɗa masa ya mana."

Kallon ɗinkunan da hirar da suke taɓawa musamman kan bikin da za'a yi jibi wanda kayan shigar bikin ne na yasa har Alhaji Auwal ya fito ba ta sameshi da maganar da ta yi niyyar zuwa su yi ba, dan ba za ta bari ta yi sanya ba, dole ta daki ƙarfe da zafi-zafinshi.

Juyawa sukayi a tare suka kalleshi yana fitowa sanye da doguwar riga, cike da kissa da kwarkwasa amarya ta shagwaɓe fuska tace "Baby, shi ne ka fito ba ka jirani ba? Gashi kuma ina son magana da kai."

Ɗan murmusawa ya yi yace "To ai ba guduwa zan yi ba, wajen Baba zan shiga, tun jiya rabona da su."

Hanyar fita ya kama ta bishi da kallo cike da jin ƙarfin gwiwar tabbas zai amince da abin da za ta zo mi shi da shi.

*Ya na* zuwa ya samu Saleema da mahaifinshi a ɗakin suna ta hira da dariya, da mamakin irin dariyar da take ya ƙarasa yana zama bakin gadon yace "Me ki ke ma dariya haka?"

Wata dariyar ta ƙyalƙyale da ita ta nuna tsohon tace "Wallahi Papi ne ya ke ta cika min ciki da dariya, labari suke bani."

Murmusawa ya yi ya kalli mahaifin na shi yace "Baba, ya jikin na ku?"

Cike da tsantsar ƙauna da kulawa dattijon ya amsa da "Alhamdulillah Auwalu, ka na lafiya?"

A tausashe ya amsa da "Lafiyata lau Baba, ka ci abinci?"

Cikin sarƙaƙƙiyar murya yace "Ban ci ba, amma kai ka ci ne?"

Da alamar damuwa da tambayar mahaifin na shi yace "Baba, sai ka dinga min tambayoyi kamar wani ƙaramin yaro, hakan ya sa wasu lokuta bana son mu haɗu."

Shiru dattijon ya yi sai kuma a sanyaye sosai yace "To ka yi haƙuri, na saba ne idan ban tambayeka ba bana jin daɗi."

Da sauri Saleema ta katsesu ta hanyar dafa hannun dattijon tace "Papi, na kawo ma ka abincin ne?"

Ɗaga kai ya yi alamar e, miƙewa ta yi Alhaji Auwal yace "Ki haɗo da maganinshi."

Jinjina kai ta yi ta kama hanyar fita, ta na buɗewa Nafissa na shigowa ɗauke da abincin, karɓa ta yi ita kuma ta koma dan wasu ayyukan. Dawowa ta yi ta zauna ta zuba da kanta sannan ta ɗago ta miƙowa Alhaji Auwal da ke shirin tashi ya tafiyarsa, kallonta ya yi da alamar jiran ƙarin bayani yace "Uhum?"

Saida ta yi takwaf-takwaf da fuskarta cike da sigar ladabi da biyayya a tausashe sosai tace "Abba, na yau kawai ka ba wa mahaifinka abinci da hannunka, a shekarun nan na shi zai yarda ka ciyar da shi ne ta hanyar bashi abinci a baki kamar yadda ya baka kana yaro, ba wai ta hanyar saka mai aiki ta dafa ba sannan ta kawo masa ya ci, na san an ɗauki shekaru rabon da ka ji shauƙi na mahaifi na fizgarka, ka fizgo wannan shauƙin ko hakan ya sa ka tuna da mahaifinka na buƙatar kulawarka, *kai kaɗai kawai* ya ke da buƙata."

Sadda kanta tayi ƙasa ta saki murmushi tace" Abba, ka na damuwa saboda yawan tambayarsu gareka, ba komai ya kawo hakan ba sai *soyayyar mahaifi ga ƙaramin ɗansa*, shi a wajenshi har yanzu kulawarsa ka ke buƙata, ba zai zama cikakken mahaifi ba idan har ya na nauyin baki wajen tambayar abin da ya shafi lafiyarka, harkokinka, farin cikinka da ma damuwarka, sannan abun farin ciki ne yau a rayuwa a ce kana da wanda ya damu da kai, Abba, wallahi duk soyayyar da iyalin nan na ka suke taƙamar suna maka bai kai rabin soyayyar da bawan Allahn nan ya ke maka ba, hatta da ƴaƴan da ka haifa..."

Tunda ta fara maganar alamun komai na ratsashi ne ya bayyana a tare da shi, dan jikinshi yayi sanyi kuma kanshi a ƙasa yake sai dai wani lokaci ya kan ɗago ya kalli mahaifin na shi da alamar jin kunya, amma yanzu da ta ce wai har yaranshi sai yasa ya kalleta da mamaki, kamar

ta san me kallon ke nufi sai kuwa ta ce "E Abba, soyayyar da yake maka ta fi wacce suke maka, sai dai idan muka kalla a zahiri shi ya na sonka ne saboda shi ya haifeka, su ma kuma suna sonka ne saboda kai ka haifesu, ba fata na ke maka ba Abba, a yanzu ba na jin akwai wata larura da za ta saka tsohon nan ya gujeka, amma yanzu Mu'az ko Mu'awwaz da za ka hanasu auren wacce suke so, to fa idan ba Allah ya shirya maka su ba, tsaf za su bijire maka a kan mace, kenan soyayyarsu ba haɗi da ta wanda ya kawoka duniya."

Burinta bai wuce kar ya ga zaƙewarta ba, ba ta so su ga ta cika shiga shirgin da ba na ta ba, sai dai kuma akwai kurakuren da take ganin ya kamata su gyarasu, saida ta ɗan faɗaɗa murmushi a ladabce tace" Dan Allah Abba kar ka fahimceni ba daidai ba, na yi magana ne saboda girma da mahimmancin iyaye garemu, idan har shi kaɗai ya rage maka a rayuwa, ya dace ka ɓata ɗan sauran lokacin da ya rage maka wajen kula da shi, duk rayuwarsa ya ɓata ta ne wajen kula da kai, a yanzu da ya kawo ƙarfi yake kuma neman tallafi, kulawarka kaɗai yake buƙata, duk abin da ka ke nema da yake ɗauke maka hankali daga nesantar mahaifinka, ba zai zama mai albarka gareka ba saboda mahaifinka ba ya farin ciki da halin da ka ke sakashi a ciki.."

Sai kuma ta kalli tsohon da ya ƙureta da ido ya ma rasa akan me zai auna yarinyar, cikin kulawa tace" Papi, ko kana farin ciki da zaman wurin nan kai kaɗai?"

Da sauri Alhaji Auwal ya kalleshi da son jin amsar da zai bayar, shi ma kallonshi ya yi da tunanin ko ya masa kara? Sai kuma ya sunkuyar da kanshi ƙasa saboda ba ya so ya sosa ranshi ko kaɗan, wani murmushi Saleema ta yi mai ciwo ta kalli Alhaji Auwal tace "Wani shirun ma amsa ce."

A hankali ta rusuna ta aje farantin abincin sannan ta miƙe tsaye tana kallon Alhaji Auwal tace "Idan har ka yi yaƙi sheɗan kuma ka yi nasara, to na san za ka yi abin da ya dace kan lamarinshi, sannan za ka ci gaba da yi har sanda mai rabawa za ta rabaku kuna mai cike da alhini da ƙaunar junanku."

Idonta cike da hawaye ta matso kusa da Alhaji Auwal ta ɗan riƙe hannunshi tace" Abba, kafin kai ko shi wani ya bar duniya, ya kamata ya shaida arziƙi da ikon da Allah ya baka ta sanadiyar jajircewarshi a kan ka har ka zama hakan."

Juyawa ta yi ta kalli tsohon da fara sharar hawaye saboda taɓo masa ciwon da ya jima yana gwaguyarsa, cike da tsokana ta marairaice ta kama kunnuwanta tace" Ayya! Papi ya na kuka saboda na taɓa masa ɗan gudaliyarsa."

Da sauri ta riƙe hannunshi ɗaya tace" To a gafarceni ba zan sake ba, na barku lafiya."

Ta faɗa tana ficewa a ɗakin da sauri-sauri, jiki a matuƙar sanyaye tsohon ya bita da kallo yana mai saka mata albarka, ko ba'a samu canji ba aƙalla dai ta sauke nauyin da ya hau kanta na faɗin gaskiya da gyara kayanka, Alhaji Auwal kuma kanshi na sadde ya kasa ɗagawa saboda tsananin kunya da nadama da kuma ƙudirin gyarawa da ya ɗarsu a zuciyarshi yanzu yanzun

nan.

Tsugunno ya yi a gaban mahaifin na shi ya riƙo hannayenshi kanshi a ƙasa cikin muryar da ke ɗauke da amon nadama yaxe "Baba ka yi haƙuri ka yafe min, na tuba Baba ba z..."

Da sauri yace masa "Shikenan Auwalu, ya isa haka ka ji ko, ni dama ban taɓa riƙeka a zuciyata ba, saboda na san illar hakan, bana so mutuwa ta riskeni ina mai hushi da kai, shiyasa duk yanda raina ya ɓace a game da halin ko in kula da ka ke nuna min sai na yi gaggawar yafe maka."

Hannayen mahaifin na shi ya ɗago ya sumbata har sau uku sannan ya durƙusa gwiwoyinshi ya rumgumo tsohon na shi ya sumbaci wuyanshi, shi kuma da abun ya zo masa da rashin sabo sai ya ji kunya ta kama shi, rintse ido ya yi sai dai yana jin ƙaunar ɗan na shi na sake narkuwa a cikin jikinshi, ɓangare ɗaya kuma soyayya yarinyar nan ya ji ta mamaye zuciyarshi da kuma saka mata albarka. Alhaji Auwal ma albarkar ya ke saka mata tare da ba wa kansa tabbacin wannan dole ma ta zama surukar gidanshi, wata zuciyar kuma na raya mi shi ba dan ɗanshi ya rigashi ba ai da shi zai so samun wannan *zinariyar waliyiyar*, dan babu wanda ba ya son alkairi wa kansa? Amma a hakan ma idan har ta zama matar ɗanshi, to shakka babu za ta ci gaba da ɗorasu a siraɗin rayuwa miƙaƙƙiya.

Bai fita a ɗakin nan ba sai da ya ba wa mahaifinshi abinci a baki ya sha maganinshi, wani abun farin cikin kuma yanda suke hira tsohon na taɓo yarinyar Alhaji Auwal wanda shi bai san ya yi ba, wani kuma ya sani amma ya manta saboda shekaru, sai ya sake yarda da abin da Saleema ta faɗa cewa har yanzu shi a ƙaramin yaro yake kallonshi tunda shi ya haifesa, to in ba haka ba har fa labarin lokacin da ya yi bayan-gari yake bashi daga makaranta, haka ya ɗauki awa biyu suna nishaɗi kuma har zuciyarshi sai ya ji kamar ya sauke wani nauyi mai girman gaske da ya jima yana dakonshi a kai.

A farfajiyar gidan suke zaune kowa ya na abin da ya fisheshi, motar Mu'az ce ta shigo gidan ya nufi inda ake aje motocin, da gudu Hamdeeya ta tunkareshi dan tarbanshi, kamar an kirata ita ma sai kuwa ta miƙe duk da kayan da ke jikinta. Ta wutsiyar ido Saleema ta  kalleta sai kuma ta maida dubanta ga gyaran persil ɗin da take taimakawa Nafissa, har ya fito daga motar yana riƙe da hannun Hamdeeya, ita ma Hadeeya ta na ƙarasawa ta riƙo hannunshi tana kallon kyakyawar fuskarshi tace "Sannu da zuwa Yayana."

Kallonta yayi da fara'a ya amsa da "Sannu budurwata, kina lafiya?"

Farrr! Ta masa da ido alamar e, ƙare mata kallo yayi ya kanne mata ido ɗaya yace "Uhum! Kin ganki kuwa? Gaskiya kin yi kyau sosai."

Murmushi tayi tace "Dama kai na yi wa."

Da mamaki yace "Da gaske?"

Jinjina kai tayi, ɗan kallon Hamdeeya yayi ya miƙa mata wayarshi yace "Je ki ina zuwa."

Karɓa tayi da farin ciki ta juya shi kum ya kalli Hadeeya ya saki hannunta ya riƙe haɓa yace "To juya na gani in dai ni aka wa kwalliyar."

Rufe fuska tayi da tafukan hannaye alamar kunya, a haka kuma ta juya masa bayanta sannan ta juyo, daga sama har ƙasa ya ƙare mata kallo, irin ɗan guntun siket ɗin dake jikinta da rigar, ba ƙarya kayan sun mata kyau, matsowa ya yi kusanta sosai ba tare da ta ankara ba ta ji ya shafo mazaunanta cikin wani irin yanayi yace "Gaskiya ƙanwata ke babbar yarinya ce..."

Da sauri ta kalleshi amma yanda ya yi narai-narai da ido kamar zai yi kuka yace "Ba ki ban amsa ba har yanzu, ko dai..."

Sai kuma yayi shiru ya jawo hannunta gaba-ɗaya ta faɗa ƙirjinshi ya tsare fuskarta da kallo, kallon fuskarshi ita ma take tana ganin idan fa ta samu guyen nan ba ƙaramin kamu ta yi ba, masha Allah son kowa ƙin wanda ya rasa, ga wata ƙasumba da gemu irin na ƴan zamani da ya ma fuskarshi ƙawanya. Da sauri ta dawo hayyacinta sanda ya sake faɗin "Ina jinki mana cheri, ko dai ban miki ba ne?"

Lumshe idonta tayi tana tantance ƙamshin me ye bakinshi ke fitarwa? Inibi ko tuffa? Take sheɗan ya saka mata wani tunani cewa "To ai dan ya taɓani ba wani abu ba ne, wayewa ce kawai, kuma da babu kyau ai da Mamanmu ba ta yi a gabanmu ba ita da Abbanmu, dan haka ba komai ba ne, kuma ma ai so na yake shine zai aureni, dan haka ba komai a ciki."

Ta na gama wannan tunanin ta buɗe manya kuma fararen idonta ta sauke a cikin na shi, ba tare da tunanin komai ba ta zubar da ajinta ta kai laɓɓanta a kan kumcinshi ta sumbata, sai bayan ta yi ne kuma sheɗan ya bijiro mata da wata kunyar ƙara durmiyata halaka sai ta rufe ido da sauri ta jaye jikinta ta ruga a guje. Da kallo ya bita bayan ya ɗora hannunshi inda ta sumbata ya saki wani shaƙiyin murmushi, a zuciyarshi ya furta "Tukuna ma, sai ranar da kika fara tatso min madarar da ke addabata da bakinki."

A hankali ya shiga takawa har ya isa inda bai tsammanin samun mutane, amma sai ya samu su Saleema zaune suna aiki, Nafissa ce tace "Ina wuni Alhaji."

Ɗaga ido tayi ta kalli Nafissa cikin raɗa tace "Wai Alhaji, sun je makka ne?"

Ita ma Nafissa cikin raɗa tace "Ai har autan gidan nan ya je."

Taɓe baki tayi tace "Amm..." Zabura ta yi saboda sunkuyo kanshi da ya yi daf da wuyanta kamar zai taɓata, ƙurawa juna ido sukayi Saleema na kallonshi cike da jin haushin wannan ɗabi'a ta

shi, murmushi ya sakar mata ya ƙyabta mata ido ɗaya yace "Ina sonki."

Raɓata ya yi ya wuce ta bishi da harara, tsaki ta ja sannan ta koma ta zauna, Nafissa kuma dariya ta yi ganin yanda Saleema ke ta kumbura kan wannan abu da ba komai ba ne a wajen samarin wannan gida.

Daga cikin falon Alhaji Auwal ya ƙwala ma Saleema kira, da sauri ta amsa da "Na'am."

Aje farantin dake kan cinyarta tayi ta miƙe ta shiga, tsaye duk ta same su shi da matan sun sakashi tsakiya, tana zuwa ƙasa ta durƙusa tace "Abba gani."

Kuɗin da ke hannunshi ya miƙo mata yace "Yawxa yar albarka, karɓi wannan kin ji, ku je ƴan kasuwa yanzu ku siyo labulen ɗaki mai kyau da carpet, sannan ki siyo sababin kwanuka guda biyu da ƙaramin tebur na tsakar ɗaki."

Ba ta tambayi komai ba ta jinjina kai tace "To Abba."

Saida ta miƙe sannan ta rusuna tace "Abba zan iya tafiya tare da Nafissa? Saboda dreba baya nan."

Jim ya yi kamar mai tunani sai kuma ya kalli ɗakin Mu'az sannan yace "A'a, ku je ke da Yayanki Mu'az, bana son hawa abun hawa na waje."

Tsammm! Ta kalli fuskarshi, ta ya za ta nuna masa ba ta son kusanci da *tantirin nan*? Bare har ta fita da shi waje, kamar ya san a kan me take tunani sai yace "Karki damu kin ji, ku je tare da shi kuma kar ku jima."

A sanyaye kawai ta jinjina kai ta nufi ɗakinta dan shiryawa ta fito, tana ji Alhaji Auwal na faɗawa Hajia babba ta sanarwa Mu'az za su fita yanzu.

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_15_

A sauƙaƙe ta shirya kamar dai kullum cikin shigarta ta mutumci ta fito, Hajia babba ce ta mata nuni da ƙofa tace "Mu'az ɗin na zuwa, ki jirashi a waje."

Hanyar ƙofar ta nufa inda amarya dake zaune kan kujera ta bita da uwar harara cike da takaicin wannan yarinya, ita gaba-ɗaya ma ta ga komai na gidan ya sauya tunda yaran suka zo, kuma Saleema ita ce silar komai, yanzu ma gashi Alhaji na wata banzar magana wai za'a gyarawa Baba ɗakinshi, ga wasu uwayen dokoki da ya lafta musu cewa dole yanzu wacce ta yi girki ita za ta kai masa har ɗakin da rana ko kuma a ba cikin yaran da ya haifa, na safe da dare kuma shi kanshi zai kai mishi, sannan wai kowace safiya sai sun je gaisheshi, abun da bai taɓa faruwa ba! To idan ba Saleema ba wa ye ua zigashi? Ƙiri-ƙiri ya ɗauko maƙodan kuɗi ya bata ta siyo kayan ɗakin bayan sai da ta roƙi ya bata dan ta san sauran canji za su zama na ta amma ya ƙi. Dan haka ita gwara ma su gama kwanakinsu su bar gidan, idan ba haka ba za ta kasa ɓoye ɓacin ranta har ta fatattaki yarinyar nan ta koma gidansu, dan dama uwarta ma ba wani shiri suke ba, saboda ita ma dai kamar ƴar take, amma abun mamaki uwar ma ta fi Saleema wayewa da ɗan cakarewa, dan ita tana saka mayafi musamman bikin ƙawaye, sannan ta na kwalliya ga uya ɗaukar wanka sannan ga ta kyakyawa ta fi ƴar, amma ita sai fama da hijaban da suka fi ƙarfinta, da haka ta jinjina kai da tunanin za su haɗe idan ta sake kutse a rayuwarsu.

*Saleema* kam ta ɗan jima a tsaye kafin ta hangeshi ya na tahowa, juya baya ta yi har ya ƙaraso ta bayanta yana faɗin "Matata ki gafarceni na saka ki jirana."

Buɗe mata ƙofa ya yi da kanshi yace "Shiga mu je."

Shiga ta yi ba tare da ta kula shi ba, dan niyya ce ta yi ba za ta biye mishi sosai ba bare har ya ga damarta ya kawo mata wargi, suna ɗaukar titi ya kai hannu ga redio ya kunna pm3, take sautin tattausan kiɗa ya karaɗe cikin motar, sanyayyar waƙa ce ta hausa ta soyayya ka rantse babu komai a duniya sai zallar soyayya saboda yanda baitukan suka fita. Hannu tasa ta na wasa da kuncinta saboda jin Mu'az na bin waƙar yana kaɗa kai alamar dai da a tsaye yake zai uya taka rawa ma, dan yanayinshi ya nuna hakan ba kaɗan ba, girgiza kai tayi a hankali yanda ba zai ji ba tace "Allah ya shirya."

"Ameen matata." Ya faɗa yana kallonta sannan ya ɗora da "Abinda na ke son ji daga bakinki kenan, ina ji a jikina addu'arki gareni karɓaɓɓiya ce."

Numfashi ta sauke ta kawar da kai ba ta tanka masa ba, leƙa fuskarta yayi yace "Matata, hushi kikayi ne?"

Kallonshi tayi sai kuma ta sake maida dubanta ga titi, cike da tsokana yace "Gaskiya ki saki fuskarki, yanzu idan na haɗu da abokina ta ya zan nuna masa ke da wannan haɗaɗɗiyar fuska? Ya ɗauka satoki na yi?"

A hankali ta furta "Ya Allah." Waro ido yayi yace "Lahhh! Wai har na dameki hakane?"

Yatsa biyu ya sa ya damƙe laɓɓanshi yace "Shikenan na yi shiru, idan na sake magana ki mari fuskata irin na jiya."

Da sauri ta kalleshi dan ita kam ta ma manta da ta mari fuskar nan ta shi da alamu suka nuna yana kula da ita, sunkuyar da kai tayi cike da jin kunya, dubanta yayi da kyau yace "Hajia kin san da marin nan ko kaɗan ba zafi? Shin tausayina ne ya hanaki marina da kyau? Ko kuma dai iya ƙarfinki ne?"

Ƙala dai ba ta ce masa ba, dogon numfashi ya ja yana kallon titi yace "To! Mu'az ka yi haƙuri, ita dama soyayya haka take, fatana bai wuce wanna. Babyn ta so ni kamar yanda na ke sonta, idan kuma ba haka ba..."

Da sauri ta kalleshi da ɗan jin haushin takura mata da surutu tace "Idan ba haka ba fa?"

Da hannunshi ya yi alama a wuyanshi kamar wanda zai yanka maƙogoronshi ya ɗan zuro harshe waje kamar wata dabbar da ta yi mummunar mutuwa yace "Ƙitttt! Sheƙawa zan yi."

Me Saleema za ta yi? Sai kuwa ta bushe da dariyar da za ta rantse tun da suka zo gidan nan ba

ta yi ba, dariya sosai take shi kuma yana kallonta cike da birgewa yanda haƙoranta ke jere reras farare tas, cikin dariya ta dafe ciki tace" Wallahi ka na da abun dariya."

Cike da ƙwarin gwiwa yace" Na sani Matata, dan ma baki sakin jikinki da ni, da ba ke ba zama gum."

Wani kallo ta masa tare da ɗan tsagaita dariyar tace" Ka taɓa ganin inda aka ba kura ajiyar nama?"

Tsammm! Ya yi yana kallonta, tabbas magana ta faɗa mai kyau, sai dai bai ji haushi ba tunda gaskiya ta faɗa, sai kawai ya bushe da dariya ya nuna kanshi yace" Ni ne kura?"

Wata yar harara ta galla masa tace" Ni dai ban ce ba."

Hannunshi ya kai da niyyar tallaɓo haɓarta dan ta kalleshi, wanda sabo ya jawo masa hakan ya manta da wacece ya ke tare, yana daf da zai kai hannun sai kuma ya tsaya cak yace" Oh! Yi haƙuri, na tuba Allah."

Sai kuma ya ɗora da" Kin san wani abu, alƙawari na ma kaina zan daina duk wani abu marar kyau, saboda ke."

Haɗe fuska tayi idonta har sun ɗan rarako tace" Saboda ni? Me yasa sai ni?"

Saida ya cire duk wasa ya mayar gefe cike da kamala sannan yace" Saboda ke kika tunasar da ni mahimmancin sallah, hakan yasa na fara bibiyar wa'azizzikan malamai, hakan kuma ba ƙaramin tasiri ya yi gareni ba, dan na ƙara jin tsoron ubangijina."

Wata nauyayyar ajiyar zuciya ta sauke ta kalleshi tace" A taƙaice dai tsoron haɗuwarka da Allah yasa za ka daina?"

Jinjina kai yayi yace" Ƙwarai."

Sanyayyan kallo ta masa mai ban sha'awa tace" Allah ya ɗoraka a hanya madaidaiciya, Allah ya baka ikon gyara duk wani kure da ka san kana yi a rayuwarka, Allah kuma ya baka lada a kan yaƙi da zakayi da tsohuwar ɗabi'arka wajen ƙirƙiro sabuwar ɗabi'a."

"Ameen, nagode matata." Ya faɗa yana kallonta da ƙauna kamar a ce an ɗaura musu aure ne.

Da mamaki ta sake kallonshi tace "Me yasa ka ke kirana da matarka? Bayan kuma ka san ba haka ba ne."

Ɗaga gira yayi yace "To ai ina sonki, kuma na faɗawa su Abba sun san da maganar, har ma ya min alƙawarin zai je ya ga Abbanki, kin ga kuwa kin zama matata."

Hankali tashe ta marairaice tace "Dan Allah Yaya Mu'az ka rufa min asiri, aure da soyayya, ni sam ban ma san su ba, dama-dama ma auren tunda ta hanyarshi aka haifeni, dan Allah kar ka ruguza min burina, sannan ka ga ina karatu kuma Abba ma ya ce ba yanzu zai aurar da mu ba sai mun cimma wata ƙwaƙwarrar matsaya a rayuwa."

Yana tuƙi yana kallonta da mamakin dama tana dogon surutu haka wanda bai shafi nasiha ko karatu ba? Sai kuma ya ɗauke kai ya taɓe baki yace" Matata kar ki damu, idan mukayi auren za ki ci gaba da karatunki, burinki kuma ki zayyane min shi yanzu, ni zan cika mi shi da yardar Allah."

Girgiza kai tayi tana kallonshi tace" Ni dai dan Allah ka dakatar da almarar nan da ka ke rerawa, sam bana son aure a yanzu saboda wasu dalilai na."

Ba alamar wasa ya kalleta yace" Faɗi biyu na ji."

Rumgume hannaye tayi tace" Ba na sonka, sannan ina da burika."

Da hannu ya mata alama ya ƙanƙance ido yace" Faɗa min buri ɗaya na ji."

Wani murmushi tayi mai kama da kuka amma ba tace komai ba, cikin kulawa ya kalleta sosai yace" Uhum! Ina jinki?"

Iska ta feso daga bakinta ta haɗe kukan da ya taho mata tace" Babban burina shine nima mahaifina ya yi alfahari da ni, ko sau ɗaya ne ina so ya furta min cewa *ina alfahari da ke*, zan so ya dafa kaina ya saka min albarka, sai dai ban sani ba ko zan cimma haka, dan na yi iya ƙoƙarina wajen koyawa kaina fahimtar karatu amma abun ya gagara, ban san me yake damun kaina ba, gashi yanzu za..."

Shiru tayi ta kalli Mu'az kamar a tsorace, dan gani take ta yi suɓul da baka sosai wajen faɗin abinda ke ranta ga wanda ba wata shaƙuwa ba ce tsakaninsu, goge hawayenta tayi ta ɗaure fuska a dole ita ba komai kawai, lura da haka yasa Mu'az bai ce mata komai ba saboda a karatunshi ya karanci l'homme et le monde (mutum da duniyarsa) yasa ya bata damar hucewa kafin ya ce mata komai.

Ba wanda ya sake magana har suka isa kasuwa shagon Alhaji Ibrahim, wanda Saleema ce ta san shi a nan suke siyan duk wank abu da ya shafi atamfa, leshi, shadda da sauransu, zaune take kan benci daga baki-bakin shagon, shi kuma ya na tsaye ya rumgume hannaye yana kallon duk wani motsinta, ita kam hankali na kan kayan da ake ta fito mata da su tana dubawa dan zaɓen wanda ya mata. Mu'az da ya kula da wani matashin da ke yawan kallon Saleema gyara tsayuwa ya yi yace "Ƙanena, sassauta mata kallon nan haka ka j, ka yi haƙuri ka bar min ita ta wa ce, ka ga ni ma ba kulani take ba bare kai."

Tunda ya fara maganar ta ɗaga kai tana kallonshi tana kallon matashin, sai da ya gama ta girgiza kai ta kalli yaron shagon da kunya ta kamshi yana ta sosa ƙeya tace" Yawwa wannan na ke so."

Nuna masa duk wanda ta zaɓa ta yi sannan ya jinjina kai yace" Bari na faɗawa Alhaji."

Shigewa ya yi ciki ita kuma ta kalli Mu'az tana sauke numfashi, shi ma kallonta yake da fara'a a fuskarshi yace" Ban san me yasa ba, amma dai haushi na ke ji idan wani na kallonki."

Fuskarta a haɗe tace" Ka daina wasar nan mana, na faɗa maka komai fa yanzun nan, sam ni da kai ba mu dace ba."

Sam babu alamar ya ji zafin maganarta ko makamancin haka, sai ma murmushi da ya sakar mata yace" A gaba za ki so ni, lokaci kawai ki ke buƙata na baki, kuma na baki daga nan har a ɗaura mana aure."

Ɗauke kai tayi ta kalli mai shagon dake fitowa yana mata murmushi suka gaisa, nuna masa kayan ta yi ya lissafa ya faɗa mata tare da mata ragi sosai saboda sanayya, godiya ta masa bayan ta biya kuɗin yaronshi ya ɗauki kayan ya na saka mata a mota. Ba su yi nisa ba aka fara kiraye-kirayen sallah magriba, faka motar ya yi gefe ya kalleta yace "Matata, za ki iya jirana na yi sallah?"

Buɗa baki ta yi za ta yi magana sai kuma ya langaɓe kai yace "Dan Allah madame, kar ki hanani, ke ce fa ki ka nuna min mahimmancin sallah kan lokacinta, shiyasa na ke ƙoƙarin kamantawa yanzu."

Sakin fuskarta tayi daga ɗaurewar da ta mata ta saki murmushi tace "To shikenan, a sakamu a addu'a."

Buɗa motar ya yi zai fita yana faɗin "Tunda na ganki na ke addu'ar samunki, kar ki damu matata, addu'ata ta ki ce."

Saida ya rufo mata ƙofar kawai ta saki wani sanyayyan murmushi tana girgiza kanta, gyara zamanta tayi sosai tana hangenshi bakin ƙofar masallacin yana alwala, irin yanda yake sauri saboda an kusa tayar da sallah, amma kuma a nutse yake kamar ba jikinshi ke kazar-kazar ɗin ba, ba ta gushe tana kallonshi ba har suka kabbara sallah.

---

Da sallama dattijuwar ta shigo ɗakin, a sanyaye ya amsa yana tashi zaune, cike da ladabi ya

karɓi kwanon hannunta yace "Mama da kan ki? Ina su Fareeda?"

Saida ta zauna tana fuskantarshi kafin tace "Suna can suna aikin da aka saba, ka san asabar ɗin nan uta ce ta farkon hutun makaranta da aka shiga, dan haka akwai bukukuwa da dama."

Jinjina kai ya yi yace "Hakane, amma Mama ai da ba ki kawo min da kanki ba."

Irin kallon nan na manya ta aika masa tace "Na kawo maka da kaina ne saboda a gabana na ke so ka ci ka bani kwanon."

Cike da kunya ya sosa ƙeya yace "Mama, Allah za..."

Dakatar da shi tayi da hannu tace "Ka ga Huzeifa, ka ci abincin nan yanzu ko ranka ya ɓace."

Sunkuyar da kanshi ƙasa ya yi tare da tallaɓe haɓarshi, bai san ta ya zai kwatanta ma mahaifiyarshi ba ya sha'awar cin komai ba? *Allah sarki, Allah jiƙan Babanmu*! Wannan zazzaƙar murya ita ke masa amsa-kuwa a kunnuwa, sahihiyar fuskarta mai cike da kamala da haiba, tsintar kanshi ya yi da murmushi shi kaɗai a zaune.

Mahaifiyarshi da ta ƙura masa idanuwa ta na jiran ya ci abincin ta ga shiru, a ƙarshe sai ganin ta yi ya ɓige da murmushi shi kaɗai, cike da kulawa tace "Huzeifa."

Zunbur ya kalleta dan ya manta a gabanta ya ke, da sauri ya kalleta ya ɗan rarraba idanu yace "Ah...ahhh, na'am Mama."

A tausashe tace "Me ya ke damunka?"

Girgiza kai yayi kanshi ƙasa yace "Ba komai Mama."

Ƙara gyara zama ta yi sosai tace "Huzeifa, kada wannan jarabawar ta sa ka illata kanka, ka daina cin abinci gabaɗaya, kullum karatu ba ka da lokacin hutu, ɗan lokacin da ba karatun ka ke ba kuma ɗinki ka ke yi, kana ganin hakan ya yi dai-dai? Ba ka tsoron ulcer ɗinka ta tashi?"

Kallonta ya yi a ladabce yace" Ki yi haƙuri Mama, in sha Allah zan kiyaye, ai komai ya zo ƙarshe tunda an gama."

Cike da tabbaci tace" An gama, amma jiran tsammanin sakamakon shi yake jefaka a halin tunanin nan, me zai hana ka bar wa Allah zaɓi, idan ka yi nasara ka gode masa, idan ba ka samu ba ka gode masa ka kuma duba wata hanyar ka bi."

Ajiyar zyciya ya sauke ya jinjina kai yace" Hakane Mama, in sha Allah zan yi yanda ki ka ce."

"Allah yasa." Ta faɗa tana kallon kwanon abincin tace "Maida hankali ka ci abincin."

"To Mama." Ya faɗa yana jawo kwanon dan ba ya son yin musu da ita, saida ta ga ya fara jefa abincin kaɗai ta bar ɗakin tana sake jadadda masa za ta zo ɗaukar kwanon da kanta, maza ya cin ye duka kafin ta dawo.

Ƙarar da wayarshi ta yi yasa ko amsa mata baiyi ba ya du a wayar, wani iska ya feso daga bakinshi ganin Sharhasila ce, ƙurawa lambar idanu yayi da tunanin ya ɗauka? Dan tun da ya fara zana jarabawar nan bai kirata ba saboda zafi da kanshi ya yi, yau ne ya gama yake tunanin zai je gidan dan su haɗu saboda ƙara ƙaratowar lokacin bikinsu, gashi kuma ta kira bai san dalili ba.

Ɗauka ya yi ya kara a kunne yana sallama, a taƙaice ta amsa wa "Alaika salam, Baby shine ka manta da ni ko kirana ba ka yi?"

Lumshe idanu yayi kamar ba zai amsa ba, sai kuma ya numfasa cikin nutsuwa yace "Ban manta da ke ba, zan zo gidan yau."

Cike da shagwaɓa da kuma sakarci tace "Ka ga ni zan zo, zan zo gidan na ku, ina son ganinka ne."

Waro idanu yayi a sauƙaƙe yace "Gidanmu kuma?"

Turo baki tayi ta amsa da "E, gidanku, na yi kewarka Baby."

Dafe gaban goshonshi yayi yace "Ba sai kin zo ba, ni zan zo anjima, kin ji?"

Cikin shagwaɓa tace "Ka yi alƙawari?"

"Na yi." Ya faɗa a tausashe, murmushi tayi wanda saida ya ji sautinsa a kunnuwa tace "To Baby ka taho mana da ice cream, ni zan ba ka wani abu idan ka zo."

Rufe idanu yayi yana mamakin wauta irin ta Sharhasila, "To." Kawai ya faɗa yana ɗauke wayar daga kunnenshi ya aje ya ci gaba da cin abincin.

*Ga mai son shiga grp ɗina ya tuntuɓi wanda ke musu post zai samu kanshi a ciki in sha Allah.*

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💏💏💏💏💏💏💏💏💏💏
*BAIWATA*

💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_16_

Fitowarta kenan daga wanka tana tsane jikinta da babban towel, su Hadeeya ta samu suna ta mitar aikin da sukayi na gyaran ɗakin Papi wanda har kayan abinci sai da Alhaji Auwal ya sa aka canza musu wuri aka maidasu madafa, Ummee haushi kamar zai kasheta da tana aikin, yanzu haka duk a gajiye suka kwanta har ƙarfe 11:00 ta yi.

Kayan baccinta ta saka ta zauna bakin gado tana addu'o'in da ta saba yi, ta shafe jikinta kenan za ta kwanta aka ƙwanƙwasa ɗakin, miƙewa tayi da niyyar buɗewa dan Hameeda tsaki ta ja tana faɗin "Daren ma ba za'a bari mu huta ba."

Ta kai hannu za ta ɗauki hijabinta aka turo ƙofar, ido huɗu sukayi da Mu'az da yayi turus yana kallonta daga ƙasa har sama, bakinshi buɗe ya kasa furta ko a, hankali ya lalubi idanunshi ya rufe dan in ba haka ba zai mutu a tsaye. Sa'a ɗaya ta yi saurin rarumo hijabi ta rufe jikinta ba

tare da ta sanya ba, sosai kunya ta kamata ta sadda kanta ƙasa, riga da wando ne jikinta na bacci, rigar ta na da hannaye iya damatsenta, saidai ta fito mata da surarta, haka ma wandon duk da bai kamata ba, amma tsayinshi iya bakin gwiwoyinta ne.

Hadeeya da ta miƙe zaune ce tace "Yaya, lafiya?"

Buɗa idanunshi ya yi ya kalleta sai kuma ya yi gyaran murya yace "Ughym! Umm..ammm...! Dama jarabawarku ne ta fito, na zo na ji lambobinku ne dan na duba muku."

Da sauri Hadeeya ta taso tana faɗin "Yawwa, Yaya ni lambata 4452..."

Saida ya saci kallon Saleema da ta wanka masa harara ta ja tsaki ta koma ta zauna kan gadon kafin ya turawa abokin na shi lambar da sunan Hadeeya ya duba masa, cikin ƙanƙanin lokaci aka faɗa masa Hadeeya da Ummee sun samu har ma da Hameeda da ita ta zana jarabawar ne kawai amma ba ta kai ga ajin ba (candidate libre), cikin ƙanƙanin lokaci ɗakin ya hargitse da ihu da shewa na ƴan matan, da gudu suka fita dan sanar da iyayen da har yanzu suke zaune a falo suna kallo suna hira.

A hankali ya tako ya zo gabanta cikin sanyin murya kamar mai tsoronta yace "Saleema, lambarki?"

A zafafe tace "Ba na buƙata malam, ka ga shigo mana ɗaki da ka yi ma ba tare da an baka izini ba ya isa, dan haka kar ka hassalani dayawa."

Kawar da kai tayi tana sake haɗe fuska sosai ita dole ya ɓata mata rai, durƙusawa ya yi niyyar yi dan ci gaba da bata haƙuri, haka kawai ya ke jin ranshi ba daɗi saboda ranta ya ɓace, da sauri ta jaye ƙafafunta dake kusa da shi tana ɗan galla masa harara, miƙewa yayi tsaye yace "Ki yi haƙuri Saleema, na shigo ne dan na ga baku jima da shigowa ɗakin ba bare a ce har kun kwanta, amma ai na ƙwanƙwasa ƙofa, kuma sai da na ɗan jinkirta kafin na shigo, tunanina hakan ya ba wa wacce ke farke damar kimtsa jikinta."

Sake marairaicewa ya yi yace" Saleema, ni fa ba kowace mace ke birgeni ba, ba kuma kowane tsiraici na ke son gani ba, tunda na ke a rayuwata ban taɓa jin ina son wata ƴa mace ba sai ke, ke ce mace ta farko da na ji ina so na yi rayuwar aure da ita, ke ce macen da na ji ina sha'awar ta zama uwar ƴaƴana, Saleema..."

Yanda ya kira sunanta yasa ta ɗaga kai ta kalleshi, ci gaba ya yi da cewa" Tabbas ƙarya na faɗa idan har na ce surarki ba ta birgeni, amma ki sani na yi tarayya da mata da suka fi ki kyau da wayewa, sai dai ba su min ba saboda sun rasa *aji*, a gareki ne na fahimci duk wata mace mai aji, to tana tare da *kamun kanta*, wallahi abu ɗaya ya sa na ke sonki da aure, wannan abun kuma shine *tarbiyya*, ina da yaƙinin tarayyata da ke za ta zama tsanin hawana hanya madaidaiciya, kamar yanda na ke da tabbacin zuri'ata indai ta tsatsonki za su fito, to za su zama abun alfaharin kowa, sannan na zama uba ma fi dacen ƴaƴa a duniya."

Da sauri ya durƙusa gabanta yayi tsugunno irin na maza yana kallon fuskarta kamar yadda ita ma take kallonshi da ƙyar take ƙyaftawa yace" Saleema, ki nemi zaɓin ubangijinki a kan lamarina, kar kiyi gaggawa dan ni ma ba zan yi ba, duk da kuwa ina matuƙar son yin aure saboda wani babban dalili, idan har kika ji kin gamsu za ki aureni, to ki sanar da ni a ko da yaushe, ni kuma na miki alƙawarin faɗa miki komai a game da ni, har da ma wanda iyayena kansu ba su sani ba, dan bana so mu fara zama na gaskiha ba tare da kin san wannan abun ba, dan gaskiya ba na jurar matsala daga abun da na ke so, musaman ma..."

Saida ya yi ƙasa da kanshi kafin yace" Musamman ma ke, wallahi zan iya miki kuka idan kina hushi dani."

Da sauri ya ɗago ya kalleta yace" Kin gane? Ni kwata-kwata ban saba da rayuwar wahala ba, ban taɓa jin abu ya birgeni lokaci ɗaya ba kamar yadda kika shiga raina, an reneni cikin gata da bani duk abin da na ke so, dan Allah Saleema kar ki hana min kanki a karon farko na rayuwata."

Buɗa ido tayi da kyau tana kallonshi, ɗan jan hijabinta tayi ta ƙara rufe ƙafafunta da take jin ta kamar a tsirara, ba tare da ta ɗauke dubanta gareshi ba tace" *Aku*, aku sarkin surutu."

Laƙace mata hanci yayi yana dariya yace" Ke ma da kin aureni za ki koyi surutu."

Da sauri ya miƙe tsaye yana sake faɗin" Yanzu bani lambar ta ki kema na sa a duba miki?"

Girgiza kai tayi tace" Gaskiya a'a, ina ji a jikina ma ban ci ba, ba sai ka wahalar da kanka ba."

Da mamaki yace" Me yasa? Ya za ki cire rai haka?"

Cike da jimami tace" Ka share kawai, nagode da kulawarka."

Ɗaga kafaɗa ya yi yace" Shikenan, bari na canza kaya sai na je na dubo miki."

Da mugun sauri ta miƙe tsaye har tana sakin hijabin ya zube ƙasa ta yi ram da rigarshi tana faɗin" A'a, a'a dan Allah kar k..."

Sai kuma ta saki rigarshi ta ja baya tana durƙusawa ta ɗauki hijabin kanta ƙasa cike da kunyar abun da ta aikata, ganin ta yi shiru babu ma alamar za ta ce ƙala sai kawai ya fita shima ya na ji a ranshi lallai lallai dole ya dinga nisantar yarinyar nan dan gudun samun matsala, dan in dai zai dinga ganinta a haka, sannan har wani dalili ya sa su haɗa jikinsu, to fa tabbas komai na iya faruwa a yadda yake tsananin son yin aure dan ya ci halalinsa.

Da farin ciki Hameeda ta shigo ɗakin tace "Abba ya ce ki zo."

Ba ta amsa mata ba ta miƙe bayan Hameeda ta fita a ɗakin, zane ta ɗaura a kan wandon

sannan ta saka hijab ɗin ta fito, falon ta samesu suna ta murna inda ta ji Ummeeta na faɗin "Gaskiya Abba ni dai ƙaton sa za'a yanka min, ƙawayena su ci nama su ƙoshi."

Tana ƙarasowa ya kalleta yace "Saleema ke ba ki faɗa mana sakamakonki ba?"

A sanyaye tace "Abba da safe zan je da kaina na dubo."

Da mamaki yace "A'a, me yasa to? Gashi a sauƙaƙe Yayanku na diba muku."

A ladabce tace "Abba na fi so na duba a can."

Kallon Amarya ya yi yace "Ai ina tunanin ƴan Bac ma gobe ake fito musu da sakamako?"

Saida ta yatsina fuska ta kalli Saleema tace "Haka ake saka rai."

Jinjina kai yayi yace "To shikenan, Allah kaimu goben sai ki je tunda haka kika fi so."

Juyawa tayi ta koma ɗaki ta kwanta gabaɗaya take ji a jikinta kawai ba ta samu ba, amma dai za ta je dan ta samu tabbacin haka.

*Washe gari*

Ta jima wajen Papi suna hira tana faɗa masa wani abu da ya zo kanta daren jiya kafin bacci ya ɗauketa, ganin ta samu goyon baya ɗari bisa ɗari sannan ta fito daga ɓangaren na shi ta nufo falon dan ɗaukar jakarta ta tafi makaranta dubo sunanta. Kai tsaye madafa ta nufa ta samu Nafissa da amarya suna aiki, ɗan kama musu tayi saboda Nafissa take so ta ma magana, tana ganin Amarya ta buɗa mangaza ta raɗawa Nafissa abu a kunne, kallonta tayi da mamaki tace "Kin tabbatar?"

Lumshe ido tayi alamar e tace "Ki yarda dani, ki ƙwarara kanki."

A tsorace ta furta "Gaskiya ina jin tsoro."

Girgiza mata kai tayi ta riƙe hannubta tace "Ki ji tsoron Allah kawai, yana tare da mu kuma zai taimakemu, saboda niyyarmu mai kyau ce."

Jin amarya na fitowa yasa Saleema raba hannunta da na Nafissa tace "Yawwa ni na tafi, sai na dawo."

Jinjina kai tayi tace "A dawo lafiya."

Da harara amarya ta bita tana ayyana "Allah raka taki gona, na san ma ba samu zakiyi ba tunda ba karatun ne a gabanki ba."

Amarya na idar da girki ta kira Ummee, tana zuwa ta bata abincin Papi ta ce "Ki kaiwa Baba ɗakinshi."

Wani yatsina fuska tayi tace "Papi kuma? Ba ga Nafissa nan ba."

Rai ɓace amarya tace "Ke in za ki karɓa ki karɓa, doka ce kuma ubanki ya ɗorata, in ba za ki kai ba na kira Mu'az ya kai sai na faɗa masa ke kin ƙi."

Da sauri ta finciko kwanon ta juya kamar za ta cira bakinta tana bubbuga ƙafafu ta nufi ɗakin cike da takaicin me ye sai ita za ta kai masa abinci, tana shiga ɗakin ba sallama dan ta nuna bata so ba fa, ajewa kawai ta yi ba ko ina kwana duk da yana zaune falon haka ta juyo ta fito, da kallo ya bita kawai ya girgiza kai a ranshi yace "Allah ya shiryaku."

Tare da dreba suka tafi makarantarsu, a kam ta samu ɗalibai da dama da suma suka zo duba na su sunan, ba ta ;ata lokaci ba wajen fara duba sunayen da suka fara da harafin H, shiru babu alamar na ta sunan, haka ta dinga dubawa daga farko har ƙarshe amma babu, jiki a sanyaye ta koma gefe ƙofar wani aji ta zauna ta tangale kanta da ginshiƙin wurin, sannu sannu ta ji idanunta sun fara kawo mata ruwa, kamar an daketa sai kawai ta fashe da kuka.

Cikin ƴan ajinsu ne wata ta dafa kafaɗarta tace "Saleema."

Ƙin ɗagowa tayi saboda ita kaɗai ta san me take ji, ganin haka yasa ta sake faɗin "Saleema, ki yi haƙuri idan ba ki samu ba, kinga ni ma ban samu ba kuma ban damu ba, saboda na san akwai gaba kuma haka Allah ya tsara, kinga dayawa ma basu samu ba amma kowa ya haƙura, wannan shekarar jarabawa ta zubar da ɗalibai dayawa, ki ƙwarara kanki in sha Allah wata shekara sai ki ga kin samu."

A hankali ta rage kukanta jin ba ita kaɗai ba ce akwai dayawa, share hawayenta tayi ta miƙe tsaye ta kalli budurwar tace" Nagode Chafa'atu, nagode sosai, Allah ya sa haka shi ya fi zama alkairi."

"Ameen." Ta faɗa tana murmushi, da sauri Saleema ta nufi hanyar fita ta samu dreba na jiranta ta shiga suka tafi, haka kawai ta ji zuciyarta ta bushe da tunanin hukuncin da mahaifinta zai mata, a ganinta idan ma duka ne ai ba yau ne farko ba, ya jima yana dukanta tun bata san ciwon jikinta ba, dan haka za ta ɗauka idan ma dukan ne, ai dai ba zai ɗauki ranta ba idan ba Allah ya nufi hakan ba, kyauta kuma ya ba wa su Hadeeya duk abin da ya mallaka bai dameta ba, in dai bai hukunta mahaifiyarta da laifinta ba to komai ya yi.

Cikin takon nutsuwa ta shigo falon, a hankali ta shiga bin kowa na ɗakin da kallo saboda yanda

ta ga sunyi zugum-zugum, babban abin da ya ɗaga hankalinta shine ganin mahaifinta a gefen Alhaji Auwal zaune fuskarshi yanda kasan hadarin gabas, sai dai kuma a gefe da ta ga Nafissa durƙushe tana kuka ƙashirban sai ta ɗan murmusa kamar hankalinta a kwance yake.

Duk da arnan kallon da mahaifinta ke aika mata bai hanata ƙarasawa kusa da shi ba ta zauna ƙasa irin zaman tahiya tace "Abba ina kwana."

Ɗauke kanshi yayi daga kanta da mamakin ita yarinyar nan ba ta gane ɓacin rai ne? Kusanshi fa ta zo bayan ta san zai iya tattakata, Alhaji Auwal ne ya dawo da shi daga tunanin da yake ta hanyar faɗin "Y'ata ya batun sakamakon?"

Kallonshi tayi sai kuma ta sunkuyar da kai a hankali ta girgiza kanta alamar ba magana, da sauri ya kalli Alhaji Yusuf da zai yi magana a zafafe ya masa alama da ido ya yi shiru, haɗewa ya yi yana jinjina kai kamar zai tashi sama, a tsanake ya kalleta yace "Y'ata, kar ki damu kanki kin ji, faɗa min ya kike so? Kina son samun kanki a aji na gaba ne? Ko kuma kina so nan da awa ɗaya ki ga sunanki a kafe a wata takardar?"

Kallonshi tayi tace "A'a Abba, nagode da karramawarka, amma na fi so na samu dalilin ƙoƙarina, idan akayi haka an zalunci dayawa wanda ba su da yanda zasuyi."

"Kuma har abada ba za ki samu ba indai da ƙoƙarinki ne." Cewar Alhaji Yusuf har da saka ƙafa ɗaya ya tureta daga kusanshi, sai da tayi kamar za ta yi sujada dan abun bazata ne, gyara zamanta tayi sanda Alhaji Auwal ke faɗin "Ka ga kar ka kuma dukar min yarinya, karatun ba na Allah ba ne? Ko dabararta za ta bata ne?"

Cije leɓen ƙasa Alhaji Yusuf ya yi kamar zai ciji iska, Alhaji Auwal kuma kallon Nafissa ya yi da ke ta sharar hawaye yace "Zan nemeki, ki bamu wuri yanzu."

Miƙewa ta yi ta nufi madafa, kallon Hajia Rabi da amarya yayi yace "Dan Allah ku bamu wuri za mu tattauna?"

A kasalance suka miƙe musamman amarya da ta bi Saleema da harara, har yaran ma duka ya korasu sannan ya kalli Alhaji Yusuf yace "Bari na nuna maka wani abu game da ƴarka."

Kallon Saleema ya yi a tsanake yace "Matso nan Baby."

Miƙewa tayi ta koma kusa da shi ta zauna ƙasa, a nutse ya kalleta yace "Saleema, wannan yarinyar Nafissa ta zo min da wata magana yanzu, amma ban yarda da ita ba saboda na san ɗana..."

Gyara zamanshi ya yi yace "Ta faɗa min wai Yayanta ne ya ke so ya kashe min ɗana Mu'awwaz saboda ya gano akwai wata mummunar alaƙa tsakaninshi da ita Nafissa, kuma ta tabbatar da zai aikata saboda Yayan na ta ɗan daba ne, shi ne ta tsorata take sanar dani wai na yi wani abu

a kai, da fari ma ƙin faɗa ta yi sai da na yi da gaske ta faɗa min dalili, to magana ta gaskiya na ɗan taɓa ganin abin da ya sani zargin Mu'awwaz, sai dai ba na jin zai iya neman ƴar aikin gidan nan, to yanzu ke ya kike gani? Na tura Mu'awwaz wata ƙasar ne? Ko kuma na sanar da hukuma su shiga tsakaninsu."

Da sauri Saleema da dama komai shirinta ne ta kalleshi tace" A'a Abba, kar ka yi ko ɗaya."

Da alamar tambaya ya tambayeta da" Me yasa?"

A nutse cike da hankali tace" Abba, ta min bayani akan Yayan nan na ta, ɗan shaye-shaye ne da babu abin da yake sai zaman banza, ba ya da tunanin kansa bare ya yi tunanin rayuwar wasu na shi, a ganina idan ka shigar da maganar wajen hukuma, to kamar mun daɓawa kanmu wuƙa ne, dan shakka babu za'a san abin da Mu'awwaz ya aikata, idan kuma ka fitar da Mu'awwaz ƙasar waje, to fa wannan ɗan daban zai iya fallasashi da tunanin ya gudu ne saboda tsoron kar ya ɗauki fansa, idan kuma har maganar ta fito fili, to hukumar kare haƙƙin mata da yara ƙanana za su iya saka ido a kan lamarin, idan haka ta faru kuma za'a ce a gudanar da bincike, a ƙarshe kotu za ta shiga lamarin da ƙorafin Mu'awwaz na ɗaya daga cikin ma su cin zarafin mata musamman marasa galihu."

A sanyaye sosai kamar za ta yi kuka tace" Abba, kuma ka san hukumar kare haƙƙin mata ba ta wasa da lamari irin wannan, za su ɓata lokaci da kuɗi har ma da iko wajen ganin sun kayar da mu wannan shari'ar, gwamnati ma ba ta ja da su Abba, dan su suna da goyon baya daga turawa ne."

Ta ƙarashe maganar da sigar dake nuna tana son tsoratar da shi, ai kam a tsorace Alhaji Auwal yace" Hakan na nufin mutumcin gidan nan zai zube kenan?"

Cikin raɗa kamar za ta yi dariya tace" Abba, ai har siyasarka ta shekaru ma lalacewa za ta yi, abokan hamayya sun samu abun tsokanarku da shi, gaskiya a duba wata hanyar."

Riƙe haɓa Alhaji Auwal ya yi ya kalli Alhaji Yusuf da ya kafe Saleema da idanu da mamakin ina duk ta san wannan abubuwan? Wa ya bata wannan hikimar? Cike da jimami yace" Ya ka ke gani Alhaji Yusuf?"

Ɗauke idanu yayi daga Saleema yana ɗan matse fuska yace" Gaskiya ne Alhaji, a duba wata hanyar daban."

Jinjina kai ya yi yace" To kenan ya kake gani?"

Kallon Saleema ya yi yace" Ke shiga ciki."

Jinjina kai tayi ta fara yunƙarawa a kasalance za ta bar wurin, inda shi kuma ya kalli Alhaji

Auwal yace" Ina ganin a kira yaron sai a bashi kuɗi ma su yawa da zai sa ya bar maganar kawai, kuma ma yarinyar ai ba fyaɗe ya mata ba, da son ranta haka ya faru tunda ba karan-kanta ta zo ta faɗa ba."

Da sauri Alhaji Auwal ya juya ga Saleema da ke tafiya a hankali tana jin me mahaifin na ta ke faɗa, ta na ganin idan ɗaya daga cikinsu haka ta faru, shin haka zai faɗa? Kiranta ya yi yace" Dawo zauna."

Dawowa ta yi ta zauna yana kallonta yace" Kin ji me mahaifinki ya faɗa, ke me kike tunani?"

Saida ta saci kallon mahaifinta dake ta hararenta tace" Abba, mu fara tabbatar da gaskiyar maganar ta hanyar tuntuɓar Mu'awwaz."

Jinjina kai yayi yace" Wannan ma magana ce, amma yanzu ke mu ƙaddara an tuntuɓeshi kuma gaskiya ne abin da aka faɗa, me ye mafitar?"

Ƴar dariya tayi ta girgiza kai tace" Abba, gaskiya a wautar kasancewata ƴar fari kuma mace mai rauni, idan a ra'ayina ne sai na ce mu aura masa ita, kunga kenan ko da daga baya maganar ta fito, to sai a ɗaukeshi kawai soyayya ce irin ta masu ƴanci, tunda dukansu sun haura shekara sha takwas, dan idan kuɗi mu ka bashi hakan zai iya sa wa ya dinga yaudararmu ta hanyar karɓan kuɗi lokaci lokaci (blackmail), kunga kenan babu hutu kuma ko yaushe dai asirin zai tonu, amma idan ta zama matarshi babu mai ɗaga maganar."

Bubbuga cinya Alhaji Auwal ya yi ya washe baki yana dariya yace" Wannan yayi, wannan shawara ta yi, hakan shi ne mafita."

Sai kuma ya kalli Alhaji Yusuf da mamaki ya sakashi zuba musu idanu kawai ya nuna mishi Saleema yace" Ka gani ko, abinda na ke so ka fahimta kenan, wannan ita ce *BAIWAR ƳARKA*."

Kallonta yayi yace" Tashi ki shiga ciki Baby, amma zan fara shawara da Baba na ji me yake gani game da hakan, dan yanzu bana komai sai da shawararshi."

Murmushi ta saki ta miƙe kawai dan ta san ta wajen Papi ma ba za'a samu matsala ba, dan ta gama da shi tun kafin ma ta kitsawa Nafissa abin da za ta yi.

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💏💏💏💏💏💏💏💏💏💏
*BAIWATA*
💏💏💏💏💏💏💏💏💏💏

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_17_

Tunda Papi ya fara magana bayan sun faɗa masa abin da ke faruwa Abban Saleema ke kallonshi kamar a tsorace, to sak shawarar da ƴar ƙaramar ƴarsa ta bayar shi ma yake maimaita duk da ba su faɗa masa sun tattauna da kowa ba, har sai da Alhaji Auwal ya taɓoshi yace "Ka gani ko, ya kamata ka saka ido akan yarinyar nan, tunda ta zo gidan nan abubuwa masu kyau ke faruwa, sannan rayuwata da ta iyalina ta fara hawa kan saiti, wallahi babbar *kadara* Allah ya baka, ka kula da ita yanda ya dace, idan Allah yasa ba ta cikin wanda za su ci moriyar boko, to ka tambayeta abin da za ta iya yi bayan wannan, za ka sha mamakin yarinyar nan idan na faɗa maka watarana ni da kai za ta iya yi mana alfarmar da duk ikonmu da iliminmu ba za su sama mana ita ba."

Maida dubanshi yayi ga Papi yace" Baba, tunda kai ma abin da ka gani kenan, ina ga anjima sai mu je gidansu yarinyar, ko ba komai ni a ganina ya kamata Mu'awwaz ya shiga hankalinshi, dan abin da yarinyar ta zo da shi ya tabbatar min da zargina a kan shi, Baba kamar Mu'awwaz na

kamashi da kororn roba  (comdom) a motarshi, amma da na yi magana ya dinga min kame-kame, yanzu kam na yarda da abin da ke faruwa a gidan nan, tunda shi ya lalata mata rayuwa, to shi ya kamata ya aureta ko ba ya so, idan ta auri wani a haka za ta iya fuskantar tsananin rayuwa da ƙiyayya, idan mun yi sa'a auren ya yi ƙarko to za ta rayu cikin tsangwama, amma idan shi ne da ya fara, bai da bakin aibatata dan shi ya fita lalacewa."

Kallon Alhaji Yusuf ya yi dake tunani kan abin da Alhaji Auwal ya faɗa masa, a ganinshi me ye ya kamata a ce kamar Saleema na so bayan karatu? Ai sai dai in soyayya take, ko kuma aure take so? A gaskiya ba ya jin zai iya taimaka mata da komai in dai ba abin da ya shafi karatu ba, to me ya fi ilimi a duniyar nan? Idan ba ka da ilimin nan na boko wani baƙauye ka ke zama, ƙaramin misali sau tari zai yi magana da yaran da harshen faransanci su mayar mi shi, amma ita ko ya yi niyyar yi mata sai ya dakata dan ya san ba za ta san me ya ce ba bare ya samu abin da yake so. Dafashi Alhaji Auwal ya yi yace "Muje ko?"

Ɗan zabura ya yi sannan ya miƙe yana kallon Papi yace "Baba sai an jima."

Da haka suka fita farfajiyar Alhaji Yusuf na faɗin "Yanzu sai yaushe za'a turo min yaran? Ina buƙatarsu a gidan nan wallahi, gaba ɗaya mun yi kewarsu."

Nauyayyar ajiyar zuciya Alhaji Auwal ya sauke yace "Ka yi ƙoƙari ka sama musu ƙannai mana, ka ga fa duk sun zama ƴan mata nan gaba kaɗan aurar da su za ka yi."

Murmushi ya yi yana shafa wuyanshi yace "Alhaji ai... Ina ga sun isa haka, dama namiji ne muke ta fatan Allah ya bamu, kuma na fi so ya fito daga wajen mahaifiyar Saleema, amma Allah bai nufa ba har yanzu."

Murmushi Alhaji Auwal ya yi yace "Da alama kai kanka ka fi yarda da tarbiyar da Safiya ta ke ba wa na ta yaran?"

Sadda kanshi yayi ƙasa bai ce komai ba, murmushi Alhaji Auwal ya sake yi yace "Shikenan ba komai, zan turosu da yamma, akwai tsarabar da nake son haɗa musu ne, sannan da dare zan zo gidan na ka akwai maganar da na ke so muyi da kai a kan ita Saleema da kuma Hameeda."

Da sauri ya kalleshi yace "Lafiya dai ko? Ba wani abu sukayi ba?"

Girgiza kai yayi yace "Ba abin da suka aikata, idan na zo za ka ji ko menene."

Jinjina kai yayi yace "Shikenan Alhaji, Allah kaimu."

Musabaha sukayi ya bar gidan da tunanin wace magana kuma zai zo mishi da ita a kan Hameeda da Saleema? Da haka ya isa gida ya shaida ma Safiya Saleema ba ta samu ba kamar dai yanda tun farko ya je makarantar ya dubo musu, saida ta yi ƙwalla na rashin jin daɗi da fatan Allah ya nuna mata ilimin da ke cikin hakan.

Idar da sallah azahar ɗinta kenan ta samu Hajia babba tace "Mama, dan Allah wayarku za ku ara min na kira Mamana."

Da fara'a ta nuna mata wayar da ke kan gado tace "Gata nan, idan kin ida kuma sai ki faɗawa su Hadeeya su shirya, Alhaji ya ce zaku fita tare siyayya."

"To Mama." Ta faɗa a ladabce tana ɗaukar wayar, fitowa tayi daga ɗakin tana ɗora wayar a kunne, jim kaɗan Mamanta ta ɗauka suka gaisa a tsanake, ɗorawa tayi da "Mama lambar Khairat za ki duba min a wayarki, ina so zan yi magana da ita."

Numfashi Safiya ta sauke har tana jin sautinshi kafin tace "Shikenan, amma me zai hana ki bari har ki dawo, tunda anjima za ku zo."

A shagwaɓe tace "Mama, magana ce ta gaggawa, kwana huɗu ya rage saukar makaranta, ina so na tambayeta wani abu ne."

"Shikenan." Ta faɗa tana cewa "Bari na duba na gani."

Har za ta kashe wayar Saleema ta yi saurin cewa "Mama."

Dakatawa tayi tace "Ina jinki."

Cikin ladabi tace "Abba bai miki faɗa ba a kan rashin samun jarabawata?"

Murmushi Safiya tayi tace "Bai yi ba Hajia, dake tun jiya ma kwance na ke ban da lafiya, amma yanzu da sauƙi."

Hankali tashe Saleema tace "Ayya! Mama baki da lafiya, ki yi haƙuri jiya ban kiraki ba, ya jikin na ki?"

A tausashe tace "Da sauƙi sosai Saleema, kuma har da rashinki a kusa dani, amma yau na ji ƙarfi sosai da aka ce za ku dawo."

Cike da tausayin mahaifiyar ta ta tace "Zan zo Mama, shiyasa nake ta miki addu'a Allah ya sa ki min ƙane, ko hakan zai sa ki sassauta soyayyarki a kaina."

Muryarta ɗauke da sautin jimami da rawar murya tace "To ya na iya Saleema, ke kaɗai Allah ya bani, dole na tattara duka soyayyata na ɗora a kan ki, idan so samuna ne Saleema mahaifinki ya miki aure tun yanzu, ta hakane zan saka ran ganin jikoki daga gareki."

Kunya ce ta kamata kamar tana gabanta, rufe fuska tayi da tafin hannunta ɗay tace "Kai Mama, dan Allah ki daina ni bana so."

Safiya ma murmushi tayi daga inda take tace "To shikenan na daina, amma idan kika zo zamuyi maganar dan ki tabbatar ina buƙatar hakan daga gareki."

Ɗan matse bakinta tayi tace "To Mama, karki manta lambar."

"To." Ta faɗa tana kashe wayar dan turo mata lambar, ƙarasawa tayi ga kujera ta zauna tana jiran shigowar saƙo, kamar an ce ɗaga kanki kalli ƙofa sai kal suka haɗa idanu ita da Mu'awwaz dake shigowa falon da sauri kuma da alamar ɓaci rai da tashin hankali. Kai tsaye ita ya nufo da mugun sauri, sai da ya zo gabanta ya tsaya, juyawa ya yi dama da hauni ya ga ba kowa sai ita kaɗai, maida dubnshi yayi gareta yace "Ke, me kika faɗawa Abbana?"

Wani kallo da take jifanshi da shi ƙasa da sama kamar ta ga abun ƙyama, ƙarshe ma ɗauke kai tayi ta taɓe baki tace "Me ya ce masa na faɗa mi shi?"

Sunkuyowa ya yi kamar zai yi ruku'u yace "Na tabbata akwai abin da kika faɗa masa, yanzu yake tambayata wai me ye tsakanina da Nafissa."

Kallonshi tayi ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya tace "In tambayeka mana? Me yasa ka min ƙarya a waccen ranar?"

Rarraba idanu yayi yace "Ƙarya kuma? Yaushe na miki ƙarya?"

Nunashi tayi da yatsa tace "Ranar ka faɗa min shi ne farko, ashe wata uku kenan ka na anfanar ƴar mutane kamar wata matarka, yanzu ka ƙaddara kai ne mijinta ka sameta a haka, ya za ka ji?"

Taɓe baki yayi ya yatsina fuska cike da shaƙiyanci yace "Sam, ki ma daina kwatanta ƙazamar can da zamowa matata, kuma abin da ya faru ai biyanta na ke, ba dole na mata ba."

Cike da takaici Saleema ta miƙe tsaye tana riƙe wayar hannunta da kyau wacce ta ji shigowar saƙo tana kallonshi tace "Ka sani alƙawarin Allah ba ya tashi, wallahi kai ba ka isa ka lalata rayuwar ƴan mata ba son ranka, sannan idan ka tashi aure kace kamila nutsatsiya ka ke buƙata, dole ka girbi abin da ka shuka, ɓarnar da ka fara kuma kai ne za ka ƙarasata."

Sama da ƙasa ta dalla masa harara ta juya za ta bar wurin, cak ta tsaya saboda idanu da suka haɗa da Mu'az na tsaye a bayansu, ganinshi tsaye ya sa Mu'awwaz shiga taitayinshi ya fara sadda kai ƙasa yana kame-kame da sosa ƙeya.

Haɗe fuska ta sake yi ta ɗaga ƙafa da niyyar wucewa ta barsu, sai kuma Mu'az da fuskarshi ta nuna alamar tashin hankali ya fara takowa da sauri yana nufota, irin yanda yake tahowa gabaɗaya sai take ganin kar dai ya rumgumeta, baya ta fara ja a hankali amma ya na ci gaba da nufota, ba tare da sani ba ta kai wa Mu'awwaz karo a bayanta da sauri ta juya ta kalleshi, sai

kuma ta juyo a hassale inda Mu'az yake cike da ɓacin rai tace "Mu'az wai me ye haka? Ka na I..."

Nuna mata Mu'awwaz ya yi fuskarshi ɗauke da fushi yace "Me ye tsakaninki da wannan yaron?"

Da mamakin tambayarshi ta wara idanunta kaɗan a saman fuskarshi tace "Kamar ya me ye tsakaninmu? Me ka gan..."

Tsawar da ya daka mata ta hanyar nunata da yatsa yace "Ke!!!" Ya sa ta ruf da bakinta ta rintse ido, sai kuma ya shaƙo wuyan rigar Mu'awwaz ya fincikoshi gabanshi yana kallonshi yace "Me ye tsakaninka da matata?"

Turnuƙe fuska Mu'awwaz ya yi yana son ƙwatar kansa yace "Ni ba komai tsakanina da ita, magana kawai muke."

"A kan me kuke maganar?" Ya faɗa a tsawace, Saleema da ta koma gefe tana kallonsu ce tace "Amma ai bai shafeka ba."

Gam-gam! Ya sake matse wuyan rigar Mu'awwaz bayan ya kalleta sannan ya kalleshi yace "Me ka ke faɗa mata?"

Cikin jin haushi Mu'awwaz yace "Wai me ye haka? Na faɗa maka ba komai, me zan mata ne a tunaninka?"

Cikin ɓacin rai yace "Saboda na san halinka, na san duk iskancin da ka ke a garin nan, zuba maka idanu na yi kayi saboda rayuwarka, amma ka ga wannan?"

Ya nuna masa Saleema dake gefe sannan ya ci gaba da cewa "Matata ce, wannan ta fi ƙarfin ka mata iskanci Mu'awwaz, wallahi idan ka kwatanta yin haka sai na fizge abin da ka ke taƙama da shi a jikinka wajen faɗawa ƴaƴan mutane."

Hankaɗashi ya yi da ƙarfi har saida ya faɗa kan kujera, har zai juya sai kuma ya sake juyowa da ƙarfi ya sake fincikoshi ya miƙar da shi tsaye, taɓe masa baki ya yi ya ɗan matsa fuskarshi sosai kusanshi ya shinshina bakinshi har zuwa wuyanshi, Mu'awwaz na ganin ya fara shinshinarshi ya fara sissine kai a tsorace, da maɗaukakin mamaki Mu'az ya kalleshi sosai yace "Mu'awwaz sigari ka fara sha?"

Da sauri ya girgiza kai yace "A'a wallahi."

Sakin wuyan rigarshi ya yi tare da fara cajeshi yana laluba duka aljijunanshi daga na gefe-gefe har na baya, ai kam sai ga kwalin sigari da maƙyasta, cirosu ya yi ya shiga ƙare masa kallo yace "Mu'awwaz bayan neman matan yanzu kula shaye-shaye za ka fara? Wai me ka ke neman maida rayuwarka ne? Ka kuwa san illar haka?"

Saleema dake gefe tana kallonsu kiran da Mamanta ta mata dan ta tambayeta ko ta ga lambar ne ya sa ta juyawa da niyyar barinsu nan su ci kansu idan suna so. Mu'az da dama ya ke son kora mata kashedi a kan tayi nesa da ƙanin na shi a zafafe ya gusa daga wajen Mu'awwaz tare gabanta yana kai hannu kamar zai riƙe hijabinta, kallon da ta aika mishi yasa shi dakatawa ya sunkuyar da kai yana ɗaga hannu alamar saranda yace "Shikenan na gane, kinga ni na miki alƙawarin zan kiyaye tabaki har sai bayan aure."

Sai kuma ya kalli fuskarta yana sauke numfashi kamar wanda ya yi gudu ya nunamata inda Mu'awwaz yake da idanu yace "Kinga wannan?"

Wayam! Ba Mu'awwaz har ya bar wurin, ba tare da ta ɗauke kanta ba ta ci gaba da kallonshi da mamakin shasheƙar da yake, ɗorawa ya yi da "Saleema dan Allah ki kiyaye shi, wallahi bai da mutumci ko kaɗan, kinga idan kina tsayawa tare da shi komai zai iya faruwa, Saleema ni na san Mu'awwaz wallahi har ta ƙarfi zai iya yi miki abin da bana so."

Wani kallo ta jefeshi da shi tace "Me ye baka so ɗin?"

Sadda kanshi yayi kamar mai jin kunyarta yace "Zai iya yi miki iskanci."

"Hummm!" Ta faɗa tana raɓashi tace "Nagode da kulawa."

Da kallo ya bita har ta ɗan yi nisa sai kuma ta juyo tace "Wataƙila a gunka ya koya."

Da wani tattausan gudu ya tare gabanta da mamakin maganarta, iska ya feso ya na tunanin wace irin jarabawa ce Ubangiji ke masa haka? Shin dan ya kasance mai taɓa jikin macen da ba ta halatta gareshi? Shi ne Allah ya jarabceshi da wannan ƙwaya ɗayan tak? Shi bai ma taɓa sanin ana son mutum lokaci ɗaya haka ba sai yau, a kwana uku da sukayi gidansu kawai haukacewa yake neman yi, ba kuma shine farkon da ya fara saninta ba, a'a ya santa jimawa dai ake ba'a haɗu ba, wannan ikon Allah ya fi gaban wasa kam, gashi sai ta mishi wauta da katoɓara, amla sai ya ji ya haɗe ranshi bai ɓace ba ko ɗaya. Yanzun ma dai bai ji haushi ba, sai ma ƙanƙance idanu da yayi cike da son ta yarda da shi yace "Wallahi Saleela ni ban taɓa sanin wata ƴa mace ba, shiyasa na faɗa miki ki nemi zaɓin Allah a kaina, idan kika ji gamsuwa a kan hakan ki faɗa min, na miki alƙawarin sanar da ke komai da ya shafeni, kuma wallahi gaskiya kawai zan faɗa miki, amma ki yarda dani Saleema ban taɓa zina ba, ke ce mace ta farko da na ke so na fara sani a rayuwata bayan aurenmu."

Wani irin faɗuwar ne ya ziyarceta sakamakon abin da ya faɗa, hakan yasa ta gyara tsayuwa ta ƙanƙance idanunta tace" Mu'az, yanzu idan aka ce ba na da wannan abun da ka ke tunanin samu a tare da ni, anya kuwa za ki iya zama da ni a haka?"

Tsurawa fuskarta idanu yayi yana kallo, saida ya mayar da wasa gefe cike da bata tabbaci yace" Ban san ta ya ne zan kwatanta miki yanda na ke ji ba, amma nan..."

Ya faɗa yana ɗora hannunshi na dama akan daidai zuciyarshi sannan ya ce" Gabaɗaya na ke jinta ta ki ce, duk wata bugawarta ɗaya da sunanki take amsawa, ƙwaƙwalwata a yanzu ba ta tunanin komai sai ke kawai, a yanda na ke ji Saleema zan iya rayuwa da ke ko babu wannan abun da kike tunanin shi ne kaɗai na ke so, ban taɓa sha'awar macen da ban ga jikinta ba, amma ke jinin jikina a sanyaye yake tafiya idan na ganki, ina da sauri a kan komai, amma akan lamarinki sanya nake tamkar gajiyayyan matafiyi, Saleema, a duk duniyar nan ke kaɗai ke da alhakin gajiyar da ni."

Ita ba *dutse* ba ce, hakan yasa a karo farko maganganun Mu'az sukayi matuƙar tasiri a zuciyarta, dan hatta da tsigar jikinta saida ta dinga tashi, saƙon ya ratsata matuƙa, babban abun tunaninta shine, dama a haka da mahaifinta ke kusheta akwai wani namiji da zai so ta a haka? Yanzu duk kalaman nan nata ne ita kaɗai? Son da yake mata har ya kai haka dama? Yadda ta ke kallonshi ne ya sa shi ƙyasta yatsunshi biyu yace "Matata ya dai?"

Da sauri ta zabura tana kallonshi, sai kuma ta kalli wayar dake hannunta ta nuna masa tace "Zan...ina zuwa, zan amsa waya."

Da sauri-sauri ta raɓa ta wuceshi shi kuma ya bita da kallo, saida ya ga shigewarta ɗakinsu kaɗai ya juya ya fita shi ma fatanshi ɗaya Allah ya ɗorashi a kan yarinyar nan dake wofantar da shi, irin yanda mata ke mararinsa suna kawo kawunansu gareshi, da yadda idan ya na wasa da mace take baje basirarta dan son ganin ya isa babbar fada, babu irin salon munafurci da kisisinar da ba'a masa ba dan ya faɗa tarko, amma ya dage ya nuna a'a fa, har saida ya taɓa samun kanshi yana daf da afkawa amma ya ce a jira sai ya nemo kororon roba saboda tsaro, daga ranar bai kuma haɗuwa da yarinyar ba dan a ganinshi wani abun ta ke da da yasa ya kusa wuce gona da iri ranar.

*Duk* abin da ke faruwa a idanun Hadeeya wacce ke sama fitowarta daga ɗakin amarya kenan ta hangesu, laɓewa ta yi tana kallonsu, irin yanda Saleema ke mishi magana kamar da gadara da isa, shi kuma yana ta wani sussunkuyar da kai, hakan sai ya sata tunanin to me ye a tsakaninsu? Ba ta iya samun amsa ba dan ba ta jin me suke faɗa, saida ta ga kowa ya bar wurin sannan ta sauko ita ma da tunanin me ye wai? Soyyaya suke? Ko kuma dai wani abun ne na daban?.

Lambar Khairat ta kira, bayan sun gaisa ta faɗa mata ita ce, ɗorawa tayi da cewa "Yawwa Khairat, ai nan da kwana huɗu ne saukar makaranta ko?"

Daga ɓangaren Khairat ta amsa da "E, muna ta shirye shirye ma."

A nutse tace "Yawwa, Khairat dan Allah ki min wata alfarma, ki samu malam ki faɗa masa na amince yanzu a saka sunana a jerin masu saukar."

Da mamaki Khairat tace "Amma me yasa? Na ga da fari ke kika ce ba kya so saboda Abbanki,

yanzu kuma kin ce a saka, Abban ya amince ne?"

A tausashe tace "Ko ɗaya Khairat, yanzu ma zan yi ne ba tare da saninshi ba, sai dai ban damu da ko me zai faru ba, ban ci jarabawar ba bai kamata na bari wannan damar ma ta wuce ni ba."

Khairat ce ta amsa da "Gaskiya kuma hakane, to amma ta ya zakiyi sauka bai sani ba?"

Kamar za ta fashe da kuka tace "Khairat ke dai ki faɗawa malam, in dai har ya amince za'ayi dani, to zan samu kuɗi a hannun Mama ko da na iya wainar da za'ayi sadaka ne."

"To shikenan." Cewar Khairat tana ci gaba da faɗin "Bari na faɗa masa dama yanzu ya shigo gida zai ci abinci."

"Yawwa nagode, yanda kukayi ki kirani da wannan lambar, amma anjima da yamma za mu koma gida."

Da haka suka rabu ita da Khairat, bai fi minti 15 ba ta sake kiranta da lambar malam ɗin dan ita wayarta ba kuɗi ta sanar mata ai ya amince kuma ya yi farin ciki sosai, wannan magana ita ta saka Saleeema farin ciki marar misaltuwa tana jin ko ba komai dai za ta kafa tarihi a zuri'arsu cewa ita ce ta farko da za ta sauke Alƙur'ani kuma a haddace.

Dreban da ke ta jiransu Alhaji Auwal ya kalla ya musu nuni da shi yace "Ku je yarana, Allah muku albarka."

Sai kuma ya kalli Saleema yace "Amma dai za ki dinga kawo mana ziyara ko?"

Ɗaga kai tayi alamar e, da yatsa ya nunata yace "Da gaske?"

Da murmushi ta amsa da "Allah ko Abba."

Jinjina kai yayi yace "Shikenan to na yarda."

Juyawa Saleema tayi ga Hajia Rabi tace "Mama sai anjima."

Shafa kuncinta tayi tana fara'a tace "Allah ya miki albarka ƴata, ki gaishe da Mamanki."

Jinjina kai tayi alamar to, Papi dake gefe Saleema ta ƙarasa gareshi, riƙo hannayenshi tayi duka biyun tana kallon fuskarshi tace "Papi nagode sosai da goyon bayan da ka bani, mu zamu tafi, sai wani lokaci kuma."

Jaye hannunshi ɗaya yayi ya ɗora a kanta yace "Allah ya miki albarka, Allah ya baki miji na gari, Allah ya saka farin ciki a rayuwarki, Allah ya baki zuri'a ta gari wacce za ta zama sanyin

idaniyarki."

Ɗora hannunta tayi kan na shi tana murmushi tace "Ameen Papi, nagode sosai, kai ma Allah ya ƙara maka lafiya da nisan kwana."

Ummeeta dake tsaye kusan Hameeda da kallon ƙyama take binsu har saida suka shiga mota suna ta ɗaga musu hannu suka bar gidan, duk da Saleema na jin za ta yi kewar mutanen, amma dai ta fi farin ciki da komawarta gidansu dan shine kwanciyar hankalinta.

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: 💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑
*BAIWATA*
💑💑💑💑💑💑💑💑💑💑

*NA*

_SAMIRA HAROUNA_

*SADAUKARWA GA*

*AHALINA*

*GAMAYYAR MARUBUTAN NIJAR (ASSO.)* 🤜🤛
_(Burinmu d'aga muryoyinmu sama domin anfanar da al'umma had'e da ciyar da adabin hausa.)_
☆ *[G. M. N. A]* ☆ 📖🖊️

_Bismillahir rahamanir rahim_

_18_

Tunda suka shigo gidan sai suka ga kamar sun yi watanni ba sa nan, cike da kewar iyayensu duk suka zube falo, daga iyayen har su kansu yaran sun girgiza ganin irin tarin tsarabar da aka saka musu bayan mota wacce sai yanzu da dreba ya yi ta shigowa da su suka gani, wani kwali na daban dreba ya miƙawa Saleema yace "Wannan Alhaji ne ya ce na baki."

Karɓa tayi tace "Ka min godiya sosai."

Duk tarin kayan dake gabansu wanda komai aka saka daidai da na kowa, hatta da takalmi dake wurin kowa da lambar da ƙafarshi ke ɗauka, dan Saleema talatin da takwas take anfani da shi, Hadeeya kuma arba'in daidai ƙaramar lamba, sai Hameeda talatin da tara, amma Hadeeya da ta ƙwallafa rai tana son sanin me je cikin kwalin, saida ta matso kusan Saleema tace "Mu ga miye a ciki?"

Ba tare da tunanin komai ba Saleema ta miƙa mata wanda saida Safiya ta kalli Saleema da mamaki, dan ita ta san abin da ba'a ba kowa ba ne aka ba ƴarta. Hadeeya na buɗewa jikinsu har rawa yake ita da Hameeda wajen ciro kayan ciki, wata mahaukaciyar lafiyayyar abaya kalar pink Hameeda ta buɗe tare da yin tsaye tana gwada rigar a jikinta, Hadeeya kuma wasu takalmi dake ciki kalar rigar ta ɗauka tana gwada a ƙafarta wanda takalmin da ganinsu ta san masu tsada ne kuma sabin kalar da ba kowa ya sansu ba.

Hameeda dake tsaye da rigar a hannu ce ta hango kwalin da ya saka gabanta faɗuwa, da sauri ta saki rigar ta durƙusa ta ɗauki kwalin tana buɗewa, Hadeeya ma da ta gani zaro idanu tayi ta furta "IPhone 14 pro max."

Ardiya ma zaburowa tayi tana ƙwalalo ido dan jin wai da gaske suke ko dai wasa? Uban wa zai ba Saleema wayar da ta haura million ɗaya? Ta na ganin camera ɗin wayar ya tabbatar mata da gaskiya, Hadeeya riƙe wayar ta yi gam tana ta dubawa tana jin ina ma ta zama ta ta, take ta kalli Saleema tace "Bari na tura miki abubuwa, ba komai a ciki."

Saleema ko a jikinta, yo ita me zata yi da waya? Miƙewa ma kawai ta yi ta barsu nan ta shige ɗakin Mamanta dan yin wanka, Hadeeya da Hameeda ai sai suka shiga ture-ture da ɗaukar hoto suna turawa a wayoyinsu suna nuna fa da IPhone 14 aka ɗauki hoton, wayar da har yanzu su dai duk yanda suke tare da ƴaƴan masu kuɗi kuma maƙaryata ba su ga wanda ya yi jarumtar riƙeta ba bare su da har yanzu Abbansu ne ke siya musu idan suka birgeshi.

*Suna* zaune kan sallaya Saleema ta kalli Mamanta tace "Mama, kwana huɗu ya rage saukar makaranta, kuma na roƙi malam ya saka sunana, yanzu kuɗi nake so a wajenki da zan ɗinka sabon hijabi irin na sauran ɗalibai, sai ka inda hali ki min waina da za'a yi sadaka."

Ajiyar zuciya Safiya ta sauke tace "Me yasa kikayi haka? Kina so mahaifinki ya wulaƙancemu

ne?"

Turo baki tayi da alamar shagwaɓa tace "Dan Allah fa Mama, kinga wannan ce kaɗai damar da nake da da Abba zaiyi alfahari dani, baki ga ba ɗazu gidansu Yaya Mu'az yanda yake hararata."

Buɗa ido Safiya tayi tace "To, Yaya Mu'az kuma? Yaushe ya zama Yayan na ki?"

Cike da kunya ta sunkuyar da kanta amma ba tace komai, jin shiru yasa Safiya nisawa tace "Shikenan, amma yanzu dai kinga bana da kuɗi gaskiya, kuma ko da za'ayi saukar nan sai dai mu ja baki muyi shiru kar kowa ya ji, dan bana son fitina a halin da na ke cikin nan."

Marairaicewa Saleema tayi tace "To amma Mama ina zan samu kuɗin?"

A tsanake ta kalleta tace "Karki damu, bari Abban na ki ya shigo, zan san yanda zan yi na samo miki."

Fara'a tayi tace "Nagode Mama."

Miƙewa tayi ta buɗa wata ƙaramar drower ta ɗauki chocolate a cikin tsarabar da aka basu ne, da kallo Safiya ta bita har ta fita a ɗakin, murmushi ta saki tana fatan Allah ya kareta a duk inda take, har yanzu wayar nan tana hannunsu Hadeeya, amma ita ba ta damu ba, sannan tsarabar ma na sauran kayan Ardiya ce ta raba ta aiko Hamdeeya ta kawo wai na Saleema, kayan ba su taka kara sun karya ba, ta san za suyi tunanin ai ita an bata wannan babbar kyauta, amma abun mamaki Saleema karɓa ta yi sam alamu ma ya nuna hankalinta ba nan yake ba bare ta yi ƙorafin wannan ɗan abun za'a bata? Tabbas halin ko in kula na abin da ya shafi ci ko na duniya mai ƙarewa halinta ne, sai dai ƴar ta ta tafi ta halin ko in kula akan abun, dan ita tana gane an cuceta sai dai kawai ta yi shiru, amma ita Saleema sai dai ka ga alamar bata san abun a kai ba bare ya dameta, gale da kyautar da mahaifinsu ke ba ƴan uwan ita ya hanata kaɗai take ɗan damuwa, shi ma da an kwana biyu ta shiga sabgar gabanta.

Suna zaune kan teburin cin abincin ya fito cikin farar jallabiya, zaunawa yayi inda ya saba zama kullum, Saleema dake kusa da shi ta sadda kanta saboda kallon da ya mata, miƙewa Safiya tayi a kasalance ta fara zuba masa abincin, shi kuma hakalinshi na ga Saleema yace "Na faɗa miki idan har ba ki samu jarabawar nan ba dama zan ɗauki mataki na ƙarshe a kanki."

A hankali ta ɗaga idanunta ta kalleshi a ladabce tace "Ka yi haƙuri Abba, a gaba zan yi in s..."

Tsawa ya daka mata da cewa "Ke! Ni sa'an wasanki ne?"

Da sauri ta sadda kanta ƙasa saboda alamar da Safiya ta mata da idonta, cike da masifa yace "To bari ki ji Saleema, idan ma aure kike so ki fito da miji na aurar da ke, amma ki sani na daina asarar kuɗina a kanki, wallahi na daina zuba miki ƙwandala da sunan karatu, dan haka ba ke ba sake fita a gidan nan da sunan za ki tafi makaranta, *na dakatar da ita daga yau*."

Duk zuba mishi idanu sukayi har Safiya dake tsaye, sai kuma ta girgiza kai tana lumshe idanunta, Saleema ma idanunta cike da hawaye ta kalleshi sai kuma ta kalli mahaifiyarta da tunda ta zo ta fahimci kamar har yanzu jikinta ba ta jin daɗinshi, abin da take son faɗa masa tsoro kuma ya hanata dan kar ya bigeta, sai kwatsam mahaifiyarta ta yi tambayar cewa "Amma Alhaji ka hanata zuwa islamiyya shekara takwas da suka wuce, ka hanata ɗinki tun tana ƙarama, yanzu kuma ka dakatar da bokon ma, toe za ta yi idan ta zauna a gidan?"

Kallonta yayi a zafafe yace "Wannan hukuncina ne kuma na gama yankewa, ta zauna a gidan ta dinga kama muku aiki har ta fito min da wanda ta ke so nan da wata biyu na aurar da ita."

Da sauri Saleema ta furta "Aure Abba, amm..."

Kallon da ya mata ya sa ta yi shiru, ƙwafa yayi tare da faɗin "Idan la ba ki da saurayin ni zan miki, kuma ma ai ba zaki rasa ba tunda har kika ƙi maida hankali ga karatu, na san soyayya ce ke hanaki."

Ardiya da take jin daɗin haka cike da kissa tace "Ai shekarunta sun isa na aure, ba ka ga duk wata wahalar da take sha kafin ganin al'adarta ba?"

Kunya ce ta sa Saleema duƙar da kanta, inda Hadeeya da Hameeda suka yi dariya a tare, Safiya kuma kallon Ardiya tayi tace "Me yasa kike min hakane? Dan ba ƴarki ba ce?"

Taɓe baki Ardiya tayi tace "Kowa dai na gidan nan ya san gaskiya na faɗa, na tabbata soyayya ke hana Saleema karatu har sha'awarta ke ƙara tunzura, idan ba'a aurar da ita yanzu ba wata rana abun kunya za ta ɗauko..."

Cokalin da take zuba miyar da shi dake hannunta ta buga a kan teburin da ƙarfi tana rintse ido tace" Ya isheki haka."

Duk kallon Safiya sukayi da tayi kwaratsin, nuna Ardiya tayi da cokalin za ta yi magana, da sauri Alhaji Yusuf ya miƙe tare da jawo Safiya jikinshi ya ɗan rumgumata, ba ya so ta ɗaga murya sosai, ba ya so ta yi faɗa da Ardiya, ba ya so ta ɗaga hankalinta kamar yadda likita ya faɗa masa a kiyaye duk wani tashin hankali da ɓaci ranta saboda cikin dake jikin na wata uku. Yunƙurawa ta yi za ta tashi tana sake faɗin "Wallah..."

Hannu ya kai kan bakinta ya toshe cikin raɗa yace "Ya isa haka Sofeena, rabu da ita kinji uwargidana."

A hankali ta dinga sauke numfashi tana ƙara tusa kanta a ƙirjinshi, shafa bayanta ya dinga yi yana kallon fuskar Ardiya dake kumbura tana musu wani mugun kallo. Saleema kunya ce ta sake kamata a ranta ta ayyana" Tofa! Mun dawo kenan, wai Abbanmu ba ya girma ne shi?"

Ɗago kai Safiya tayi ta kalleshi idanunta taf da hawaye tace" Dama ina son magana da kai."

Cike da kulawa da guje duk abin da zai ɓata mata rai ya tallabo haɓarta yace" Ina jinki, ko sai mun shiga ciki?"

Turo baki tayi cike da shagwaɓa ta ɗan saci kallon Ardiya da har yanzu ke kallonsu tana mamakin mijin na su, mamakinta bai wuce yadda in suna tare yake nuna ba wata sai ita ba, ko aikace wasu lokuta ya na nuna mata ta fi Safiya mahimmanci, amma duba yanzu yanda yake ta naniƙeta a gabansu wai dan tana da ciki, hmmmm! Ta faɗa tana ayyana "A haifeshi mu gani."

Safiya da ta fahimci haka cikin shagwaɓa tace "Dama kuɗi na ke so, kuma ka ga watan da ya wuce ba ka bani komai ba."

Ajiyar zuciya ya sauke jin matsalar ta ta ba wata babba bace, dama dan bata aiki ya ɗauki alƙawarin bata jaka saba'in kowane wata, duba da Ardiya tana aiki kuma tana ɗaukar albashi, dan kar abun ya mata yawa ya shi ɗaukar wannan matakin, duk da wasu lokuta idan ya bata ma sai ta ce ba ta buƙata ko kuma ta ɗauki rabi, wani lokaci kuma shi yake mantawa kamar dai yanda ya yi watan da ya wuce.

Cikin sassauta murya yace "Shikenan, zan ganki anjima, yanzu je ki huta ɗakinki ina zuwa, bana son hayaniyarki."

Jinjina kai tayi alamar to tare da nufa hanyar ɗakin na ta, da kallo duk suka bita har Hadeeya ta taɓe baki, dan ita ba ta taɓa ganin haka ba sai yau, Saleema kuma zaman ne ta ji zai isheta tunda babu mai tsaya mata a wurin, miƙewa tayi za ta bi bayanta ba kunya ba komai Alhaji Yusuf yace "Kar ki sake ki takura min mata da matsalolinki, ciki ne da ita kuma bana son abin da zai ɗaga mata hankali."

Rufe idanu Saleema tayi sai kuma ta girgiza kai tace "Ba wajenta zan je ba, falo zan zauna."

Tana wucewa Hadeeya ta kalleshi cike da wauta da gaɓanci tace "Abba, ka ga ni dai irin wayar da na ke so ka siya min, ta ya ma Saleema za ta riƙe wannan wayar ni ina fama da wannan Samsung."

Ko kallonta bai yi ba yace "Um um! Ban da arziƙin da zan siya miki wayar nan."

Turo baki tayi ta kalli Ardiya tace "Momma..."

Da yatsabta nunata tace "Kar ma ki fara, ubanki bai iya sai ni ce zan iya?"

Ɗan kallon Ardiya ya yi sai kuma ya girgiza kai ya ci gaba da cin abincinshi, Ardiya dake kallonshi tana ta hassala ne tace "Shi ne ma ba zaka kulani ba."

Ɗagowa yayi yace "Me ya faru?"

Cike da masifa da harshenta na hausa da baya fita da kyau tace "Shi ne zaka wulaƙantani a gabanta? Ka yi ta wani rumgumeta dan na gane ita ma mowa ce a wurinka."

Ajiyar zuciya ya sauke yace "Ki yi haƙuri to, ba dan ranki ya ɓace na yi ba, na faɗa miki yanda likita yace game da lafiyarta, dole mu kiyaye ɓata mata sannan mu lallaɓata."

Jinjina kai tayi tace "Shikenan to ya yi, sai ka yi ta lallaɓatan ai."

Miƙewa tayi a hassale ta nufi ɗakinta, da sauri ya tashi ya bi bayanta dan ba zai so ita ma ta yi hushi ba, dan wallahi alƙawari ya la kanshi cewa ba zai kuma kusantar Safiya ba sai ya ga cikinta ya girma, dan yanzu gani yake motsi kaɗan zai sa ta yi ɓari.

*09:00* Safiya ta sameta ɗakinta har ta yi shirin bacci tana zaune kan gado tana karatu, da fara'a ta ƙaraso ta zauna kusanta ta miƙo mata kuɗi, da sauri ta amsa tana murna ita ma, ƙidaya kuɗin tayi ta kalleta tace "Mama duka wannan ne suka bayar?"

Da murmushi ta jinjina mata kai alamar e, ita ma jinjina kan tayi ta faɗa jikinta tace "Nagode Mamana, gaskiya Abbanmu yana sonki."

Murmushi kawai ta sake yi amma ba ta musa mata ba, dan gaskiya ne ya na sonta kuma yana yawan faɗa mata haka, sannan a aikace ma yana nuna mata, duk irin yanda take da sani kan ya auro Ardiya ne saboda iliminta da wayewa, sannan ya na sonta da kuma ƴaƴanta kyawawa, amma tana da tabbacin soyayya ta gaskiya yake mata, dan kuwa ba ta nemi komai ta rasa a wajenshi ba, duk abin da zai ma Ardiya shi zai mata, idan zai kashe ma Ardiya million ɗaya to ita ma haka, matsalar Saleema ce ma kawai ta sa wasu lokuta yake faɗa mata magana mai ɗaci ko a gaban yaran, wanda hakan take ɗaukarsa a matsayin saɓani na ma'aurata. Amma ko daren jiya da suka je asibiti aka faɗa masa tana da ciki, kai tsaye wajen cin abinci suka wuce ya kashe mata kuɗi sosai a kan abinci kafin su zo gida, jimawar da sukayi yasa Ardiya rufeshi da masifa har saida ya faɗa mata dalilin kaɗai.

Ɗagata tayi daga jikinta ta kalli fuskarta tace "Kin san me? Baƙi mukayi a gidanmu."

Da mamaki tace "Baƙi kuma? Su wa ye?"

Irin kallon tuhuma da tsokana ta mata tace "Alhaji Auwal ne da mahaifinshi, sai kuma... Yaya Mu'az ɗinki."

Ta ƙarashe tana mata dariya, waro idanu tayi tace "Mu'az kuma?"

Da sauri ta nemi saukowa daga kan gadon tace "Mama mama, na roƙeki Mama kar ki bari Abba ya biyewa haukan Mu'az, shi fa sam ba ya da hanakali."

Dariya ta ƙyalƙyale da ita tace "Zamu gani dai waye mahaukacin, yanzu tashi ki je Abbanki na nemanki."

Kyaɓe fuska tayi kamar za ta yi kuka tace "Maaamaaa."

Ita ma kyaɓe fuska tayi tace "Na'aaaam.." Ɗaure fuska tayi tace "Tashi ki je."

Jiki a sanyaye ta miƙe ta ɗauki hijabinta iya gwiwa ta saka sannan ta fice cike da fatan ba abin da take tunani ba ne zai faru. Dan in kuwa hakane to tabbas Mu'az bai da sanya a lamura kuma ya mata shigar sauri, amma fa hakan ba ya na nufin za ta amsa buƙatarshi ba ne, duk da kuwa bayan dawowarsu ta yi tunaninshi sau ɗaya, dan sosai kalaman nan na shi a haɗuwarsu ta ƙarshe suka tsaya mata a zuciya da ma ƙwaƙwalwarta.

Tashin muryar Alhaji Auwal yasa ta nutsuwa sosai ta sadda kanta sosai duk da faɗuwar da gabanta ke yi ta ƙwanƙwasa ƙofar tare da sallama a sanyaye sosai, ba tare da ya amsa ba Alhaji Yusuf ya bata umarni da "Shigo."

Tura ƙofar tayi a hankali ta shiga takawa a nutse ba tare da ta ɗaga ta kalli kowa ba, ita dai kawai ta ji idanun mutane a jikinta suna yawo, sannan daga ƙamshin turaren one million ta gane kusurwar da Mu'az yake zaune dan shi ke anfani da turaren, daga kallon ƙafafu ta gane inda mahaifinta yake, a kusa da shi ta zauna a ladabce tana faɗin "Ina wuninku."

"Lafiya lau Saleema." Alhaji Auwal da Papi suka faɗa a tare sai Alhaji Auwal da ya ɗora da "Baby kin ga har na fara kewarku tun yanzu, ina ma za ki koma gidana da zama?"

Sai kuma ya yi dariya yace "Ko da yake abinda ya kawomu kenan, amsarki ita za ta bayyana mana shin za ki rayu da mu ko akasin haka, dan babu wanda ya isa ya miki dole in dai ina raye."

Wani kallo Mu'az ya watsa mishi ta ƙasan idanu da tunanin "Za ko kaga abin da zan yi, a cikin gidan nan zan ɗirka mata ciki in ya so kwa shafa mana fatiha bayan raɗawa ɗanmu suna."

Maida dubanshi ya yi ga surukin na shi dake kallon Saleema yana faɗin "Mu'az ne dama ya ce yana sonki, kuma ya ce kin san da maganar, yanzu haka sun zo neman aurenki, kin amince a bashi aurenki?"

Alhaji Auwal ne ya katseshi da cewa "Ba ta amince a ba da aurenta ba, ta amince ta na sonshi?"

Ɗaure fuska Alhaji Yusuf yayi dan shi wannan sa'a ta Saleema a ganinshi ba sai an tuntuɓeta ba, dan kawai Papi da Alhaji Auwal ɗin sun matsa ne, wanda ya tasa dalilin da ya sa suke wani ririta yarinyar, alamu ma nuna masa yake Alhaji Auwal zai iya yin komai dan Saleemar, kamar

dai wacce ta aikata masa wani babban abu da ba wanda ya taɓa kwatanta yi masa. Maida dubanshi yaui ga Saleema yace "Muna jinki, kin amince?"

Daga cikin hijabi ta zuro hannunta ta share gumin da ya jiƙa mata goshi har zuwa dogon hancinta, rawa jikinta ya kwasa da tunanin mafita, duk ƙoƙarinta na satar kallon Mu'az ta kasa ganin fuskarshi saboda tsayinshi sannan ya shige cikin kujerar da yake zaune sosai, tana so ko ya ne su haɗa idanu ta aika masa kallon "Ya za ka min haka? Haka kwatsam?"

Saidai rashin nasarar ganin fuskarshi yasa ta ɗauki sama da minti ɗaya ba ta amsa ba har ma ta manta a ina take saboda tashin hankalin da take ciki, ba ta san me ye so ɗin ba kanshi, ba ta san wane irin zama za ta yi da shi ba, hasalima ba ta jin komai a game da shi, sannan abubuwan da ya dinga mata farkon haduwarsu ya saka mata shakku a kanshi, idan fa bai da ɗabi'ar ƙwarai? Za ta rayu da baƙin ciki kenan har abada?

A kausashe Alhaji Yusuf yace "Malama ke fa muke jira, ya zaki wani yi mana shiru kamar yaranki."

A gigice ta ɗago kanta, hakan ya ba hawayen da suka taru a idanunta damar zirarowa suka sauko kan kutatunta, a kiɗile ta girgiza kai sai kuma ta kalli inda Mu'az yake, suna haɗa idanu ya jefo mata kallon" Ki min rai Saleema."

Inda ita ma ta bishi da kallon" Ba zan iya ba Mu'az." Alhaji Auwal ne yace "Ƴata."

Kallonshi tayi saidai suna haɗa idanu ta fashe da kuka, cikin kulawa ya taso daga inda yake ya zo kusanta ya tsuguna, cikin tausasawa yace" Baby, kina ji na? Idan ba ki shirya ba ki faɗa mana, kamar yadda na faɗa miki da farko babu wanda zai miki dole, faɗi ina jinki?"

Sadda kanta tayi ƙasa cikin muryar kuka tace"...

*Alhamdulillah.*
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>
24/05/2022 à 14:11 - Mom Lateef: <Médias omis>